
# Jagoran Malamai

## Lissafi

Aji2




Partnership for Learning for All in Nigeria

plane

UKaid
from the British people

# Jagoran Malamai Lissafi

Aji2

## Rights and Permission

These materials were created under the Partnership for Learning for All in Nigeria (PLANE) project, funded by UK aid. These materials were adapted from materials developed under three previous UK aid funded programmes in Nigeria - the Education Sector Support Programme in Nigeria (ESSPIN), the Teacher Development Programme (TDP) as well as the Reading and Numeracy Activity (RANA) as part of the Girls' Education Project Phase 3 (GEP3) – and materials from the USAID Addressing Education in Northern Nigeria (AENN) activity. Content from these sources were streamlined into a single materials package and revised to align with the Nigerian National Curriculum and endorsed by the Kano, Kaduna and Jigawa State Governments. These materials are licensed under the Creative Commons Attribution 4.0 International license.

## Mallaka da Samarwa

An wallafa waɗannan kayan aiki ne a ƙarƙashin shirin haɗaka don samar da ilmi ga kowa da kowa, wato 'PLANE' da tallafi daga hukumar bayar da tallafi ta ƙasar Ingila, wato (UK aid). An samar da waɗannan kayan aiki ne ta hanyar 'yan sauye-sauye daga kayan aiki uku da hukumar bayar da tallafi ta ƙasar Ingila (UK aid) ta tallafa wajen aiwatar da su a Nijeriya a baya wato, tallafi ga bangaren ilimi a Nijeriya (ESSPIN) da shirin inganta malami a Nijeriya (TDP) da kuma shirin inganta karatu da lissafi (RANA) wanda aka gudanar ƙarƙashin shirin inganta ilimin 'ya'ya mata na 3 (GEP 3), sai kuma kayan aiki na shirin bunƙasa ilimi a arewacin Najeriya (AENN) wanda hukumar bayar da tallafi ta ƙasar Amurka ta yi wato, USAID. An dai tattara bayanan da aka samo daga kayayyakin aiki dabam daban da aka ambata a sama zuwa cikin wannan kundin guda ɗaya na kayan aiki wanda masana a fagen ilmi suka tabbatar da dacewarsa da tsarin manhajar koyon karatu da karantarwa ta Nijeriya sannan kuma da amincewar Gwamnatocin Jihohin Kano da Kaduna da Jigawa. Kayan aikin na da lasisi ne a ƙarƙashin tsarin bai ɗaya na mallaka mai lamba 4.0 na ƙasa da ƙasa.

# Wadanda Suka Bayar da Gudunmuwa

# (List of Contributors)

| Suna - Name | Wurin Aiki - Organisation |
|---|---|
| **Federal Partners** | |
| Nafi'u Adamu | Federal Ministry of Education, Abuja |
| Dr. Aminu Saidu | Nigerian Educational Research & Development Council |
| Abdurrazak Shehu | Universal Basic Education Board, Abuja |
| Bala M. Tatama | National Commission for Mass Literacy, Adult & Non-Formal Education |
| Auwalu Hamza | Partnership to Engage Reform and Learn (PERL), Kano |
| **Kaduna** | |
| Dr. Yahuza Salmanu | Federal College of Education, Zaria |
| Najmuddeen Alhassan | Federal College of Education, Zaria |
| Mercy B. Kude | Ministry of Education, Kaduna |
| Tanko S M Aliyu | State Universal Basic Education Board, Kaduna |
| Abubakar Umar | State Universal Basic Education Board, Kaduna |
| Pikawi Iliya Dauda | Kaduna State College of Education, Gidan Waya |
| Hauwa Maidala | Kaduna State Quality Assurance Authority |
| Garba Mohammed | LGEA Primary School, Unguwar Dankande, Igabi LGA, Kaduna |
| **Kano** | |
| Dr. Miswaru Bello | Sa'adatu Rimi College of Education, Kano |
| Zuwaira Yahaya | Sa'adatu Rimi College of Education, Kano |
| Muhammad Bello Gaya | State Universal Basic Education Board, Kano |
| Mohammed Yahaya | Kano Educationa Resource Department |
| Salisu Idris | Ministry of Education, Kano |
| Amina Umar | State Universal Basic Education Board, Kano |
| Munzali Mustapha | State Universal Basic Education Board, Kano |
| Dr. Kabir Hamisu Kura | Community Development Initiative, Kano |
| Wasila S. Jauro | Hotoro South, Special Primary School, Kano |
| Umar Shariff Ibrahim | State Universal Basic Education Board, Kano |
| Ibrahim L. Abdul | Aminu Kano College of Islamic and Legal Studies, Kano |
| Nuruddeen Dahiru | State Universal Basic Education Board, Kano |
| Dr. Atika Bala | Aminu Kano College of Islamic and Legal Studies |
| Dr. Auwalu Halilu | Civil Society Coalition on Education for All (CSAFECA), Kano |
| Baffa Sale | State Universal Basic Education Board, Kano |
| Tijjani Haladu B | School Based Management Committee, Kano |
| **Jigawa** | |
| Hamisu Iliya | State Universal Basic Education Board, Jigawa |
| Abdu Ahmed Ciroma | State Universal Basic Education Board, Jigawa |
| Dr. Sani Abdullahi | College of Education, Gumel |
| Dr. Binta U. Umar | College of Education, Gumel |
| Murtala Bala Sule | Roni Primary School, Roni |
| Habu Musa Lawal | Ministry of Education, Jigawa |
| Babangida Haruna | State Universal Basic Education Board, Jigawa |
| Arma Mohammad | Nasaro Primary School, Gumel |
| **Consultants** | |
| Dahiru Yalwa | Consultant Translator, College of Education, Azare |
| Dr. Naziru Ibrahim Abbas | Consultant Translator, Usmanu Danfodio University, Sokoto |
| Adamu Ago Saleh | Consultant Translator, Amadu Bello University, Zaria |

| | |
|---|---|
| Godwin Ondoma | Consultant Graphic Designer |
| Aliyu Sani Rafindadi | Consultant Graphic Designer |
| John Norj Akanbi | Consultant Illustrator |
| Lisa Walker | Curriculum Writer |
| Bethany Davidson-Widby | Curriculum Writer |
| **PLANE Staff** | |
| Dr. Grace Bila | Inclusion Advisor, PLANE |
| Hadiza Umar | Gender Equality and Social Inclusion Specialist, PLANE |
| Lawan Ali Bukar | Technical Officer, Materials Development, PLANE Kaduna |
| Nura Garba Bakori | Technical Officer, Teacher Professional Development, PLANE Kaduna |
| Abubakar Umar | Technical Officer, Materials Development, PLANE Kano |
| Shu'aibu Mohammed Dabo | Technical Officer, Teacher Professional Development, PLANE Kano |
| Phoebe Mshelia | Technical Officer, Materials Development, PLANE Jigawa |
| Sulaiman Muhammad Bakori | Technical Officer, Teacher Professional Development, PLANE Jigawa. |
| Gabriel Yakubu | Maths Officer, PLANE Abuja |
| Zahra Abubakar Maishanu | Literacy Officer, PLANE Abuja |
| Innocent Chukwu | Monitoring and Evaluation Specialist, PLANE Abuja |
| Zainab Isah Arah | State Technical Advisor, Kano |
| Awal Mohammed | State Technical Advisor, Jigawa |
| Salim Sadiq | State Technical Advisor, Kaduna |
| Mustapha B Ahmad | State Team Lead, PLANE Jigawa |
| Lawan Umar | State Team Lead, PLANE Kano |
| Diana Agabi | State Team Lead, PLANE Kaduna |
| Caitlin Downs | HQ Technical Officer, Education |
| Edward Ishaku | Education Coordinator/ Interim Output 1 lead, PLANE |
| Emily Koester | HQ Technical Advisor, PLANE |

## Gabatarwa

An samar da wannan Jagoran Malamin ne tare da tallafin Shirin haɗaka domin bunƙasa ilmi ga kowa da kowa (PLANE), da Ofishin kula da bayar da tallafi da ci gaba na ƙasar Birtaniya (FCDO). Jihohin da a yanzu za a bai wa fifiko su ne jihohin Kano da kaduna da kuma jihar Jigawa. Har wa yau, wannan Jagorar Malamin ya samu sanya albarkar masu faɗa- a-ji a harkar ilmi tun daga matakin Gwamnatin Tarayya da na jihohi. Hukumomi kamar Majalisar gudanar da bincke da ci gaban ilmi NERDC da Hukumar lura da shirin bayar da ilmi na bai ɗaya ta ƙasa UBEC da Ma'aikatun kula da ilimi na jihohi da kuma hukumomin bayar da ilmi na bai ɗaya da ke jihohin Kano da Kaduna da Jigawa duk sun sanya wa Jogarar albarka.

### Yadda za a yi amfani da Jagoran Malamai

Wannan Jagoran Malamin na ɗauke ne da tsarin gabatar da darussan lissafi a kowacce rana. Bugu da ƙari, tsarin karantar da darasin lissafi da ke cikin Jagoran ya yi daidai da tsarin manhajar karantarwa da Majalisar gudanar da bincke da ci gaban ilmi ta ƙasa wato, NERDC ta amince da shi. Tsarin gabatar da darussan karatu kamar dai yadda yake ƙunshe a cikin Jagoran, yana ɗauke da tsarin darussan ne na tsawon makwanni talatin da shida (36). Haka kuma, an rarraba waɗannan darussan ne zuwa zango uku na shekarar karatu. Kowanne mako na ɗauke da adadin yawan darussa biyar. Darussan da za a gabatar a mako na shida da mako na goma sha biyu na kowanne zangon karatu sun ƙunshi waiwaye ne a kan darussan da aka gabatar a baya da kuma auna fahimtar ɗalibai.

Shi dai tsarin gudanar da darasin yana ɗauke ne da sassauƙar hanyar koyarwa da ta ƙunshi Fara darasi da yin waƙa da Koyo da Bayyanawa da Aikin Gida. Wannan tsarin yana sauƙaƙa koyo da koyarwa sannan ya samar da yanayin maimaici mai sauƙi ga dalibai.

- **Fara darasi:** Fara darasi da motsa jiki ko rera waƙa wata dabara ce ko salo na janyo hankalin ɗalibai kafin a fara aiwatar da darasin wannan rana. Irin wannan dabara ko salo kan ƙunshi rera waƙa ko wasan kacici-kaci da kuma duba aikin gidan da aka bai wa ɗalibai su yi a gida.
- **Koyo:** Ita dai wannan dabara tana taimaka wa ɗalibai ne wajan fahimtar wasu sababbin dabarun koyon karatu. Wannan tsarin koyon, malami ne ke jan linzamin gabatar da sabuwar dabarar koyon.
- **Gwaji:** Wannan salo na nuna ƙwarewa da fahimtar ɗalibai kan abin da aka koyar. Kuma yakan ba ɗaliban dama ta musamman domin su kwakwayi aiwatar da wannan sabuwar hanyar koyo kamar dai yadda malamin nasu ya/ta kwatanta musu. Salon gwajin yakan ƙunshi ɗalibai ne ke tafiyar da komai a yayin da Malami zai/za ta sanya ido ya/tana ganin abin da kowa ke yi.
- **Bayyanawa:** Wannan salon na bai wa ɗalibai damar bayyana abin da suka koya daga darasin da malami ya koyar. Hakan, zai ba Malaman zarafin gane ko ɗaliban sun fahimci darasin da aka yi ko a'a**.**
- **Aikin Gida:** Wani salo ne da Malami kan bai wa ɗalibai aiki su yi a gida. Yana da matuƙar muhimmanci Malamai su riƙa ƙarfafa wa ɗalibansu gwiwa da su riƙa yin aikin gidan da aka ba su saboda ci gaban ilmin yara yakan ta'allaƙa ne ga irin ƙarin nazari da koyo da ɗaliban kan yi bayan a tashi daga makaranta.

Muna fata wannan Jagora zai taimaka wa Malamai su riƙa gabatar da darussa nagartattu da zai ba yara damar bayar da gudumawarsu a lokacin koyar da darussa. Har wa yau, ana buƙatar Malamai su yi amfani da hikima da basirarsu don ƙara sauƙaƙa wa ɗalibai fahimtar abin da suke koyar da su.

## Muhimman Ɓangarorin Lissafi

| Ɓangare | Ma'ana | Misalai |
|---|---|---|
| Fahimtar Lambobi | Fahimta da nuna ƙwarewa wajen iya tantancewa da kuma iya amfani lambobi daban daban. | • Karanta sunayen lambobi da kuma rubuta su.<br>• Kirga lambobin zuwa gaba da baya<br>• A san muhimmanci da kimar kowace lamba |
| Matakan yin lissafi. | Nuna ƙwarewa wajen iya bin matakan lissafi daban daban. | • Tarawa<br>• Ɗebewa<br>• Rabawa<br>• Sau/Ninkawa |
| Ilmin sanin zubi da tsarin da'irori/siffofi | Nuna fahimta da ƙwarewa wajen iya tantance zubi da tsarin da'irori/siffofi daban daban | • Nuna fahimta da iya tantance da'irori<br>• Iya zana da'irori<br>• Iya kwatantawa da banbance da'irori<br>• Iya auna tsawo ko faɗin da'irori/siffofi |
| Ilmin iya sanin awo ko yawan adadin wani abu | Nuna fahimta da ƙwarewa wajen iya sanin girma ko yawan adadin wani abu | • Kuɗi<br>• Lokaci<br>• Tsayi<br>• Faɗi<br>• Girma/Nagarta<br>• Karɓowa da tantance yawan alƙaluman da za a iya amincewa da su. |
| Tantance zubi da tsarin lambobi daban daban. | Ilmin iya fahimta da tantance zubi da tsarin da kuma dangantakar da ke tsakanin lambobi daban dabam. | • Kirƙira da maimaita matakan lambobi da zana da'irori/siffofi<br>• Kintatatar lambar da za ta biyo bayan wadda ake magana a kai.<br>• Cike giɓin lambobin da ba a sanya ba. |

### Nagartacciyar Hanyar Karantar da darasin Lissafi

- **Hanyoyi ko dabarun daban daban na gabatar lissafi:** Yana da matuƙar muhimmanci ɗalibai su san hanyoyi ko dabarun koyon lissafi daban daban domin su samu ƙarin gogewa a ɓangaren na lissafi. Alal-misali, ɗalibai kan iya wakiltar lamba ko fasalin lissafi ta hanyar hotuna da taswira da wani abu a zahiri ko kuma labari.
    - **Wadatataccen lokacin yin gwaji**: Yin nazari ko bita a- kai-a-kai na taimaka wa ɗalibai wajen ƙara ƙwarewa a fannoni daban daban na koyon lissafi. Yana da kyau ɗalibai su fuskanci iya warware wasu matsalolin tarawa ko ɗebewa ko rabawa da makamantansu a lokacin da suke makaranta ko idan sun dawo gida.

  **Alaƙanta lissafi da rayuwar ɗalibai:** Yana da matuƙar muhimmanci malamai su nuna wa ɗalibansu yadda za su riƙa yin amfani da salo daban daban wajen koyon darasin lissafi har ya zama jiki a gare su. Kaɗan daga cikin ire-iren waɗannan salo sun haɗa da koyon sanin adadin kaya da za a saya ko kudi da za a kai wa wani a kasuwa ko kuma ɗalibi ya iya sanin yawan adadin takawar da ya/ta yi daga gida zuwa makarantarsu.

## Dokoki na bai-ɗaya don shigar da dukkan dalibai a cikin darasi

1. A riƙa kiran ɗalibai da sunayensu a yayin da za su amsa tambaya ko domin su gwada yin wasan kwaikwayo na wani labari.

2. A lokacin da ake gabatar da wasan kwaikwayon labarin a gaban aji, a tabbatar kowane rukunin ɗalibai sun sami dama domin su ma su gwada (kamar maza da mata da ɗalibai masu buƙata ta musamman).

3. A duk lokacin da ɗalibai ke aiki a cikin ƙananan rukunoni a aji, a riƙa sauya ɗaliban da suke jagorancinsu lokaci zuwa lokaci (wani lokaci namiji, wani lokaci mace, wani lokacin daga cikin ɗalibai masu buƙata ta musamman).
    - A tabbatar da cewa ana bai wa ɗalibai masu buƙata ta musamman damar aikin rarrabawa ɗalibai littafai ko abubuwan ƙidaya da sauran kayan aikin da ake buƙata wajen gudanar da darasi.

4. A lokacin da ake zazzagayawa a cikin aji domin tallafawa ɗalibai da auna fahimtarsu, a tabbata ana sauya ɗaliban da ake tambaya a kowace rana domin a bai wa kowa dama ya faɗi amsarsa.

5. Idan ɗalibai suna shan walaha wajen fahimtar darasi, yi amfani da wasu dabarun koyarwar da za su sauƙaƙa fahimta, a kuma riƙa yabawa ɗalibai akai- akai.

## Kai ɗauki ga buƙatun Ɗalibai

1. ***Idan ɗalibai suna da matsalar gani (ido). Sai…***
    - A sauya masu wurin zama zuwa gaban aji.
    - A haɗa su da wani/wata ɗalibi/ɗaliba a matsayin aboki/ƙawa a cikin ƙaramin rukuninsu, wanda za su riƙa tallafa masu wajen fahimtar aikin da aka bayar kafin su fara aiwatar da aikinsu na su kaɗai.
    - A kama hannayen ɗalibai masu matsalar gani domin tallafa masu. Misali a nuna masu yadda za su yi amfani da yatsun hannu wajen ƙidaya, a darasin lissafi.
    - A tabbatar ɗalibai suna amfani da layin lambobi da kuma jadawalin lambobi na ɗaya zuwa ɗari da ke cikin littafin ɗalibai domin ya taimaka masu wajen fahimtar abin da aka rubuta a allo.

2. ***Idan dalibai suna fama da matsalar saurare (ji) a lokacin aka ke magana da su, sai..***
    - A tabbata ana kallon ɗalibai a lokacin da ake rera waƙoƙi, kuma a daina ba su baya.
    - Umurci ɗalibai su kalli bakinka/ki a lokacin da ka/kike furta kalmomin da ke cikin waƙar.
    - A nuna hoton da ke jikin waƙar domin taimaka wa ɗalibai su fahimci abin da waƙar ta ƙunsa.

3. ***Idan ɗalibai suna bukatar ƙarin taimako da zai sa su kewaya a cikin ajin don nemo abubuwan ƙidaya ko kuma zuwa wajen aji. Sai….***
    - A taƙaita neman kayan aikin a muhallin da ɗalibai suke.
        - Ɗalibai za su iya jagorantar rera waƙa a lokacin da aikin ke gudana daga kowane ɓangare na ajin. Ɗaliban da ke jagorantar waƙar za su tsaya a rukuninsu yayin da sauran ɗaliban ajin za su juya fuskokinsu gare su.
        - A riƙa zagayawa a cikin aji a lokacin da ake koyarwa. Duk da cewa Allo yana gḁban aji, ba tilas bane kowane gwaji da malami zai yi sai ya kasance a gaban allo ba. Misali a

darasin ƙidaya za a iya zuwa kowane ɓangare na aji, a nemi wani rukunin ɗalibai da su tashi domin ƙirga adadinsu.

- A wakilta wasu daga cikin ɗalibai su zama masu bayar da tallafi a kowane rukunin ɗalibai.
    - Ɗalibai masu tallafawa za su taimaka wa sauran ɗalibai wajen tattara littafansu ko su jagoranci sauran ɗaliban zuwa wani ɓangare na aji domin gudanar da wani aiki da aka ba su. A ƙarfafa aikin haɗaka tsakanin ɗalibai da ba su damar gudanarwar a tsakaninsu.
- A ba wa ɗalibai ayyuka na musamman a rukuninsu da zai ba kowannesu damar shiga a ciki, ba tare da buƙatar sai an fita wajen aji ba.
    - A lokacin da ake tattara guntayen itatuwa domin samar da ɗaurin goma-goma. Za a iya ba wa ɗaliban aikin ƙidaya kowane ɗauri su tabbaatar da itatuwan sun cika daidai, su ɗaure, su kuma yabawa sauran ɗaliban da aka ba wa aikin tsintar itatuwan.
    - Maimakon a umurci dukkan ɗalibai su fita waje domin nemo surorin abubuwa kamar da'ira ko akwati, za a iya ba su damar gudanar da wasan '**Na gani**' a cikin aji. Ɗalibai su duba duk wani abu da suke iya samowa a cikin aji, masu siffofi daban-daban su zana su a cikin littafansu na rubutu.

4. ***Idan ɗalibai suna buƙatar ƙarin tallafi domin mayar da hankali ga aikin da aka basu. Sai…***
    - A jawo hankalinsu zuwa ga allo, a kan duk wani zane ko hoton da zai tallafawa darasin.
        - A lokacin rera waƙa, nuna kowace kalma ko hoto da ke da alaƙa da waƙar, musamman a yayin rera sabuwar waƙa a karon farko.
        - A lokacin da ake nuna abubuwa daban-daban a kan allo, nemi ɗalibai su karanta bayan ka karanta.
        - A bai wa ɗaliban da ba sa mayar da hankali wani aiki na musamman a cikin aji ko a rukuninsu domin ƙarfafarsu su mayar da hankali a kan aikin aji.
        - A karfafa haɗa ɗalibai ƙanana da manya wuri ɗaya, domin su tallafa masu shiga a cikin aikin da aka ba su.

5. ***Idan ɗalibai suna buƙatar* ƙ*arin tallafi a kan ƙidayar lambobi. Sai…***
    - A ba su dama su fara yin ƙidayar da abokansu a cikin rukuninsu, kafin su yi su kaɗai.
    - A samar da wani abu na zahiri kamar itatuwa ko duwatsu ko murfin kwalabe da sauransu da zai ba wa ɗalibai damar taɓawa su lissafa da kansu domin ƙarfafa fahimta a kan lambobi.
    - Umurci ɗalibai su yi amfani da hannayensu da wasu sassan jikinsu ko adadin ɗalibai da ke rukuninsu wajen aikin ƙirge.
    - A madadin saka ɗalibai su yi ƙidaya da takun ƙafa, za a iya ba su umurni su ƙirga adadin ƙiftawar idanunsu ko tafi ko tsalle gwargadon abin da za su iya.

6. ***Idan ɗalibai suna neman ƙarin tallafi a aikin rubuta lambobi, Sai….***
    - A sauƙaƙa matakan rubutun.
        - Da farko, a nuna wa ɗalibai yadda ya kamata a riƙe fensiri.
        - Daga nan, sai a zana dogon layi a allo. Umurci ɗalibai su lura da yadda a ke zanen.
        - Maimaita zana wani layi mai lanƙwasa a ƙasa.
        - A kowane rukuni, rabawa ɗalibai takarda mai ɗauke da waɗannan layuka, domin tallafawa ɗalibai masu buƙata ta musamman. A umurci ɗalibai su kwatanta zana layukan a littafansu na rubutu ta la'akari da takarda da aka ajiye a rukuninsu domin ta yi masu jagora.

7. ***Idan ɗalibai suna buƙatar karin tallafi a kan aikin tarawa, sai…***

- A ƙarfafa masu yin amfani da layin lambobi da ke cikin littafin ɗalibai akai- akai. Su nuna kowace lamba a lokacin da suke lissafin, daga 1 zuwa 100.
  - Umurci ɗalibai su yi amfani da layin lambobi a duk lokacin da suke gabatar da aikin tarawa, har sai sun ƙware da matakan da ake bi wajen aikin tarawar.
- Nuna wa ɗalibai hanyoyi mabanbanta da za su iya gudanar da aikin tarawa. Kamar amfani da abubuwan da za su iya taɓawa ko hotuna ko ta hanyar labari.
- A saka alamar ɗigo a katin nune, da ke nuna adadin lambar da aka rubuta a jikin katin, domin taimaka wa dalibai sauƙin fahimtar adadin da lambar ke wakilta.

8. ***Idan ɗalibai suna buƙatar karin taimako a aikin ɗebewa, sai…***

- A ƙarfafa masu yin amfani da layin lambobi da ke cikin littafin ɗalibai, tare da nuna lambobin daga gaba zuwa baya (100 – 1) a lokacin da suke aikin lissafin.
  - Umurci ɗalibai su yi amfani da layin lambobi a duk lokacin da za su yi lissafin ɗebewa, har sai sun ƙware da matakan da ake bi wajen aikin ɗebewa.
- Nuna wa ɗalibai hanyoyi mabanbanta da za su iya gudanar da aikin ɗebewa. Kamar amfani da abubuwan da za su iya taɓawa ko hotuna ko ta hanyar labari.
- A saka alamar ɗigo a katin nune, da ke nuna adadin lambar da aka rubuta a jikin katin, domin taimakawa ɗaliba sauƙin fahimtar adadin da lambar ke wakilta.

9. ***Idan ɗalibai suna buƙatar tallafi wurin amfani da hannayensu da tafukansu. Sai…***

- A gudanar da 'wasan '**Dankali mai zafi'** a cikin da'ira, ta amfani da ƙwallon takarda domin yin lissafin tsallaken lambobi. Idan yin amfani da kwallon takarda zai yi wahala, ɗalibai zasu iya kiran sunan wanda zai cigaba da lissafin a cikin wasan a madadin jefa kwallon.
- A wurin aikin auna tsawo da faɗi, a yi amfani da mabanbantan kayan awo.
  - A maimakon yin amfani da hannu ko tafin ƙafa wajen awo, a nemi ɗalibai su yi amfani da abubuwan da za a iya samu a cikin aji, kamar littafi ko fensiri ko takarda da sauransu.

| Na. 1 | Zango na 1, Mako na 1, Darasi na A |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya ƙirgen ɗaya zuwa 100 ta amfani da abubuwan ƙirge da kuma Jadawalin lambobi 1-100.

**Kayan Aiki:** Jadawalin lambobi 1-100 **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Wasan Kirge (minti 5)

- A yi wa ɗalibai bayanin cewa za a faɗi wata lamba. Da zarar an faɗi lambar, sai su fara ƙirge daga lambar da sauri. Alal misali, idan aka ce "7," ɗalibai sai su fara faɗin "8, 9 10, 11..."
- Bayan 'yan daƙiƙai kaɗan, sai a ce "su tsaya." Daga nan sai a sake maimaita wannan tsarin da wata sabuwar lamba.

## Koyo

Kirge zuwa 100 (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi yadda ake ƙirge daga 1-100.*
- A yi ƙirge daga 1 zuwa 100 daga jadawalin lambobi na 1-100, tare da nuna kowace lamba a lokacin da ake faɗin ta. A nemi ɗalibai su yi ƙirgen tare da malami.
- A sa ɗaliban ajin su taimaka wajen ƙirga yawan ɗaliban da suke cikin ajin.

| | | | | | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| 1 | 2 | 3 | 4 | 5 | 6 | 7 | 8 | 9 | 10 |
| 11 | 12 | 13 | 14 | 15 | 16 | 17 | 18 | 19 | 20 |
| 21 | 22 | 23 | 24 | 25 | 26 | 27 | 28 | 29 | 30 |
| 31 | 32 | 33 | 34 | 35 | 36 | 37 | 38 | 39 | 40 |
| 41 | 42 | 43 | 44 | 45 | 46 | 47 | 48 | 49 | 50 |
| 51 | 52 | 53 | 54 | 55 | 56 | 57 | 58 | 59 | 60 |
| 61 | 62 | 63 | 64 | 65 | 66 | 67 | 68 | 69 | 70 |
| 71 | 72 | 73 | 74 | 75 | 76 | 77 | 78 | 79 | 80 |
| 81 | 82 | 83 | 84 | 85 | 86 | 87 | 88 | 89 | 90 |
| 91 | 92 | 93 | 94 | 95 | 96 | 97 | 98 | 99 | 100 |

## Gwaji

Aikin ƙaramin rukuni: Kirga abubuwa daga 1-100 (minti 15)

- A sa ɗalibai a ƙananan rukunoni.
- A sa ɗalibai su fita waje su nemo wasu abubuwan ƙirge guda 100. Alal misali; suna iya zagazagawa su nemo kara 100 (ko duwatsu, idan babu kara a wurin).
- Da zarar sun sami kara 100, za su fara gwajin ƙirge daga 1-100, suna nuna kowane ɗaya daga cikin karan, daidai da lambar da ta dace da shi lokacin da suke ƙirgen.
- A zaga ana lura da ɗalibai. A yayin zagawar, a duba ko sun ba da amsa daidai, a kuma taimaka musu idan akwai buƙatar hakan.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A nuna wata lamba ba bisa tsari ba a kan Jadawalin Lambobin 1-100 sai a ce ɗalibai su faɗe ta.

## Aikin gida

A nemi ɗalibai su yi gwajin yin ƙirge daga 1-100.

| Na. 2 | Zango na 1, Mako na 1, Darasi na B |
|---|---|

# Zango na 1, Mako na 1, Darasi na B

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya ƙirgen bibbiyu da biyar-biyar zuwa 100 ta amfani da abubuwan ƙirge da kuma Jadawalin lambobi 1-100

**Kayan Aiki:** Jadawalin lambobi 1-100 da kara 200 da katunan lamba 1-100 **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Wasan Kirge (minti 3)

- A yi wa ɗalibai bayanin cewa za a faɗi wata lamba. Da zarar an faɗi lambar, sai su fara ƙirgawa da bibbiyu da sauri. Alal misali, idan aka ce "62," ɗalibai sai su fara faɗin "64, 66 68, 70..."
- Bayan 'yan diƙaƙai kaɗan, sai a ce "su tsaya." Daga nan sai a sake maimaita wannan tsarin da wata sabuwar lamba.

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

## Koyo

Kirgen bibbiyu zuwa 100 (minti 5)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi yadda ake ƙirgen bibbiyu da biyar-biyar zuwa 100.*
- A yi ƙirgen tsallaken lamba da bibbiyu a fara daga 2 zuwa 100 yayin da ake nuna lamba daga Jadawalin 1 zuwa 100. A nemi ɗalibai su yi ƙirgen tare da malami. A tambayi ɗalibai ko sun lura da wani tsari?
- **Ka/ki ce:** *Duk lokacin da kuka yi ƙirgen tsallaken lamba da bibbiyu kuka fara daga 2, lambar ko dai ta ƙare da 0 ko 2 ko 4 ko 6 ko kuma 8.*

| | | | | | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| 1 | 2 | 3 | 4 | 5 | 6 | 7 | 8 | 9 | 10 |
| 11 | 12 | 13 | 14 | 15 | 16 | 17 | 18 | 19 | 20 |
| 21 | 22 | 23 | 24 | 25 | 26 | 27 | 28 | 29 | 30 |
| 31 | 32 | 33 | 34 | 35 | 36 | 37 | 38 | 39 | 40 |
| 41 | 42 | 43 | 44 | 45 | 46 | 47 | 48 | 49 | 50 |
| 51 | 52 | 53 | 54 | 55 | 56 | 57 | 58 | 59 | 60 |
| 61 | 62 | 63 | 64 | 65 | 66 | 67 | 68 | 69 | 70 |
| 71 | 72 | 73 | 74 | 75 | 76 | 77 | 78 | 79 | 80 |
| 81 | 82 | 83 | 84 | 85 | 86 | 87 | 88 | 89 | 90 |
| 91 | 92 | 93 | 94 | 95 | 96 | 97 | 98 | 99 | 100 |

Kirgen biyar-biyar zuwa 100 (minti 5)

- A yi ƙirgen tsallaken lamba da biyar-biyar a fara daga 5 zuwa 100 yayin da ake nuna lambar da ake ƙirgawa a kan Jadawalain Lambobi 1-100. Malami ya nemi ɗalibai su yi ƙirgen tare. A tambayi ɗalibai ko sun lura da wani tsari?
- **Ka/ki ce:** *Duk lokacin da muka yi ƙirgen tsallaken lamba da biyar-biyar muka fara da 5, lambar za ta ƙare ko da da 5 ko kuma 0.*

## Gwaji

Aikin ƙaramin rukuni: Kirgen abubuwa da bibbiyu da kuma biyar-biyar zuwa 100 (minti 15)

- A raba aji zuwarukuni 2. A ba kowane rukuni kara guda 100.
- A ɗaga katunan lamba masu lambobi bibbiyu sai a faɗi lambar a bayyane.
- A sa ɗalibai su ƙirga lambar da ta yi daidai da yawan kara, sannan su raba su a cikin rukunoni biyu.
- Bayan wani ɗan lokaci, a ɗaga katunan lamba masu lambobi biyar-biyar sai a faɗi lambar a bayyane. A nemi ɗalibai su ƙirga lambar da ta yi daidai da ita da yawan kara sannan su raba su a cikin rukunoni biyar.
- A zagaya ana lura da ɗalibai. A yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai yadda suka samo amsarsu, a kuma tabbatar idan daidai suke.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A zana katin lamba mai ɗauke da lamba ta bibbiyu ko ta biyar-biyar ba kan tsari ba.
- A kira wani ɗalibi ɗaya gaban aji ya nuna lambar ta yi daidai da lambar katin a kan Jadawalin Lambobi 1-100. Idan akwai lokaci, a maimaita haka da wata lambar.

## Aikin Gida

A nemi ɗalibai su yi gwajin ƙirge da bibbiyu da kuma biyar-biyar zuwa 100 a gida.

| Na. 3 | Zango na 1, Mako na 1, Darasi na C |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su yi ƙirge da goma-goma zuwa 100 ta amfani da damin kara da kuma Jadawalin lambobi 1-100.
**Kayan Aiki:** Jadawalin lambobi 1-100 da kara da robar ɗauri **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

<u>Kirge daga 1-100 (minti 3)</u>

- A yi ƙirge daga 1-100 daga Jadawalin Lambobi 1-100, a nuna kowace lamba lokacin faɗinta. Malami/malama ya/ta nemi ɗalibai su yi ƙirgen tare.

<u>Duba aikin gida (minti 2)</u>

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu, sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

## Koyo

<u>Kirgen goma-goma zuwa 100 (minti 8)</u>

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi yadda ake ƙirgen goma-goma zuwa 100.*
- A nemi ɗalibai goma su zo gaban aji.
- **Ka/ki ce:** *Yatsu nawa kuke da su?*
- Umurci ɗalibai su ɗaga hannayensu, ta yadda duk 'yan ajin za su ga yatsun nasu.
- **Ka/ki ce:** *Kirga yatsun ɗaya bayan ɗaya yana da tsaiko sosai. Saboda muna da yatsu guda goma ne, muna iya yin ƙirge da goma-goma har mu kai 100.*

| | | | | | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| 1 | 2 | 3 | 4 | 5 | 6 | 7 | 8 | 9 | 10 |
| 11 | 12 | 13 | 14 | 15 | 16 | 17 | 18 | 19 | 20 |
| 21 | 22 | 23 | 24 | 25 | 26 | 27 | 28 | 29 | 30 |
| 31 | 32 | 33 | 34 | 35 | 36 | 37 | 38 | 39 | 40 |
| 41 | 42 | 43 | 44 | 45 | 46 | 47 | 48 | 49 | 50 |
| 51 | 52 | 53 | 54 | 55 | 56 | 57 | 58 | 59 | 60 |
| 61 | 62 | 63 | 64 | 65 | 66 | 67 | 68 | 69 | 70 |
| 71 | 72 | 73 | 74 | 75 | 76 | 77 | 78 | 79 | 80 |
| 81 | 82 | 83 | 84 | 85 | 86 | 87 | 88 | 89 | 90 |
| 91 | 92 | 93 | 94 | 95 | 96 | 97 | 98 | 99 | 100 |

- A nuna wa ɗalibai yadda ake yin ƙirge zuwa 100 ta amfani da yatsunsu a matsayin misali.
- Malami ya nuna wa ɗalibai yadda ake yin ƙirgen goma-goma a kan jadawalin lambobi 1-100. Lokacin da malami yake ƙirgen, ya nuna kowace lamba da ya faɗi sannan ya sa ɗalibai su maimaita lambar bayan ya faɗi.

## Gwaji

<u>Aikin ƙaramin rukuni: Samar da damin goma-goma (minti 20)</u>

- Umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunoni.
- A naɗa jagora a kowane rukuni da zai taimaka wajen rarraba dukkan karan da aka tattara a wannan makon.
- A nuna yadda ake ƙirgen kara goma da kuma ɗaure su a cikin dami guda da robar ɗauri.
- **Ka/ki ce:** *Wannan tarin na rukunin kara guda goma ana iya kiransa ɗaurin goma.*
- A yi wa ɗalibai bayanin cewa su yi ƙoƙarin samar da ɗaurin kara goma gwargwadon yawan yadda za su iya yi.
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai. A yayin zagayawar, a kula ko suna yin aikin daidai, a kuma taimaka musu idan akwai buƙatar hakan.

## Bayyanawa

<u>Auna fahimta nan-take (minti 2)</u>

- A nuna wata lamba (10, 20, 30, 40, 50, 60, 70, 80, 90, ko 100) ba bisa wani tsari ba a kan Jadawalin Lambobi 1-100 sai a nemi ɗalibai su karanta lambar.

## Aikin Gida

A nemi ɗalibai su yi gwajin ƙirgen goma-goma zuwa 100 a gida.

| Na. 4 | Zango na 1, Mako na 1, Darasi na D |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su cike lambobin da babu tsakaninlamba 1-100.
**Kayan Aiki:** Katin lambobi da Jadawalin Lambobi 1-100 **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Ni wace lamba ce? (minti 5)

- A karanta kowane daga cikin waɗannan jawaban. A nemi ɗalibai su ba da amsa tare da faɗin lambar a bayyane. Idan ɗaliban sun ba da amsa daidai, a nuna lambar da suka karanta a kan jadawalin lambobi 1-100.
- **Ka/ki ce:** *Da 1 na fi 99. Wace lamba nake?*
- **Ka/ki ce:** *Da 5 na fi 25. Wace lamba nake? A ci gaba da wasu misalai.*

**Koyo**

Gabatar da lambobin da babu (minti 8)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu nemo lambobin da babu.*
- A sa ɗalibai 10 su zo gaban aji. Kowannensu ya ɗauki katin lamba guda sannan sai su jera kansu bisa tsari daga 1 zuwa 10. Za su ɗaga katin lambobinsu sama ta yadda dukkan sauran ɗaliban aji za su gane su.
- **Ka/ki ce:** Muna da ɗalibai 10, masu lambobi 1-10.
- A sa ɗalibin da yake ɗauke da lamba ta 2, ya duƙa ya ɓoye katin lambarsa.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu dole mu yi tunanin, wace lamba ce ta ɓata? Wace lamba ce ke zuwa bayan 1 ko kuma kafin 3?*
- A maimaita aikin da wasu ɗalibai daban, su duƙa, domin nuna wasu lambobi daban-daban da babu.

**Gwaji**

Aikin a cikin ƙaramin rukuni: Wasan gyara-tsari (minti 10)

- A umurci ɗalibai su zauna cikin ƙanana rukunoni da ba su wuce ɗalibai 4 ba. Kowane rukuni su zaɓi jagora ɗaya.
- **Ka/ki ce:** *Wani lokaci tsarin lambobi na iya tsallake ƙirge da bibbiyu ko biyar-biyar ko kuma goma-goma.*
- A rubuta lambobin "80 da 82 da 84, ___, 86 da 88" a kan allo.
- **Ka/ki ce** *Wace lamba ce babu a tsarin?*
- A sa ɗalibai su yi aiki tare domin su gano lambar da babu. Ɗaliban su rubuta amsarsu a cikin littafansu na rubutu.
- A gayyota rukuni 1 ko 2 su faɗi amsoshinsu, su kuma yi bayanin idan sun yi ƙirgen ne da ɗaiɗai ko bibbiyu ko biyar-biyar ko kuma goma-goma.
- A maimiata aikin da wasu misalan ƙirgen tsarin lambobi na ɗaiɗai ko bibbiyu ko biyar-biyar ko kuma goma-goma.

**Bayyanawa**

Gwajin aikin gida (minti 10)

- A buɗe littafin ɗalibai shafi na 5 sannan a karanta umurnin ciki.
- A yi aiki na farko tare da ɗalibai a aji. Ɗalibai su juyi aikin a cikin littafan rubutu.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 5 a cikin littafin rubutunsu.

| Na. 5 | Zango na 1, Mako na 1, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi bita da gwajin abin da suka koya a cikin wannan makon.
**Kayan Aiki:** Jadawalin Lambobi 1-100 **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masugwiwa.

Kirge daga 1-100 (minti 5)

- A yi ƙirgen 1-100 a kan jadawalin lambobi 1-100, ana nuna kowace lamba yayin da aka faɗe ta. A ce ɗalibai su yi karatun tare da kai.

| | | | | | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| 1 | 2 | 3 | 4 | 5 | 6 | 7 | 8 | 9 | 10 |
| 11 | 12 | 13 | 14 | 15 | 16 | 17 | 18 | 19 | 20 |
| 21 | 22 | 23 | 24 | 25 | 26 | 27 | 28 | 29 | 30 |
| 31 | 32 | 33 | 34 | 35 | 36 | 37 | 38 | 39 | 40 |
| 41 | 42 | 43 | 44 | 45 | 46 | 47 | 48 | 49 | 50 |
| 51 | 52 | 53 | 54 | 55 | 56 | 57 | 58 | 59 | 60 |
| 61 | 62 | 63 | 64 | 65 | 66 | 67 | 68 | 69 | 70 |
| 71 | 72 | 73 | 74 | 75 | 76 | 77 | 78 | 79 | 80 |
| 81 | 82 | 83 | 84 | 85 | 86 | 87 | 88 | 89 | 90 |
| 91 | 92 | 93 | 94 | 95 | 96 | 97 | 98 | 99 | 100 |

## Koyo

Bita da maimai (minti 8)

- A zaɓi wani darasi daga cikin darrusan da aka yi a cikin makon, wanda ake ganin ɗalibai ba su fahimce shi sosai ba. A sake koyar da darasin ko a sake koyar da shi ta wata sabuwar hanya ta daban.

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai a cikin rukuni: Zane da kuma rubutu (minti 15)

- A ba ɗalibai aikin da zai taimaka musu wajen yin gwajin darasin da aka yi bita (alal misali; ƙirge zuwa 100 da ɗaiɗai ko nemo lambar da babu a cikin wani tsari). Ɗalibai na iya yin aiki ɗaiɗaya ko kuma a cikin ƙananan rukunoni.
- Yayin da ɗalibai suke gudanar da wani aikin da aka ba su, a ƙara taimaka musu a inda ba su gane sosai ba.

## Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala a lokacin Gwajin.

## Aikin Gida

A ba ɗalibai aikin gida na bita da kuma gwajin ƙwazonsu.

| Na. 6 | Zango na 1, Mako na 2, Darasi na A |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya tara lambobi tare da haɗa su har zuwa 20 ta amfani da abubuwan da ake samu a cikin aji da kuma labarai.
**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge (wake ko tsakuwoyi) **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai sau da yawa.
- A nemi ɗaya daga cikin ɗalibai ya zo gaban aji ya rera waƙar.

Waƙar Tarawa
Ana batun tarawa /
Komai a tara da ɗaya /
1+1= 2 / 2+1= 3 / 3+1= 4 /
4+1= 5 / 5+1= 6 / 6+1= 7 /
7+1= 8 / 8+1= 9 / 9+1= 10

## Koyo

Gabatar da tara lambobi daga lamba 1-20 (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi yadda ake tara lambobi daga lamba ɗaya zuwa ashirin.*
- A kira ɗalibai goma su zo a gaban aji. A nemi ɗalibai su faɗi mutane nawa ne ke gaban ajin.
- A ƙara kiran wasu ɗalibai shida a gaban ajin.
- **Ka/ki ce:** *Karin wasu ɗalibai shida sun shigo rukunin. Ɗalibai nawa ne gaban ajin gaba ɗaya yanzu?*
- A ƙirga yawan adadin ɗaliban ajin a bayyane tare da dukkan ɗaliban ajin.
- **Ka/ki ce:** *Ɗalibai 10 da kuma ɗalibai 6 sun zama ɗalibai 16 ke nan gaba ɗaya. Ku tuna, haɗa rukunin waɗannan abubuwan wuri guda kamar haka shi ake kira tarawa.*
- A maimaita haka da adadin ɗalibai daban-daban.

## Gwaji

Aikin ƙananan rukunoni: Tarawa da abubuwan ƙirge (minti 15)

- A umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunoni: A zaɓi jagora daga cikin kowane rukunin da zai taimaka wajen rarraba abubuwan ƙirge 20 ga rukuninsu.
- **Ka/ki ce:** *Ɗalibi guda a cikin rukunin ya ɗauki abubuwan ƙirge 14 ya aje su a tsakiyar rukuninsu. Sannan sai wani ɗalibi daban kuma ya ɗauki ƙarin wasu abubuwan ƙirge uku ya haɗa su da na tsakiyar.*
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai a kuma tabbata ɗaliban suna saka lambobin abubuwan ƙirge da suke daidai a tsakiyarsu.
- **Ka/ki ce:** *Abubuwan ƙirge nawa gare mu gaba ɗaya?*
- Idan da lokaci, a sake maimaitawa da wani labarin. A tabbata ɗalibai suna jujjuyawa wajen amfani da abubuwan ƙirgen.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- Yi wa ɗalibai bayanin cewa za ka faɗi wani lissafin tarawa.
- **Ka/ki ce:** *Akwai tsuntsaye 15 a kan bishiya. Karin wasu tsuntsaye 2 sun hau a kan bishiyar. Tsuntsaye nawa ne a kan bishiyar gaba ɗaya?*
- A nemi ɗalibai su ɗaga hannuwansu sama idan sun san amsar tambayar.
- Idan akwai lokaci, a maimaita ta amfani da wasu lambobi daban.

## Aikin Gida



A sa ɗalibai su yi gwajin lissafin tara tsakuwoyitare da wani daga cikin 'yan'uwansu ko abokansu.


| Na. 7 | Zango na 1, Mako na 2, Darasi na B |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya tara lambobi tare da haɗa su har zuwa 20 ta amfani da abubuwan ƙirge da kuma gidan dara goma.

**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge (wake ko tsakuwoyi) **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)




- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa

Labari da kuma Hotuna (minti 3)

- Bayyana labarin hotunan kan allo. Amina ta ɗauki damin fulawa 13 don ta ba ƙawarta Nana. A kan hanyarta ta zuwa gida sai ta ƙara samun wasu fulawoyi guda 2. Fulawoyi nawa gare ta gabaɗaya kenan?
- A nemi ɗalibi guda ya zo gaban aji ya gwajin yadda labarin yake.

## Koyo

Tarawa ta amfani da gidan dara goma (minti 10)



- **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi gwajin lissafin tarawa zuwa 20 ta amfani da gidan dara goma-goma.*
- A yi gwajin labarin ta amfani da gidan dara da ke kan allo. A saka ɗigo-ɗigo goma sha uku a cikin gidan dara, sannan sai a ƙara wasu biyu don su kasance goma sha biyar.
- A maimaita da wani adadin yawan fulawoyi daban. A nemi ɗalibai su zo gaban allo su yi gwajin gano jimillar yawan fulawoyin, ta amfani da gidan dara goma.

## Gwaji

Aikin ƙaramin rukuni: Tarawa da gidan dara goma (minti 10)

- A nemi ɗalibai su zauna a cikin ƙananan rukunoni: A zaɓi jagora daga cikin kowane rukuni da zai taimaka wajen rarraba littafin ɗalibai da abubuwan ƙirge 20 ga rukuninsu. Nemi ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai inda yake da gidan dara goma da babu komai a cikinsu.
- **Ka/ki ce:** *Kaji sun yi ƙwai 8 jiya, suka yi ƙwai 6 a yau. Kwai nawa kenan gabaɗaya?*
- A sa ɗalibai su yi amfani da abubuwan ƙirge da gidan dara goma wajen gwajin wannan labarin.
- A zagaya ana lura lokacin da ake maimaita karanta labarin.
- Idan akwai lokaci, a sake maimaitawa da wani labarin. A tabbata ɗalibai suna jujjuyawa wajen amfani da abubuwan ƙirgen.

## Bayyanawa

Gwajin aikin gida (minti 10)

- A buɗe littafin ɗalibai shafi na 6 sannan a karanta umurnin ciki.
- A yi aiki na farko tare da ɗalibai a aji. Ɗalibai su juyi aikin a cikin littafan rubutunsu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 6 a cikin littafin rubuturubutunsu a gida.


| Na. 8 | Zango na 1, Mako na 2, Darasi na C |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya tara lambobi tare da haɗa su har zuwa 20 ta amfani da abubuwan ƙirge da gidan dara goma da kuma alamar + .
**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge wake ko tsakuwoyi) da gidan dara goma-goma **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafi gwiwarsu.




Labari da kuma Hotuna (minti 3)

- A bayyana labarin hotunan kan allo. Abubakar ya sami goro guda shida. Washegari a makaranta, abokinsa ya ƙara ba shi wasu goro guda biyar.
- A nemi ɗaya daga cikin ɗalibai ya zo gaban aji ya yi gwajin yadda labarin yake.

## Koyo

Tarawa ta amfani da gidan dara goma da kuma alamar + (minti 10)



- **Ka/ki ce:** *Yau mun yi gwajin tarawa har zuwa 20 ta amfani da gidan dara goma. Haka ma za mu yi gwajin rubuta fasalin lissafi ta amfani da alamomin + da = .*
- A yi gwajin labarin ta amfani da gidan dara goma dake kan allo. A a yi ɗigo-ɗigo guda 6 a cikin gidan dara 10, daga nan sai a ƙara wasu guda 5 don su cike guda 11.A rubuta fasalin daidaito na 6 + 5 = 11 kan allo. A yi bayanin cewa fasalin lissafiyana bayyana labarin.
- **Ka/ki ce:** *Kasancewar Abubakar yana da goro guda shida sannan abokinsa ya ba shi ƙarin wasu guda 5, yana da jimillar goro goma sha ɗaya, muna iya rubuta 6 + 5 = 11. Goro shida da goro 5, daidai suke da goro goma sha ɗaya.*
- A sake maimaita labarin da wani adadin yawan goro na daban, ta amfani da gidan dara. A nemi ɗalibai su zo gaban aji su yi gwajin yadda ake gano jimillar yawan goron, ta amfani da gidan dara.

## Gwaji

Aikin ƙaramin rukuni: Tarawa da gidan dara goma da kuma alamar + (minti 10)

- A nemi ɗalibai su zauna a cikin ƙananan rukunoni: A zaɓi jagora daga cikin kowane rukuni da zai taimaka wajen rarraba littafin ɗalibai da kuma abubuwan ƙirge 20 ga rukuninsu. Nemi su buɗe littafin ɗalibai inda yake da gidan dara goma da babu komai a cikinsu.
- **Ka/ki ce:** *A gidansu Mustapha suna da awaki 15. Mahaifinsa ya ƙara sawo wasu guda 3. Jimillar awaki nawa kenan gabaɗaya?*
- A sa ɗalibai su yi amfani da abubuwan ƙirge da gidan dara goma wajen gwajin wannan labarin.
- A zagaya ana lura da ɗaliban. A nemi ɗalibai su faɗi yadda za su rubuta lissafin daidaiton.
- Idan akwai lokaci, a sake maimaitawa da wani labarin. A tabbata ɗalibai suna jujjuyawa wajen amfani da abubuwan ƙirgen.

## Bayyanawa

Gwajin aikin gida (minti 10)

- A buɗe littafin ɗalibai shafi na 7 sannan a karanta umurnin ciki.
- A yi aiki na farko tare da ɗalibai a aji. Ɗalibai su juyi aikin a cikin littafan rubutu.

## Aikin Gida


A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 7 a cikin littafin rubutunsu.

| Na. 9 | Zango na 1, Mako na 2, Darasi na D |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya tara lambobi tare da haɗa su har zuwa 20 ta amfani da abubuwan ƙirge da gidan dara goma da kuma alamar +.

**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge (wake ko tsakuwoyi) da layin lamba **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi




Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masugwiwa.

Labari da kuma Hotuna (minti 3)

- Bayyana labarin hotunan kan allo. Tsuntsaye goma sha biyar suna kan bishiya. Wasu ƙarin tsuntsaye huɗu sun tarar da su a kan bishiyar.
- A nemi ɗalibai goma sha tara su zo gaban aji su yi gwajin yadda labarin yake.

## Koyo




Tarawa ta amfani da layin lamba da kuma alamar + (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu tara lambobi ta amfani da layin lamba.*
- A yi gwajin labarin ta amfani da layin lamba da ke kan allo. A kewaye lamba 15 domin nuna adadin yawan tsuntsayen da ke kan bishiyar. Daga nan, sai a yi amfani da layin lamba don ƙirga yawan tsuntsayen da suka ƙaru a kan bishiyar.
- A rubuta fasalin lissafi na15 + 4 = 19 kan allo. A yi bayanin cewa fasalin lissafi yana bayyana labarin tsuntsayen da ke kan bishiyar.
- A sake maimaita labarin da wani adadin tsuntsayen. A nemi ɗalibai su zo gaban aji su yi gwajin yadda ake gano jimillar yawan tsuntsayen ta amfani da layin lamba.

## Gwaji

Aikin ƙaramin rukuni: Tarawa da layin lamba (minti 10)

- A nemi ɗalibai su zauna a cikin ƙananan rukunoni: A zaɓi jagora daga cikin kowane rukuni da zai taimaka wajen rarraba littafin ɗalibai da kuma abubuwan ƙirge 20 ga rukuninsu. Nemi ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai inda aka kawo layin lamba.
- **Ka/ki ce:** *Shanu 13 suna kiwo a cikin fili. Wasu ƙarin 4 sun tarar da su. Jimillar shanu nawa kenan gabaɗaya?*
- A sa ɗalibai su yi amfani da abubuwan ƙirge da layin lamba wajen gwajin wannan labarin.
- A zagaya ana lura da ɗaliban lokacin da ake maimaita labarin, a yayin zagayawar, a tambaye su yadda suka sami amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.
- Idan akwai lokaci, a sake maimaitawa da wani labarin. A tabbata ɗalibai suna jujjuyawa wajen amfani da abubuwan ƙirgen.

## Bayyanawa

Gwajin aikin gida (minti 10)

- A buɗe littafin ɗalibai shafi na 8 sannan a karanta umurnin ciki.
- A yi aiki na farko tare da ɗalibai a aji. Ɗalibai su juyi aikin a cikin littafan rubutunsu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 8 a cikin littafin rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 10 | Zango na 1, Mako na 2, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi bita da gwajin abin da suka koya a cikin wannan makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Waƙar Tarawa
Ana batun tarawa /
Komai a tara da ɗaya /
1+1= 2 / 2+1= 3 / 3+1= 4 /
4+1= 5 / 5+1= 6 / 6+1= 7 /
7+1= 8 / 8+1= 9 / 9+1= 10

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai sau da yawa.
- A nemi ɗaya daga cikin ɗalibai ya zo gaban aji ya rera waƙar.

**Koyo**

Bita da maimai (minti 10)

- A zaɓi wani darasi daga cikin darussan da aka yi a cikin makon, wanda ake ganin ɗalibai ba su fahimce shi sosai ba. A sake koyar da darasin ko a sake koyar da shi ta wata sabuwar hanya daban.

**Gwaji**

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai a cikin rukuni: Zane da kuma rubutu (minti 10)

- A bai wa ɗalibai aikin da zai taimaka musu wajen yin gwajin darasin da aka yi bita (alal misali; tarawa har zuwa ashirin ta amfani da gidan dara goma ko layin lamba. Ɗalibai suna iya yin aiki ɗaiɗai ko kuma a cikin ƙananan rukunoni.
- Yayin da ɗalibai suke gudanar da wani aikin da aka ba su, a ƙara taimaka musu a inda ba su gane sosai ba.

**Bayyanawa**

Gwajin aikin gida (minti 10)

- A buɗe littafin ɗalibai shafi na 9 sannan a karanta umurnin ciki.
- A yi aiki na farko tare da ɗalibai a aji. Ɗalibai su juyi aikin a cikin littafan rubutu.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 9 a cikin littafin rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 11 | Zango na 1, Mako na 3, Darasi na A |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iyai lissafin ɗebewa tsakanin 1-20 ta amfani da abubuwan da ake samu a cikin aji da kuma labarai.
**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge (ƙwayar wake ko tsakuwoyi) **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafi gwiwarsu.

Waƙa (minti 2)

- A rera waƙar tare da ɗalibai.

| | |
|---|---|
| Oyoyo oyoyo<br>Oyoyo Baba ya dawo<br>Ya dawo daga kasuwa<br>Ya sawo muna goriba<br>Ni an bani guda huɗu | Na ci daya saura uku<br>In ya ci ɗaya saura biyu<br>In ta ci ɗaya saura ɗaya<br>In ka ci ɗaya ba ko daya |

**Koyo**

Gabatar da lissafin ɗebewa (minti 10)

- **Ka/ki ce:**_A yau za mu koyi yadda ake ɗebewa daga lamba ɗaya zuwa ashirin._
- A kira ɗalibai ashirin su zo a gaban aji. A nemi cewa ɗalibai nawa ne ke gaban ajin.
- A nemi ɗalibai goma sha biyu su zauna.
- **Ka/ki ce:**_Muna da ɗalibai ashirin, daga nan sha biyu daga cikinsu suka zauna. Yanzu ɗalibai nawa suka rage mana a tsaye._
- A ƙirga adadin yawan ɗaliban a bayyane tare da aji gaba ɗaya.
- **Ka/ki ce:**_Idan kana da 20, sai ka cire 12, saura takwas. A tuna, cire adadin abubuwa kamar haka shi ake kira ɗebewa._
- A maimaita haka da adadin ɗalibai daban-daban.

**Gwaji**

Aikin ƙaramin rukuni: Ɗebewa da abubuwan ƙirge (minti 15)

- A nemi ɗalibai su zauna a cikin ƙananan rukunoni: A zaɓi jagora daga cikin kowane rukuni da zai taimaka wajen rarraba abubuwan ƙirge 20 ga rukuninsu.
- **Ka/ki ce:**_Ɗalibi ɗaya a cikin rukuninku ya ɗauki abubuwan ƙirge 16 ya aje su a tsakiyar rukunin. Sannan sai wani ɗalibi daban kuma ya cire abubuwan ƙirge 2 daga cikin rukunin 16._
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai a kuma tabbatar ɗalibai a kowane rukuni suna cire lambar da tadace.
- **Ka/ki ce:**_Abubuwan ƙirgen nawa suka rage?_
- Idan akwai lokaci, a sake maimaitawa da wani labarin. A tabbata ɗalibai sun jujjuyawa amfani da abubuwan ƙirgen.

**Bayyanawa**

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- Yi wa ɗalibai bayanin cewa za ka faɗi wani aikin lissafin ɗebewa sannan sai su warware aikin.
- **Ka/ki ce:**_Akwai tsuntsaye 17 a kan bishiya. Tsuntsaye 4 suka tashi daga kan bishiyar. Tsuntsaye nawa suka ragea kan bishiyar?_
- A nemi ɗalibai su ɗaga hannuwansu sama idan sun san amsar tambayar.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su yi gwajin lissafin ɗebe tsakuwoyi a gida tare da wani daga cikin 'yan'uwansu ko abokansu.

Na. 12

# Zango na 1, Mako na 3, Darasi na B

**Manufa:** Ɗalibai za su iya lissafin ɗebewa daga lamba 1-20 ta amfani da abubuwan ƙirge da kuma gidan dara goma.

**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge (ƙwayar wake ko tsakuwoyi) **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.


Labari da kuma Hotuna (minti 3)

- A karanta labarin dake cikin hotunan a kan allo. Ɗalibai 20 suna cikin jirgin ruwa. 9 daga cikinsu sun tsallaka cikin ƙorama domin su yi iyo.
- A nemi ɗalibi 20 su zo gaban aji su yi gwajin yadda labarin yake.

## Koyo

Ɗebewa ta amfani da gidan dara goma (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau zamu yi gwajin lissafin ɗebewa ta amfani da gidan dara goma.*
- A yi gwajin labarin ta amfani da gidan dara goma dake kan allo. A yiɗigo-ɗigo a gidan dara goma, sannan sai a goge ɗigo tara su koma 10.
- A maimaita da wani labari daban da kuma wasu adadin ɗalibai daban. A nemi wani ɗalibi ya yiɗigo-ɗigo daidai yawan da suke a cikin gidan dara goma.



## Gwaji

Aikin ƙaramin rukuni: Ɗebewa da gidan dara goma (minti 15)

- A umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunoni: A zaɓi jagora daga cikin kowane rukuni da zai taimaka wajen rarraba littafin ɗalibai da abubuwan ƙirge 20 ga rukuninsu. Nemi ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai inda yake da gidan dara goma da babu komai a cikinsu.
- A karanta labarin ga ƙananan rukunonin ɗaliban sannan sai a sa ɗalibai su yi amfani da abubuwan ƙirge da gidan dara goma wajen gwajin wannan labarin.
- **Ka/ki ce:** *Mage 14 suna wasa a cikin lambu. Mage 11 sun tafi. Mage nawa aka bari?*
- A zagaya ana lura lokacin da ake maimaita karanta labarin. Yayin zagayawar, a tambaye su yadda suka samar da amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.
- Idan akwai lokaci, a sake maimaitawa da wani labarin. A tabbata ɗalibai sun jujjuyawa amfani da abubuwan ƙirgen.

## Bayyanawa

Gwajin aikin gida (minti 10)

- A buɗe littafin ɗalibai shafi na 10 sannan a karanta umurnin da ke ciki.
- A yi aiki na farko tare da ɗalibai a aji. Ɗalibai su juyi aikin a cikin littafin rubutunsu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 10 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

| Na. 13 | Zango na 1, Mako na 3, Darasi na C |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya lissafin ɗebewa daga lamba 1-20 ta amfani da abubuwan ƙirge da kuma gidan dara goma da kuma alamar - .
**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge (ƙwayar wake ko tsakuwoyi) da gidan dara goma **Lokaci:** Minti 35


## Fara Darasi

<u>Duba aikin gida (minti 2)</u>

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masugwiwa.

<u>Labari da kuma Hotuna (minti 3)</u>


- A karanta labarin dake cikin hotunan a kan allo. Akwai tsuntsaye 15 a kan bishiya. Tsuntsaye 9 daga cikinsu sun tashi suka bar kan bishiyar.
- A nemi ɗalibi 15 su zo gaban aji su yi gwajin yadda labarin yake.



## Koyo

<u>Ɗebewa ta amfani da gida dara goma da kuma alamar - (minti 10)</u>

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi darasi a kan alamar ɗebewa -.*
- A yi gwajin labarin ta amfani da gidan dara goma da ke kan allo. A yi ɗigo-ɗigo 15 a cikin gidan dara goma, daga nan sai a goge tara daga cikin dɗigo-ɗigo su koma 6 kawai.
- A rubuta fasalin lissafi na 15 - 9 = 6 a kan allo. A yi bayanin cewa wannan fasalin fasalin yana bayanin labarin tsuntsayen nan ne da suke kan bishiya.



- **Ka/ki ce:** *Alamar – tana nuna ɗebewa. Ɗebewa tana nufin a cire rukunin wasu abubuwa ko kuma lambobi daga cikin wani rukuni. Tana da alaƙa da lambobin da ake ɗebewa a cikinsu. Alamar = tana zuwa ne kafin adadin jimillar abubuwan da ake magana a kai. Tsuntsaye 15 - tsutsaye 9 = jimillar tsuntsaye 6.*
- A sake maimaitawa da wani labari da kuma wasu ɗalibai daban. A nemi wani ɗalibi ya zana hoton adadin yawan ɗigo-ɗigoda suke daidai a cikin gidan dara goma.

## Gwaji

<u>Aikin ƙaramin rukuni: Ɗebewa da gidan dara goma da kuma alamar - (minti 10)</u>

- A umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunoni: A zaɓi jagora daga cikin kowane rukuni da zai taimaka wajen rarraba littafin ɗalibaida kuma abubuwan ƙirge 20 ga rukuninsu. Nemi ɗalibai su buɗe littafin ɗalibaiinda yake da gidan dara goma da babu komai a cikinsu.
- **Ka/ki ce:** *A gidansu Mustapha suna da awaki guda 20. Mahaifinsa ya sayar da 4 daga ciki. Awaki nawa suka rage?*
- A sa ɗalibai su yi amfani da abubuwan ƙirge da gidan dara goma wajen gwajin wannan labarin.
- A zagaya ana lura da ɗaliban, yayin da ake maimaita labarin. A nemi ɗalibai su faɗi yadda za su rubuta fasalin lissafin.
- Idan akwai lokaci, a sake maimaitawa da wani labarin. A tabbata ɗalibai sun jujjuyawa amfani da abubuwan ƙirgen.

## Bayyanawa

<u>Gwajin aikin gida (minti 10)</u>

- A buɗe littafin ɗalibai shafi na 11 sannan a karanta umurnin da ke ciki.
- A yi aiki na farko tare da ɗalibai a aji. Ɗalibai su juyi aikin a cikin littafin rubutunsu.

## Aikin Gida


A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 11 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

| Na. 14 | Zango na 1, Mako na 3, Darasi na D |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya lissafin ɗebewa daga lamba 1-20 ta amfani da layin lamba da kuma alamar -
**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge (ƙwayar wake ko tsakuwoyi) da layin lamba **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

<u>Duba aikin gida (minti 2)</u>




- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

<u>Labari da kuma Hotuna (minti 3)</u>

- A karanta labarin dake cikin hotunan a kan allo. Akwai shanu 16 a cikin fili. 3 sun tafiyarsu.
- A nemi ɗalibai goma sha shida su zo gaba aji su yi gawajin yadda labarin yake.

## Koyo

<u>Ɗebewa ta amfani da layin lamba da kuma alamar - (minti 10)</u>




- **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi lissafin ɗebewa ta amfani da layin lamba.*
- A yi gwajin labarin ta amfani da layin lamba dake kan allo. A yi da'ira a kan 16 domin nuna adadin yawan shanun dake cikin filin. Daga nan, sai a yi amfani da layin lamba don ƙirga yawan shanun da suka tafi.
- A rubuta fasalin lissafi na 16 - 3 = 3 kan allo. A yi bayanin cewa fasalin lissafin yana bayyana labarin shanun.
- A sake maimaita labarin da adadin wasu ɗalibai. A nemi wani ɗalibi ya zo gaban aji ya warware aikin lissafin ta amfani da layin lamba.

## Gwaji

<u>Aikin ƙaramin rukuni: Tarawa da layin lamba (minti 10)</u>

- A umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunoni: A zaɓi jagora daga cikin kowane rukuni da zai taimaka wajen rarraba littafin ɗalibai da kuma abubuwan ƙirge 20 ga rukuninsu. A nemi ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai inda aka kawo layin lamba.
- **Ka/ki ce:** *Abubakar ya samu alewa 18? Ya sha 4 daga cikinsu. Alewa nawa ya rage masa?*
- A sa ɗalibai su yi amfani da abubuwan ƙirge da layin lamba wajen gwajin wannan labarin.
- A zagaya ana lura da ɗaliban lokacin da ake maimaita labarin. A yayin zagayawar, a tambaye su yadda suka samar da amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.
- Idan akwai lokaci, a sake maimaitawa da wani labarin. A tabbata ɗalibai sun jujjuyawa amfani da abubuwan ƙirgen.

## Bayyanawa

<u>Gwajin aikin gida (minti 10)</u>

- A buɗe littafin ɗalibai shafi na 12 sannan a karanta umurnin da ke ciki.
- A yi aiki na farko tare da ɗalibai a aji. Ɗalibai su juyi aikin a cikin littafin rubutunsu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 12 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

| Na. 15 | Zango na 1, Mako na 3, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi bita da gwajin abun da suka koya a cikin wannan makon.

**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)

- Rera waƙar tare da ɗalibai.

| | |
|---|---|
| Oyoyo oyoyo<br>Oyoyo Baba ya dawo<br>Ya dawo daga kasuwa<br>Ya sawo muna goriba<br>Ni an bani guda huɗu | Na ci ɗaya saura uku<br>In ya ci ɗaya saura biyu<br>In ta ci ɗaya saura ɗaya<br>In ka ci ɗaya ba ko ɗaya |

**Koyo**

Bita da maimai (minti 10)

- A zaɓi wani darasi daga cikin darrusan da aka yi a cikin makon, wanda ake ganin ɗalibai ba su fahimce shi sosai ba. A sake koyar da darasin ko a sake koyar da shi ta wata sabuwar hanya ta daban.

**Gwaji**

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai a cikin rukunoni : Zane da kuma rubutu (minti 10)

- A baiwa ɗalibai aikin da zai taimaka musu wajen yin gwajin darasin da aka yi bita (alal misali; ɗebewa daga lamba 1-20 ta amfani da gidan dara goma ko layin lamba. Ɗalibai suna iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma a cikin ƙananan rukunoni.
- Yayin da ɗalibai suke gudanar da wani aikin da aka ba su, a ƙara taimaka musu a inda ba su gane sosai ba.

**Bayyanawa**

Gwajin aikin gida (minti 10)

- A buɗe littafin ɗalibai shafi na 13 sannan a karanta umurnin da ke ciki.
- A yi aiki na farko tare da ɗalibai a aji. Ɗalibai su juyi aikin a cikin littafin rubutunsu.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 13 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

Na. 16

# Zango na 1, Mako na 4, Darasi na A

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya tarawa da rarrabewa tsakanin lambobi cika da mara.
**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge (ƙwayar wake ko tsakuwoyi) **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Kirge (minti 5)

- A yi wa ɗalibai bayanin cewa za a faɗi wata lamba. Da zarar an faɗi lambar, sai su fara ƙirge daga lambar da bibbiyu da sauri. Alal misali, idan aka ce "62," ɗalibai sai su fara faɗin "64, 66 68, 70..."
- Bayan 'yan daƙiƙu kaɗan, sai a ce "su tsaya." Daga nan sai a sake maimaita wannan tsarin da wata sabuwar lamba.

## Koyo

Gabatar da lambobi cika da mara (minti 8)

- **Ka/ki ce:***A yau za mu koyi lambobi cika da mara.*
- Malami ya zagaya a cikin aji ya ƙirga yawan ɗaliban ajin a bayyane tare da ɗaliban.
- Bayan an gama ƙirgen rubuta yawan ɗaliban a kan allo. Nemi ɗalibai su faɗi lambar a bayyane.
- Daga nan, sai a nemi ɗalibai su zauna bibbiyu. Su samu wani ɗalibi ɗaya, su tsaya tare a cikin ajin.
- **Ka/ki ce:***Idan ɗalibai suka zauna bibbiyu, wannan yana nuna lambar cika ce. Idan aka bar ƙarin ɗaya, yana nuna lambar mara ce.*
- A nemi ɗalibai su faɗi lambar da aka rubuta kan allo cika ce ko mara.

## Gwaji

Aikin ƙaramin rukuni: Rarrabewa tsakanin lambobi cika da mara (minti 15)

- A umurci ɗalibai su zauna a cikin ƙananan rukunonni: A zaɓi jagora daga cikin kowane rukuni da zai taimaka wajen rarraba abubuwan ƙirge 20 ga rukuninsu.
- **Ka/ki ce:***Ɗalibi ɗayaa cikin rukuninku ya ɗauki abubuwan ƙirge 15 ya aje su a tsakiyar rukuninku. Sannan sai wani ɗalibin ya rarraba abubuwan ƙirgen rukuni bibbiyu.*
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai a kuma tabbata duk ɗaliban suna rarraba abubuwan ƙirgen a rukunin bibbiyu.
- **Ka/ki ce:***Shin duk abubuwan ƙirgen suna da'yan uwa? Ko wannan yana nuna cewa 15 lamba ce cika ko mara?*
- A sake maimaitawa da wasu lambobi har zuwa 20.

## Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala ga wanda suke zaune tare wanda zai bayyana ko lambar da suka rubuta cika ce ko mara.

## Aikin Gida

A nemi ɗalibai su tattauna abun da suka sani game da lambobi cika da mara da wani daga cikin 'yan uwansu ko kuma abokansu.

| Na. 17 | Zango na 1, Mako na 4, Darasi na B |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya gane lambobi cika da mara daga 1 zuwa 20.
**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge (ƙwayar wake ko tsakuwoyi) **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Tattaunawar aji (minti 3)

- A nemi ɗalibi 1 ko 2 su yi wa aji bayanin bambancin da ake samu tsakanin lambobi cika da mara. (Alal misali; lambobi cika koyaushe suna iya ba da damar samun 'yan uwada za a haɗa su ba tare da rage komai ba).

**Koyo**

Gane lambobi cika daga 1 zuwa lamba 20 (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu iya gane dukkan lambobi cika da ake samu tsakanin 1 zuwa 20.*
- A kira ɗalibai goma su zo gaban aji. A ƙirga yawan ɗaliban dake gaban ajin tare da sauran 'yan ajin a bayyane.
- Nemi ɗaliban dake gaban ajin su nemi abokan haɗi su zama su bibbiyu.
- **Ka/ki ce:** *Idan aka samar da abokin haɗi ga kowane ɗalibi, wannan yana nuna lambar cika ce. Idan aka bar ragowar ɗaya kuwa, yana nuna lambar mara ce. Shin dukkan ɗaliban nan suna da abokan haɗi? Shin lamba 10 cika ce ko mara?*
- A sake maimaitawa da adadin wasu ɗalibai daban.

**Gwaji**

Aikin aji gaba ɗaya da kuma aikin ƙananan rukunoni: Gane lambobi cika (minti 15)

- A umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunoni: A zaɓi jagora daga cikin kowane rukuni da zai taimaka wajen rarraba abubuwan ƙirge 20 ga rukuninsu.
- **Ka/ki ce:** *Ɗalibi guda a cikin rukuninku ya aje abun ƙirge 1 a tsakiyar rukunin.*
- A zagaya ana lura da yadda ɗalibai suke aiki da abubuwan ƙirgen. Da zarar kowane rukuni ya aje abun ƙirge guda a tsakiyansa, nemi aji su faɗi a bayyane cewa shin lamba 1 mara ce ko cika.
- A cigaba da cewa ɗalibai su ƙara abubuwan ƙirgen ɗaya a tsakiyar rukuninsu. Yayin da ɗalibai suke gane lambobi cika tsakanin lamba 1 zuwa 20, a rubuta waɗannan lambobin a kan allo.
- Nemi ɗalibai su faɗi abun da suka lura da shi game da lambobi cika (alal misali; suna ƙarewa da 0 ko 2 ko 6 ko kuma 8).
- A sake maimaitawa da wasu lambobi har zuwa 20.

**Bayyanawa**

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A rubuta wata lamba daga 1 zuwa 20 a kan allo.
- Nemi ɗalibai su faɗi lambar cika ce ko mara.
- Nemi ɗalibai su ɗaga hannunsu sama idan sun san amsar tambayar.
- Idan akwai lokaci, a maimaita da wasu lambobi daban.

**Aikin Gida**

A nemi ɗalibai su rubuta dukkan lambobi cika daga 1-20 a cikin littafin rubutunsu.

| Na. 18 | Zango na 1, Mako na 4, Darasi na C |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya gane lamba mara daga 1 zuwa 20.
**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge (ƙwayar wake ko tsakuwoyi) **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Tattaunawa aji (minti 3)

- A nemi ɗalibi 1 ko 2 su yi wa aji bayanin bambancin da ake samu tsakanin lambobi cika da mara. (Alal misali; lambobi cika koyaushe suna iya ba da damar samun 'yan uwada za a haɗa su ba tare da rage komai ba).

**Koyo**

Gane lambobi cika daga 1 zuwa lamba 20 (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu iya gane dukkan lambobi mara tsakanin 1 zuwa 20.*
- A kira ɗalibai 11 su zo gaban aji. A ƙirga yawan ɗaliban dake gaban ajin tare da sauran 'yan ajin a bayyane.
- Nemi ɗaliban dake gaban ajin su nemi abokan haɗi su zama bibbiyu.
- **Ka/ki ce:** *Idan aka samar da abokin haɗi ga kowane ɗalibi, wannan yana nuna lambar cika ce. Idan aka bar ɗaya kuwa, yana nuna lambar mara ce. Shin dukkan ɗaliban nan suna da abokan haɗi? Shin lamba 15 cika ce ko mara?*
- A sake maimaitawa da adadin wasu ɗalibai daban.

**Gwaji**

Aikin aji gaba ɗaya da kuma aikin ƙananan rukunoni: Gane lambobi mara (minti 15)

- A umurci ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunoni: A zaɓi jagora daga cikin kowane rukuni da zai taimaka wajen rarraba abubuwan ƙirge 20 ga rukunisu.
- **Ka/ki ce:** *Ɗalibi ɗayaa cikin rukuniku ya aje abun ƙirge 1 a tsakiyar rukunin.*
- A zagaya ana lura da yadda ɗalibai suke aiki da abubuwan ƙirgen. Da zarar kowane rukuni ya aje abun ƙirge guda a tsakiyarsa, nemi aji su faɗi a bayyane cewa shin lamba 1 mara ce ko cika.
- **Ka/ki ce:** *Lamba 1 mara ce saboda ba ta da abokin haɗi. Daga nan sai a samu wani ɗalibi ya ƙara wani abun ƙirge guda a tsakiyar rukunin, sai ya zama an samu jimillar abubuwan ƙirge biyu.*
- A cigaba da cewa ɗalibai su ƙara abubuwan ƙirgen a tsakiyar rukuninsu, ɗaya a kowane lokaci. Yayin da ɗalibai suke gane lambobin da suke mara tsakanin lamba 1 zuwa 20, a rubuta waɗannan lambobin a kan allo.
- Nemi ɗalibai su faɗi abin da suka lura da shi game da lambobi mara (alal misali; suna ƙarewa da 1 ko 3 ko 5 ko kuma 9).

**Bayyanawa**

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A rubuta wata lamba daga 1 zuwa 20 a kan allo.
- Nemi ɗalibai su faɗi lambar cika ce ko mara.
- Nemi ɗalibai su ɗaga hannunsu sama idan sun san amsar tambayar.
- Idan akwai lokaci, a maimaita da wasu lambobi daban.

**Aikin Gida**

A nemi ɗalibai su rubuta dukkan lambobi mara daga 1-20 a cikin littafansu na rubutu.

| Na. 19 | Zango na 1, Mako na 4, Darasi na D |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya gane lambobi mara da ciki a cikin jerin lambobi.
**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge (ƙwayar wake ko tsakuwoyi) **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Kirge (minti 5)

- A yi wa ɗalibai bayanin cewa za a faɗi wata lamba. Da zarar an faɗi lambar, sai su fara ƙirge daga lambar da biyar-biyar da sauri. Alal misali, idan aka ce "10," ɗalibai sai su fara faɗin "15, 20, 25, 30..."
- Bayan 'yan daƙiƙai kaɗan, sai a ce "su tsaya." Daga nan sai a sake maimaita wannan tsarin da jerin wasu lambobi.

**Koyo**

Gane lambobi cika da mara a cikin jerin lambobi (minti 8)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu cigaba da gwajin yadda ake gane lambobi cika da mara.*
- A rubuta lambobin 41, 42, 43, 44, da kuma 45 a kan allo.
- A nemi ɗalibai su karanta lambobin a bayyane.
- Nemi ɗalibai biyar su zo gaban aji su tsaya a gaban kowace lamba.
- Nemi ɗalibai su yi bayanin a gaban lamba cika ko mara ce suka tsaya. Idan ba su tabbas, sauran ɗaliban ajin suna iya faɗin amsar da ƙarfi.
- Nemi ɗalibai su faɗi yadda aka yi suka san lambar cika ce ko mara.
- A sake maimaitawa da jerin wasu lambobi daban da kuma wasu ɗalibai daban.

**Gwaji**

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da kuma ɗalibai bibbiyu: Gane lambobi cika da mara (minti 15)

- A nemi ɗalibi 1 ko 2 ya taimaka wajen rarraba littafin ɗalibai ga kowane ɗalibi. A ce ɗalibai su buɗe littafin a Shafi na 14.
- A karanta umurnin da kuma tambaya ta farko a bayyane ga ɗalibai.
- **Ka/ki ce:** *Tambaya ta farko ta nemi ku gano lambobi cika a jerin waɗannan lambobin.*
- A nemi ɗalibai su warware wannan lissafin a cikin littafansu na rubutu ta hanyar rubuta dukkan lambobi cika a bisa layin. Suna iya gwada amsoshinsu da na abokin zamansu.
- A zagaya ana lura da ɗalibai. Yayin zagayawar, a tambaye su yadda suka samar da amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.
- Idan akwai lokaci, a kammala aikin lissafin na gaba dake a kan shafin.

**Bayyanawa**

Auna fahimta nan-take (minti 3)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu sama su nuna abun da suka rubuta. A yabawa ƙwazon ɗalibai.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 14 a cikin littafin rubutu a matsayin aikin gida.

Na. 20

# Zango na 1, Mako na 4, Darasi na E

**Manufa:** Ɗalibai za su yi bita da gwajin abun da suka koya a cikin wannan makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Kirge (minti 5)

- A yi wa ɗalibai bayanin cewa za a faɗi wata lamba. Da zarar an faɗi lambar, sai su fara ƙirge daga lambar da goma-goma da sauri. Alal misali, idan aka ce "20," ɗalibai sai su fara faɗin "30, 40, 50, 60, 70, 80..."
- Bayan 'yan daƙiƙai kaɗan, sai a ce "su tsaya." Daga nan sai a sake maimaita wannan tsarin da wata sabuwar lamba.

## Koyo

Bita da maimai (minti 8)

- A zaɓi wani darasi daga cikin darrusan da aka yi a cikin makon, wanda ake ganin ɗalibai ba su fahimce shi sosai ba. A sake koyar da darasin ko a sake koyar da shi ta wata sabuwar hanya daban.

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai a cikin rukuni : Zane da kuma rubutu (minti 15)

- A baiwa ɗalibai aikin da zai taimaka masu wajen yin gwajin darasin da aka yi bita (alal misali; rarrabewa tsakanin lambobi cika da mara. Ɗalibai suna iya yin aiki ɗaiɗaikunsu ko kuma a cikin ƙananan rukunoni.
- Yayin da ɗalibai suke gudanar da wani aikin da aka ba su, a ƙara taimaka musu a inda ba su gane sosai ba.

## Bayyanawa

Bita da kuma bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala a lokacin Gwaji.

## Aikin Gida

A ba ɗalibai aikin da za su yi bita a gida, su kuma yi gwajin ƙwazonsu.

| Na. 21 | Zango na 1, Mako na 5, Darasi na A |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya kawo sunayen ranakun mako da kuma ayyukan da ake yi a cikin ranakun.

**Kayan Aiki:**

**Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai sau da yawa.
- A nemi ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta zo gaban aji ya/ta rera waƙar.

> Yara, yara 'yan makaranta
> A mako muna da kwanaki guda bakwai.
> Lahadi muke shiri mu tsaftace tufa.
> Litinin mu garzaya mu je makaranta.
> Talata da Laraba mu je makaranta.
> Alhamis da Juma'a mu je makaranta.
> Asabar mu shakata mu je mu yi hutu.
> Mu wataya mu rausaya mu je muyi wasa.

## Koyo

Gabatar da ranakun mako (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi wani abu a kan ranakun mako. Ranakun mako su ne: Lahadi da Litinin da Talata da Laraba da Alhamis da Juma'a da kuma Asabar.*
- A rubuta kowace daga cikin ranakun makon a kan allo. A nuna kowace daga cikin ranakun da aka rubuta sannan a nemi ɗaliban ajin su karanta ta a bayyane.
- **Ka/ki ce:** *Ranakun mako guda nawa ne?*
- A nemi ɗalibai su yi bayanin ayyukan da suke yi a cikin ranakun mako daban-daban. (Alal misali; a ranar Juma'a suna tafiya masallaci; Ranar litinin zuwa Juma'a suna zuwa makaranta).

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da kuma aiki cikin ƙananan rukunoni: Ranakun mako (minti 15)

- A nemi ɗalibai su fito da littafansu na rubutu. Kowannensu ya zaɓi rana ɗayata mako sai ya zana hoton wani abu da suke yi a wannan ranar.
- A zagaya ana lura da ɗalibai lokacin da suke zana hotunan.. Yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai wane aiki ne suke zana hotonsa a kuma taimaka masu idan akwai bukatar hakan.
- Bayan minti 10, a nemi dukkan ɗaliban da suka zana hoton ranar litinin su tsaya a cikin rukuni ɗaya, dukkan ɗaliban da suka zana hoton ranar Talata su tsaya a cikin rukuni ɗaya, da sauransu, saboda haka za a samu rukunin ɗalibai na kowace rana ta mako.
- A nemi rukunin ɗaliban su tsaya a cikin tsari daga lahadi har zuwa Asabar.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A nemi ɗalibai su ɗaga hannunsu sama idan sun zana hoton rana ta farkon mako (Lahadi). Idan ɗalibai sun ɗaga hannuwansu sama, nemi ɗaya daga cikin su ya faɗi wace ranar mako ce.
- A maimaita da wasu ranakun mako (biyu, uku, huɗu, da sauransu.)

## Aikin Gida

A nemi ɗalibai su zana wani aiki da suke yi a kowace rana a cikin littafansu na rubutu.

| Na. 22 | Zango na 1, Mako na 5, Darasi na B |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane lokacin safe a.m. da kuma lokacin yamma p.m da kuma ayyukan da ake yi a lokacin safe na a.m da kuma lokacin yamma na p.m.
**Kayan Aiki:** Takarda mai ɗauke da lokutan rana (safiya da rana da yamma da kuma dare) **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)


- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Labari da gwaji (minti 5)

- A bayar da labarin. Nasir ya tashi da safe ya sanya tufafinsa. Ya tafi makaranta. Da rana, ya ci abincin rana. Da yamma, ya tafi gida don ya yi wasa da abokansa ya kuma ci abinci da dare. Ya yi bacci cikin dare.
- A nemi wani ɗalibi ya zo gaban aji ya yi gwajin yadda labarin yake.

**Koyo**

Gabatar da lokaci (minti 8)



- **Ka/ki ce:***Yau za mu koyi wani abu game da lokaci. A cikin wannan labarin Nasir ya kammala ayyuka da yawa a cikin lokuta daban-daban na rana ɗaya: safe da rana da yamma da kuma dare. Wasu lokuta muna kiran lokacin safe da a.m. da kuma lokacin rana da yamma da dare mu kira su p.m.*
- A nuna kowane daga cikin hotunan da ke kan allo sai a nemi ɗalibai su maimaita abin da aka karanta yayin da ake faɗin lokutan da kowane hoto daga cikinsu yake nunawa.
- Tambayi ɗalibai su faɗi wane lokaci ne Nasir ya gudanar da ayyukansa daban-daban na wuni. Tambayi ɗalibai su faɗi ayyukan da suke yi a lokacin safe a.m. da kuma lokacin yamma p.m.

**Gwaji**

Wasan aji gaba ɗaya: Wane lokacin wuni ne? (minti 15)

- Rubuta "safe," "rana," "yamma" da kuma "dare" a kan ƙananan takardu daban-daban sai a aje su a lunguna huɗu dake cikin ajin.
- A yi bayanin cewa za a faɗi wani aiki sai dukkan ɗaliban su koma lungun ajin da aka sanya lokacin da wannan aikin ke faruwa a wuni. Alal misali; idan ka ce, "a tafi makaranta" ɗalibai za su koma lungun ajin wanda ke da kalmar "safe."
- A tunawa ɗalibai cewa ana iya samun amsa fiye da ɗaya ga kowane daga cikin ayyukan (alal misali; kuna iya cin abinci da safe da rana da kuma yamma)
- **Ka/ki ce:** *Cin abinci; bacci; zuwa makaranta; dawowa daga makaranta; wasa da abokai; sallah; tashi bacci; wanki; yin aikin gida na makaranta.* Bayan kowane aiki, a jira ɗalibai su tafi lungun da ya dace, a jira ɗalibai su gane lungun da ya dace su tafi.
- Tambayi ɗaya daga cikin ɗaliban ya faɗi shin suna tsaye ne a lokacin safe na a.m ko a lokacin yamma na p.m.

**Bayyanawa**

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A kira wani lokaci cikin wuni sai a tambayi ɗalibai su faɗi wani aiki da sukeyi a kowace rana a wannan lokacin. Tambayi ɗaliban su faɗi wane lokaci ne, shin na safe ne (a.m.) ko na yamma ne (p.m.)

**Aikin Gida**


A umurci dukkan ɗaliban su zana hoton wasu ayyuka da sukeyi a lokacin safe (a.m.) da kuma lokacin yamma (p.m.) a cikin littafansu na rubutu.

| Na. 23 | Zango na 1, Mako na 5, Darasi na C |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane ɓangaroron fuskar agogo su kuma faɗi lokacin da ya rage ga awa.
**Kayan Aiki:** **Tsawon Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)



- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Labari da kuma Hotuna (minti 5)

- A bayyana wannan labari da yake ƙasa.
- Fatima ta tashi bacci da ƙarfe 7:00 na safe ta sanya tufafinta. Ta tafi makaranta da ƙarfe 8:00a.m. na safe. Da rana, ƙarfe 1:00 p.m. ta ci abincin rana. Da yamma, ta tafi gida ta yi wasa da abokanta da ƙarfe 4:00 p.m.na yamma ta kuma ci abincin dare da ƙarfe 6:00 p.m. na yamma. Ta yi bacci da ƙarfe 8:00 p.m. na dare.
- A nemi wani ɗalibi ya zo gaban aji ya yi gwajin wannan labarin.

## Koyo

Gabatar da awoyi (minti 15)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi darasi a kan agogo da kuma faɗin lokaci. Muna amfani da lambobin da suke kan agogo ne domin mu faɗi wani lokaci. Agogo yana da hannuwa guda biyu. Babban hannu wanda koyaushe yake nuna mintoci. Da gajeren hannu wanda koyaushe yake nuna awa.*
- A nuna agogon da yake kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Agogon yana da lambobi 1-12 da ke wakiltar awoyi daban-daban a rana. Akwai awoyi 24 a kowace rana. Gajeren hannun awa shi ke zagaya dukkan agogon sau biyu a rana, sau ɗaya da safe a.m. da kuma sau ɗaya da yamma, p.m.*
- A yi wa ɗalibai bayanin wane lokaci ne a ke ciki yanzu da gwajin yadda ake zana hoton gajeren hannun awa tare da nuna lambar dake a kan agogon.
- A sake karanta labarin Fatima. A dukkan lokacin da aka faɗi, a nemi wani ɗalibi guda ya zo gaban aji ya zana gajeren hannun awa a kan agogon don ya nuna lokacin da yake daidai.
- A tabbata an shafe gajeren hannun awa bayan kowane ɗalibi ya gama aikinsa, ta yadda wani ɗalibi da zai biyo bayansa yana iya zuwa ya zana nasa hoton gajeren hannun awar bayansa.

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai: Gajeren hannun awa na agogo (minti 10)

- A nemi ɗaliban su buɗe Shafi na 15 a cikin littafansu na rubutu.
- A karanta umurnin da aka rubuta ga ɗaliban a kuma warware aikin na farko tare da su.
- Idan akwai lokaci, a cigaba da warware sauran ayyukan.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 3)

- A sa ɗalibai su ɗaga abin da suka zana sama a kuma tabbatar idan sun yi daidai.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 15 a cikin littafin rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 24 | Zango na 1, Mako na 5, Darasi na D |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya faɗin lokaci da ya rage ga rabin awa.
**Kayan Aiki:** Samfurin agogon gwaji da aka yi **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Kirge (minti 3)

- A yi wa ɗalibai bayanin cewa za a faɗi wata lamba. Da zarar an faɗi lambar, sai su fara ƙirge daga lambar da biyar-biyar da sauri. Alal misali, idan aka ce “25,” ɗalibai sai su fara faɗin “30, 35, 40, 45...”.
- Bayan ‘yan daƙiƙai kaɗan, sai a ce “su tsaya.” Daga nan sai a sake maimaita wannan tsarin da wata sabuwar lamba.

## Koyo

Gabatar da rabin awa (minti 15)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu faɗi lokacin da ya rage ga rabin awa ta hanyar amfani da agogo.*
- A tambayi ɗalibai su faɗi wane daga cikin hannayyen agogon ne hannun awa sannan kuma wane ne hannun dake nuna minti.
- **Ka/ki ce:** *Agogon yana da lambobi 1-12 dake nuna awoyi a kowace rana. Hannun awa yana zagayar agogon sau biyu a rana. Hannun dake nuna minti kuwa yana zagayar agogon sau ɗaya a cikin kowace awa, ko kuma sau 24 a kowace rana. Akwai mintuna 60 a cikin kowace awa, saboda haka muna iya yin ƙirge da biyar-biyar domin mu faɗi mintuna.*
- A nuna kowace daga cikin lambobin dake a kan agogon, sannan sai a yi ƙirgen tare da ɗalibai da biyar-biyar domin a nuna mintunan.
- **Ka/ki ce:** *Idan hannun minti ya kai kusan tsakiyar agogon, za mu ce, “da rabin” awa.*
- A zana hoton lokaci 1:30 a kan agogo.
- **Ka/ki ce:** *Wannan lokacin 1:30 ko ɗaya da rabi kenan.*
- A zana hoton lokacin 3:30 a kan allo. A nemi ɗalibai su ɗaga hannunsu sama don su faɗi lokacin da aka nuna.
- Idan akwai lokaci, a nunawa ɗalibai ƙarin wasu misalai.

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai: Awa da rabin awa (minti 10)

- A nemi ɗalibi 1-2 su taimaka wajen rarraba littafan ɗalibai ga ajin. A nemi ɗaliban su buɗe agogon da bai da komai a cikinsa dake gaban littafin nasu su kuma ɗauko fensira ko tsinke guda biyu.
- **Ka/ki ce:** *A ɗauka cewa fensir ɗaya shi ne hannun awa, sannan ɗayan kuma shi ne hannun dake nuna minti a kan agogon. Idana na faɗi wani lokaci a bayyane, ku yi amfani da fensiran guda biyu wajen nuna daidai lokacin.*
- A faɗi lokutan a bayyane: 3:30, 1:30, 8:30 da kuma 2:00.
- Bayan an faɗi kowane lokaci, a zagaya don a lura da ɗaliban a kuma taimaka musu.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A nuna lokaci ƙarfe 9:30 akan agogon gwaji ko a zana hotonsa a kan allo. Nemi ɗalibai su ɗaga hannunsu sama idan suna iya faɗin lokacin. A yaba wa ƙwazonsu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su zana agogo a cikin littafansu na rubutu dake nuna lokaci ƙarfe 5:30.

| Na. 25 | Zango na 1, Mako na 5, Darasi na E |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su yi bita da gwajin abin da suka koya a cikin wannan makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Kirge (minti 5)

- A yi wa ɗalibai bayanin cewa za a faɗi wata lamba. Da zarar an faɗi lambar, sai su fara ƙirge daga lambar da biyar-biyar da sauri. Alal misali, idan aka ce "65," ɗalibai sai su fara faɗin "75", 80, 85, 90...".
- Bayan 'yan daƙiƙai kaɗan, sai a ce "su tsaya." Daga nan sai a sake maimaita wannan tsarin da wata sabuwar lamba.

### Koyo

Bita da maimai (minti 8)

- A zaɓi wani darasi daga cikin darrusan da aka yi a cikin makon, wanda ake ganin ɗalibai ba su fahimce shi sosai ba. A sake koyar da darasin ko a sake koyar da shi ta wata sabuwar hanya daban.

### Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai a cikin rukuni : Zane da kuma rubutu (minti 15)

- A baiwa ɗalibai aikin da zai taimaka masu wajen yin gwajin darasin da aka yi bita (alal misali; faɗin lokacin da ya rage a awa ko kuma rabin awa). Ɗalibai suna iya yin aiki ɗaiɗaikunsu ko kuma a cikin ƙananan rukunoni.
- Yayin da ɗalibai suke gudanar da wani aikin da aka ba su, a ƙara taimaka musu a inda ba su gane sosai ba.

### Bayyanawa

Bita da kuma bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala a lokacin Gwaji.

### Aikn Gida

A ba ɗalibai aikin da za su yi bita a gida, su kuma yi gwajin ƙwazonsu.

| Na. 26 | Zango na 1, Mako na 6, Darasi na A |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su yi taƙaitacciyar jarrabawar gwaji ta lissafi.
**Kayan Aiki:**

### JARRABAWAR GWAJI

A yi wa ɗalibai jarrabawar gwaji ta kai-tsaye da kuma rubuta makin da suka samu a cikin littafinka/ki na ajiye bayanai. Idan akwai buƙata, a nemi taimakon Jagoran Malamai da SBMC ko kuma wasu malamai domin gudanar da jarrabawar.

A bayar da wani aikin gwaji ga ɗalibai yayin da suke jiran a fara jarrabawar gwajin. Ɗalibai suna iya yin aikin gwajin tarawa da ɗebewa cikin lambobi 1-20 ko kuma faɗin lokacin da ya rage ga cikar awa ko rabin awa.

| **Jaha:** | | **Karamar hukuma:** | | **Makaranta:** | | | **Wata:** | | **Shekara:** | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| Lamba | Sunan Ɗalibi | Jinsi | Shekaru | Buƙata ta musamman (Eh/A'a) | Kirgen tsallaken lambobi | Tarawa | Ɗebewa | Lokaci | Lambobi Mara | Jimillar maki |
| | | | | | /2 | /2 | /2 | /6 | /3 | / 15 |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | | |

**Darasin Lissafi Aji 2, Zango na 1, Mako na 6 – Jarrabawar tsakiyar Zango**

**Kidaya da goma-goma daga goma zuwa ɗari.** (A bayar da maki biyu idan an amsa daidai)


**Tara waɗannan lambobi a fitar da amsa.** (A bayar da maki biyu idan an amsa daidai)


**15 + 4 = ___**

**Ɗebe waɗannan lambobi a fitar da amsa.** (A bayar da maki biyu idan an amsa daidai)

**12 – 8 = ___**

**Faɗi lokaci da waɗannan agogunan suke nuwawa.** (A bayar da maki uku ga kowace amsa)




**Karanta lambobi mara da ke ƙasa.** (A bayar da maki ɗaya ga kowace amsa, har zuwa maki 3)

**42, 75, 81, 6, 9, 32, 66, 90, 100**

**Na. 27**

# Zango na 1, Mako na 6, Darasi na B

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi ƙirgen tsallaken lambobi biyu-biyu da biyar-biyar da kuma goma-goma zuwa 100 ta amfani da abubuwan ƙirge da kuma Jadawalin Lambobi 1-100.

**Kayan Aiki:** Jadawalin Lambobi 1-100 **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

<u>Duba aikin gida (minti 2)</u>

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masua gwiwa.

<u>Ni wace lamba ce? (minti 3)</u>

- A yi wasan Ni Wace Lamba Ce? A karanta kowane ɗaya daga cikin waɗannan jawaban a bayyane. Idan ɗalibai sun bayar da amsa daidai, a nuna lambar da suka faɗi a kan Jadawalin lambobi 1-100.
- **Ka/ki ce:** *Da 2 na fi 2.*
- **Ka/ki ce:** *Da 5 na fi 20.*
- **Ka/ki ce:** *Da 10 na fi 36.*

## Koyo

<u>Kirgen tsallaken lamba da biyu-biyu zuwa 100 (minti 10)</u>

- **Ka/ki ce:** *A yau zamu yi ƙirgen tsallaken lamba da biyu-biyu da biyar-biyar da kuma goma-goma zuwa 100.*
- A yi ƙirgen tsallaken biyu-biyu a fara da 0 har zuwa 100 yayin da ake nuna lambar da aka ƙirga a kan jadawalin lambobi 1-100. A nemi ɗalibai su karanta tare da malami.
- A maimaita ƙirgen tsallaken biyar-biyar da kuma goma-goma. A sa ɗalibai su yi ƙirgen tsallaken lambar da abokan zamansu.
- A tambayi ɗalibai su faɗi me ya fi sauƙi gare su kuma me ya fi wahala gare su.

| | | | | | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| 1 | 2 | 3 | 4 | 5 | 6 | 7 | 8 | 9 | 10 |
| 11 | 12 | 13 | 14 | 15 | 16 | 17 | 18 | 19 | 20 |
| 21 | 22 | 23 | 24 | 25 | 26 | 27 | 28 | 29 | 30 |
| 31 | 32 | 33 | 34 | 35 | 36 | 37 | 38 | 39 | 40 |
| 41 | 42 | 43 | 44 | 45 | 46 | 47 | 48 | 49 | 50 |
| 51 | 52 | 53 | 54 | 55 | 56 | 57 | 58 | 59 | 60 |
| 61 | 62 | 63 | 64 | 65 | 66 | 67 | 68 | 69 | 70 |
| 71 | 72 | 73 | 74 | 75 | 76 | 77 | 78 | 79 | 80 |
| 81 | 82 | 83 | 84 | 85 | 86 | 87 | 88 | 89 | 90 |
| 91 | 92 | 93 | 94 | 95 | 96 | 97 | 98 | 99 | 100 |

## Gwaji

<u>Wasan aji gaba ɗaya: Kirge zuwa 100 da biyu-biyu da biyar-biyar da kuma goma-goma (minti 15)</u>

- A sa ɗalibai su tsaya a cikin babbar da'ira. A ba da ƙwallo ko wata dunkulallar takarda da aka naɗe ga wani ɗalibi ɗaya dake cikin da'irar.
- A yi wa ɗaliban bayanin cewa za su yi ƙirge da biyu-biyu zuwa 100 ta amfani da jefa ƙwallon da kuma kama ta. Duk ɗalibin da ya kama ƙwallon to zai faɗi lambar dake kan tsari ta gaba (alal misali; idan ɗalibin farko ya ce 2, ɗalibi na gaba zai ce 4, da sauransu.)
- A zagaya ana lura da aikin ɗaliban yayin da suke jifa da kama ƙwallon, suna faɗin lambobin dake gaba bisa tsari har zuwa 100.
- A maimaita wasan, a wannan lokaci da ƙirgen tsallaken lamba biyar-biyar. Sannan sai a yi ƙirgen tsallaken lamba goma-goma.

## Bayyanawa

<u>Auna fahimta nan-take (minti 5)</u>

- Nuna wata lamba a cikin jadawalin 100.
- Umurci ɗalibai su ɗaga hannunsa sama idan sun san amsar sai a kira wani/wata ɗalibi/ɗaliba su faɗi amsar a bayyane.
- Umurci sauran ɗalibai su bayyana ra ayinsu ta hanyar ɗaga babban ɗan yatsansu ya ƙalli sama idan daidai ne ko kuma ya kalli ƙasa idan ba daidai bane. A yiwa ɗalibai gyara yadda ya dace.

## Aikin Gida

A umurci ɗalibai su yi gwajin ƙirgen tsallaken lamba da biyu-biyu da biyar-biyar da kuma goma-goma zuwa 100 a gida.

| No. 28 | Zango na 1, Mako na 6, Darasi na C |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za suyi bitar tarawa zuwa 20.
**Kayan Aiki:** Katin Lambobi 1-20 da alamar + da alamar = da kuma wake ko tsakuwoyi
**Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)

- Umurci ɗalibai su rera waƙar tare da kai/ke.

Waƙar Tarawa
Ana batun tarawa /
Komai a tara da ɗaya /
1+1= 2 / 2+1= 3 / 3+1= 4 /
4+1= 5 / 5+1= 6 / 6+1= 7 /
7+1= 8 / 8+1= 9 / 9+1= 10

### Koyo


Bita: Tarawa zuwa 20 (minti 10)

- **Ka/Ki ce:** A yau za muyi bitar tara lambobi da basu wuce 20 ba.
- Umurci ɗalibai bakwai su fito gaban allo. Tambayi sauran ʻyan aji ko ɗalibai nawa ne a gaban allo sai ka basu kati mai ɗauke da lamba 7.
- Kira ƙarin ɗalibai 12 zuwa gaban allo sai a basu rukunin kati mai ɗauke da lamba 12.
- Kirga duka ɗaliban da ke gaban allo tare da sauran ʻyan aji a bayyane.
- Kira ɗalibi/ɗaliba ya/ta zo gaban allo ya/ta sa alamar + da kuma alamar = don a yi fasalin lissafin.
- **Ka/Ki ce:** *Ɗalibai 7 da ɗalibai 12 sun zama ɗalibai 19 kenan, saboda haka 7 a tara da 12 = 19.*
- A maimaita da wasu adadin ɗalibai daban.

### Gwaji

Aikin ƙaramin rukuni: Amfani da katin lambobi wajen rubuta fasalin lissafi (minti 15)

- Umurci ɗaliba su zauna cikin ƙananan rukuni.
- Zabi shugaba a cikin kowane rukuni don yataimaka raba abubuwan ƙirge, katin lamba 2 da alamar + da alamar = ga kowane rukuni.
- Umurci rukunai su yi fasalin lissafi daidai da katin lambobinsu. Ɗalibai su yi amfani da abubuwan ƙirge da katin lambobi domin warware aikin lissafin.




- A zagaya ana lura da ɗalibai. Yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai yadda suka samo amsar su, a kuma duba ko sun amsa daidai.
- A umurci ɗalibai su sauya katin lambobinsu da wani rukunin, sai a yi wani sabon fasalin lissafi.

### Bayyanawa

Auna fahimta nan take (minti 5)

- Rubuta fasalin lissafi a kan allo (13 + 5 =).
- Umurci ɗalibai su warware fasalin lissafin, sai a kira wani ɗalibi/ɗaliba ya/ta faɗi amsar a bayyane.
- A nemi wasu ɗalibai su duba idan amsar daidai take ko ba daidai take ba ta hanyar ɗaga babban yatsansu ya kalli sama ko kuma ƙasa. A yi gyara idan akwai buƙatar hakan.

### Aikin Gida

Umurci ɗalibai su warware aikin lissafin 15 + 4 = ___ a cikin littafan rubutunsu.

| Na. 29 | Zango na 1, Mako na 6, Darasi na D |
|---|---|

# Zango na 1, Mako na 6, Darasi na D

**Manufa:** Ɗalibai za su yi bitar lissafin ɗebewa daga lamba 1-20.
**Kayan Aiki:** Katunan lamba 1-20 da katunan alamar – da alamar = da abubuwan ƙirge da kwalabe
**Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.


Waƙa (minti 2)

- Rera waƙar tare da ɗalibai.

| | |
|---|---|
| Oyoyo oyoyo<br>Oyoyo Baba ya dawo<br>Ya dawo daga kasuwa<br>Ya sawo muna goriba<br>Ni an bani guda huɗu | Naci daya saura uku<br>In ya ci ɗaya saura biyu<br>In ta ci ɗaya saura ɗaya<br>In ka ci ɗaya ba ko ɗaya |

## Koyo

Bita: Ɗebewa tsakanin lamba 1-20 (minti 10)




15 - 3 = 12

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu yi bitar yadda ake ɗebewa cikin lambobi 1 zuwa ashirin.*
- A jera robobi goma sha biyar. A nemi ɗaliban aji su faɗi robobi nawa ne aka aje a tsaye.
- A kiran wani ɗalibi ya zo gaban aji sannan sai a nemi ya jefa ƙwallo do dunkulallar takarda ga robobin da aka jera. A ƙirga guda nawa suka faɗi ƙasa.
- A nemi wani ɗalibi ya rubuta fasalin daidaiton a kan allo. Alal misali, idan akwai robobi goma sha biyar a tsaye, sai ɗalibin ya buge guda uku suka faɗi ƙasa, za su rubuta 15 -3 =12 a kan allo.
- A maimaita da adadin wasu robobin daban guda ashirin da ɗalibai daban-daban.

## Gwaji

Aiki cikin ƙaramin rukuni: Amfani da katunan lamba a rubuta fasalin daidaito (minti 15)




- A nemi ɗalibai su zauna a cikin ƙananan rukunoni.
- A zaɓi jagora daga kowane rukuni da zai taimaka wajen raba abubuwan ƙirge da katunan lamba 2 da katin alamar ɗebewa da alamar sa amsa ga kowane rukuni.
- Umurci rukunoni su tsara fasalin lissafin wanda ya yi daidai da katunan lambobinsu. Ɗalibai su yi amfani da abubuwan ƙirge da katunan lamba domin su warware fasalin lissafin daidai.
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai yayin da ake kiran lambobin. A yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai yadda suka samo amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.
- A nemi ɗalibai su musaya ɗaya daga cikin katunan lambarsu da wani rukuni , sannan sai su tsara wani fasalin lissafin.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan take (minti 5)

- A rubuta wani fasalin lissafi a kan allo (misali; 19 - 5 = 14).
- Umurci ɗalibai su warware wannan lissafin, su kuma ɗaga hunnunsu idan sun san amsar da take daidai.

## Aikin Gida

A umurci ɗalibai su warware lissafin 17 - 6 = ____ a cikin littafansu na rubutu.

| Na. 30 | Zango na 1, Mako na 6, Darasi na E |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su gane lambobi cika da mara.
**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge (ƙwayar wake ko tsakuwoyi) **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Ni wace lamba ce? (minti 3)

- A yi wasan Ni Wace Lamba Ce? A karanta kowane ɗaya daga cikin waɗannan jawaban a bayyane. Idan ɗalibai sun bayar da amsa daidai, a nuna lambar da suka faɗi a kan Jadawalin lambobi 1-100.
- **Ka/ki ce:** *Da 2 na fi 62.*
- **Ka/ki ce:** *Da 5 na fi 35.*

**Koyo**

Gane lambobi cika da mara (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu yi darasi akan yadda ake gane lambobi cika da mara.*
- A zagaya a cikin aji, a ƙirga yawan ɗaliban dake cikin ajin gaba ɗaya a bayyane.
- A rubuta lambobin 41, 42, 43, 44, da kuma 45 a kan allo.
- Bayan an gama ƙirga dukkan ɗaliban, a rubuta jimillar yawansu a kan allo. A nemi ɗalibai su faɗi lambar a bayyane.
- Daga nan, sai a nemi kowane ɗalibi ya samu abokin haɗi, su zama bibbiyu. Su kuma samu wani ɗalibi guda su tsaya kusa da shi., Idan aka samu ɗalibin da bai samu abokin haɗi ba, ya zo ya tsaya a gaban aji.
- **Ka/ki ce:** *Ku tuna, idan a ka samu abokin haɗi ga kowane ɗalibi, to wannan lamba ce cika. Idan aka samu ragowar ɗaya kuwa, to a nan lambar mara ce.*
- Umurci ɗalibai su faɗi shin lambar da ke rubuce a kan allo cika ce ko mara.

**Gwaji**

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: Gane lambobi mara da cika (minti 15)

- A nemi ɗalibai 1-2 da za su taimaka wajen rarraba littafan ɗalibaiga kowane ɗalibi. A nemi ɗalibai su buɗe littafan rubutunsu Shafi na 16.
- A karanta umurni da aka rubuta da tambayar farko a bayyane ga ɗalibai.
- **Ka/ki ce:** *Waɗanne lambobi ne cika a cikin jerin lambobin da aka rubuta a layin farko. Ta yaya kuka san haka?*
- A umurci ɗalibai su warware lissafin a cikin littafansu na rubutu ta hanyar rubuta lambobi cika a bisa layin. Suna iya nunawa abokan zamansu amsar da suka rubuta.
- A zagaya ana lura da ɗalibai. Yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai yadda suka samo amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.
- Idan akwai lokaci, a kammala lissafi na gaba dake a kan shafin.

**Bayyanawa**

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu sama, su nuna abun da suka rubuta. A yaba wa ƙwazonsu.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 16 a cikin littafan rubutunsu a matsayin aikin gida.

**Na. 31**

# Zango na 1, Mako na 7, Darasi na A

**Manufa:** Ɗalibai za su iya ƙirgen ɗaiɗai da ƙirgen goma-goma har zuwa 200.
**Kayan Aiki:** Jadawalin lambobi 1-200 da aka rubuta a kan allo **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Bayyanawa da Raɗa: Kirge daga 1 zuwa 100 da ɗaiɗai (minti 3)

- A yi ƙirge daga 1 zuwa 100 a kan jadawalin lambobin, tare da nuna kowace lamba a lokacin da ake faɗinta. A umurci ɗalibai su yi ƙirgen tare da malami, ana sassauyawa tsakanin bayyanawa da kuma raɗa (alal misali: daga 1 zuwa 9 dukkan ɗalibai za su karanta lambobin a bayyane. Daga 10 zuwa 19, dukkan ɗalibai za su yi karatun cikin raɗa. A cigaba da yin haka har zuwa 100.

## Koyo

Wasan Bayyanawa ihu da Raɗa: Kirge daga 100 zuwa 200 da bibbiyu (minti 5)

- **Ka/ki ce:**_A yau za mu yi koyi yadda ake ƙirge zuwa 200._
- A yi ƙirge daga 100 zuwa 200 a kan jadawalin lambobi, tare da nuna kowace lamba a lokacin da ake faɗinta. A nemi ɗalibai su yi ƙirgen tare da malami, ana sassauyawa tsakanin bayyanawa da kuma raɗa.
- A sake maimaitawa sau ɗaya, ta yadda ɗalibai za su saba da ƙirgen ɗaiɗai daga 100 zuwa 200.

Kirgen Tsallake da goma-goma zuwa 200 (minti 5)

- **Ka/ki ce:** _Ana ɗaukar lokaci mai tsawo wajen yin ƙirge da ɗaiɗai. Bari mu yi gwajin yin ƙirge da goma-goma._
- A yi ƙirgen tsallake daga 0 zuwa 200 da goma-goma, ana nunawa daga jadawalin lambobin dake kan allo. Nemi ɗalibai da su yi ƙirgen tare da malami. A tambayi ɗalibai ko sun lura da wani tsari.
- **Ka/ki ce:** _Idan muka yi ƙirgen tsallake da goma-goma, kowace lamba za ta ƙare da wata lambar irinta. Idan mun fara daga 0, kowace lamba za ta ƙare da 0. Idan mun fara da 1, kowace lamba za ta ƙare da 1._
- A yi ƙirgen tsallake daga 1 zuwa 201 da goma-goma, ana nunawa daga jadawalin lambobi. A nemi ɗalibai su yi ƙirgen suma.

## Gwaji

Wasan aji gaba ɗaya: Kirge zuwa 200 da ɗaiɗai da kuma goma-goma (minti 15)

- A sa ɗalibai su tsaya a cikin babbar da'ira. A ba da ƙwallo ko dunkulallar takarda da aka naɗe ga wani ɗalibi ɗaya dake cikin da'irar.
- A yi wa ɗaliban bayanin cewa za su yi ƙirge da ɗaiɗai zuwa 200 ta amfani da jefa ƙwallon da kuma kama ta. Duk ɗalibin da ya kama ƙwallon to zai faɗi lambar dake kan tsari ta gaba (alal misali; idan ɗalibin farko ya ce 1, ɗalibi na gaba zai ce 2, ɗalibin dake bin sa ya ce 3, da sauransu.)
- A zagaya ana lura da aikin ɗaliban yayin da suke jefo da kama ƙwallon, suna faɗin lambobin dake gaba bisa tsari har zuwa 200.
- A maimaita wasan, a wannan lokaci da ƙirgen tsallaken lamba goma-goma har zuwa 200.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take: Rubutu da ɗaiɗai da kuma goma-goma (minti 5)

- A faɗi wata lamba tsakanin lamba 1-200.
- A nemi ɗalibai su rubuta lambar a cikin littafansu na rubutu.
- Bayan wani lokaci kaɗan, a rubuta lambar a kan allo, sai a nemi ɗalibai su bincika amsar da suka rubuta.

## Aikin Gida



A sa ɗalibai su yi gwajin ƙirge da ɗaiɗai da kuma goma-goma zuwa 200 a gida.

| Na. 32 | Zango na 1, Mako na 7, Darasi na B |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya ƙirge da rubuta lambobi biyar-biyar har zuwa 200.
**Kayan Aiki:** Jadawalin lambobi 1-200 da aka rubuta a kan allo **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

<u>Duba aikin gida (minti 2)</u>

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

<u>A yi Wasan Sunan Lamba (minti 3)</u>

- A rubuta lambar a kan allo. A nemi ɗalibai su faɗi sunan lambar. A maimaita sau da yawa.

## Koyo

<u>Gabatar da ƙirge da biyar-biyar zuwa 200 (minti 10)</u>

- **Ka/ki ce:** *Jiya mun koyi yadda ake ƙirge da goma-goma zuwa 200. A yau za mu yi ƙirge da biyar-biyar zuwa 200.*
- Ɗalibai su buɗe hannuwansu a gabansu ta yadda duk 'yan ajin za su ga yatsun nasu.
- **Ka/ki ce:** *Yatsu nawa muke da su a hannu ɗaya?*
- **Ka/ki ce:** *Kasancewar ɗalibai suna da yatsu biyar a hannu ɗaya, muna iya amfani da yatsunmu wajen yin ƙirge da biyar-biyar.*
- A nunawa ɗalibai yadda ake ƙirga zuwa 200 da biyar-biyar ta amfani da yatsunsu a matsayin misali. Suna iya ƙirga yatsunsu huɗu na farko, a asirce, sannan sai su faɗi lambar yatsan na biyar a bayyane.
- Daga nan, sai a yi ƙirgen tsallake daga 0 zuwa 200 da biyar-biyar, ana nunawa daga jadawalin lambobi. A sa ɗalibai su karanta a bayyane tare da malami. A tambayi ɗalibai idan sun lura da wani tsari.
- **Ka/ki ce:** *Idan mun fara da 0 muka yi ƙirgen tsallake da biyar-biyar, lambar za ta ƙare da 5 ko kuma 0.*

## Gwaji

<u>Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: A gyara tsarin (minti 15)</u>

- A rubuta lambobin "100 da 106 da 110 da 115 da 120" a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Idan ina ƙirgen tsallake da biyar-biyar, wace lamba ce ba daidai ba?*
- A nemi dalibai su yi aiki tare don su gano wace lamba ce ba daidai ba, kuma wace lamba ce daidai da ya kamata a rubuta. Dukkan ɗaliban, su rubuta amsoshinsu a cikin littafansu na rubutu. Suna iya duba amsarsu da ta abokan zamansu.
- A zagaya a lura da aikin da ɗaliban ke yi a kuma taimaka masu.
- A gayyato ɗalibai guda 2 su bayyana amsoshinsu, su yi bayanin yadda suka gano lambar da ba daidai ba.
- A maimaita aikin da wasu misalai.

## Bayyanawa

<u>Auna fahimta nan-take (minti 5)</u>

- A sa ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna abun da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su yi gwajin ƙirge da biyar-biyar zuwa 200 a gida. Ɗalibai su nuna aikinsu ga wani ɗan'uwansu ko abokinsu, su kuma tattauna a kan ko yin ƙirge da ɗaiɗai ko biyar-biyar ko goma-goma yana da sauƙi.

## Na. 33 | Zango na 1, Mako na 7, Darasi na C

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya ƙirge da rubuta lambobi da bibbiyu har zuwa 200.
**Kayan Aiki:** Jadawalin lambobi 1-200 da aka rubuta a kan allo **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

A yi Wasan Sunan Lambar (minti 2)

- A rubuta wata lamba a kan allo. A nemi ɗalibai su faɗi sunan lambar. A maimaita sau da yawa.

### Koyo

Kirge da bibbiyu zuwa 200 (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi yadda ake ƙirge da bibbiyu zuwa 200.*
- A umurci ɗalibai su ɗaga yatsunsu sama gwargwadon yadda suke iyawa a saman iska.
- **Ka/ki ce:** *Bari mu ƙirga kowane rukunin yatsun. Muna iya yin ƙirge da bibbiyu.*
- A zagaya cikin ajin a nuna kowane yatsan ɗalibi. A umurci ɗalibai su ƙirga 2 da 4 da 6 da 8 da sauransu har sai duk ɗalibai sun ƙirga yatsunsu. A umurci ɗalibai da su aje yatsunsu ƙasa bayan sun gama ƙirga su.
- Daga nan, sai a yi ƙirgen tsallake da bibbiyu, a fara da 0 zuwa 200, ana nuna kowace lamba daga cikin Jadawalin lambobin da aka zana a kan allo. A nemi ɗalibai su yi ƙirgen tare da malami. A tambayi ɗalibai ko sun lura da wani tsari.
- **Ka/ki ce:** *Idan mun fara ƙirge da 0 muka yi ƙirgen tsallake da bibbiyu, lambar za ta kare da 0 ko 2 ko 4 ko 6 ko kuma 8.*

### Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: A gyara tsarin (minti 10)

- A rubuta lambobin "102 da 104 da 105 da 108 da 110" a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Idan ina ƙirgen tsallake da bibbiyu, wace lamba ce ba daidai ba?*
- A umurci ɗalibai su yi aiki tare don su gano wace lamba ce ba daidai ba, kuma wace lamba ce daidai wadda ya kamata a rubuta. Dukkan ɗaliban su rubuta amsoshinsu a cikin littafansu na rubutu. Suna iya duba amsarsu da ta abokan zamansu.
- A zagaya ana lura da ɗalibai a kuma taimaka musu.
- A gayyato ɗalibai guda 2 su bayyana amsoshinsu, su yi bayanin yadda suka gano lambar da ba daidai ba.
- A maimaita aikin da wasu misalai.

### Bayyanawa

Gwajin aikin gida (minti 10)

- A buɗe littafin ɗalibai shafi na 17 sannan a karanta umurnin ciki.
- A yi aiki na farko tare da ɗalibai a aji. Ɗalibai su juyi aikin a cikin littafan rubutunsu.

### Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 17 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida. Ɗalibai su nuna aikinsu ga wani ɗan'uwansu ko abokinsu, su kuma tattauna a kan ko yin ƙirge da ɗaiɗai ko biyu-biyu ko biyar-biyar ko goma-goma yana da sauƙi.

| Na. 34 | Zango na 1, Mako na 7, Darasi na D |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya cike lambobi da babu tsakanin lamba 1 zuwa 200.
**Kayan Aiki:** Katunan lamba 1-10 **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Ni wace lamba ce? (minti 2)

- A karanta kowane daga cikin waɗannan jawaban. A nemi ɗalibai su ba da amsa tare da faɗin lambar a bayyane. Idan ɗaliban sun ba da amsa daidai, a nuna lambar da suka karanta a kan jadawalin lambobi 1-100.
- **Ka/ki ce:** *Da 1 na fi 199. Wace lamba nake?*
- **Ka/ki ce:** *Da 5 na fi 125. Wace lamba nake?*

**Koyo**

Gabatar da lambobi da babu (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu nemo lambobi da babu.*
- A sa ɗalibai 10 su zo gaban aji. Kowannensu ya ɗauki katin lamba guda sannan sai su jera kansu bisa tsari daga 1 zuwa 10. Za su tsaya a cikin layi, suna kallon ajin, su kuma ɗaga katin lambobinsu sama.
- **Ka/ki ce:** *Muna da ɗalibai 10, masu lambobi 1-10.*
- A sa ɗalibin da yake ɗauke da lamba ta 2, ya ɓoye katin lambarsa.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu dole mu yi tunani, wace lamba ce ta ɓata? Wace lamba ce ke zuwa bayan 1 ko kuma kafin 3?*
- A maimaita aikin da wasu ɗalibai daban, suna ɓoye lambobinsu.

**Gwaji**

Aiki a cikin ƙaramin rukuni: Gano lambobi da babu (minti 10)

- A sa ɗalibai su zauna a cikin ƙanana rukunai. A nemi kowane rukuni su zaɓi jagora guda.
- A rubuta lambobin "141 da 142, ___, 144 da 145 da 146" a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Wace lamba ce ta ɓata a tsarin?*
- A sa ɗalibai su yi aiki tare domin su gano lambar da ta ɓata. Dukkan ɗaliban su rubuta amsarsu a cikin littafansu na rubu.
- A zagaya ana lura da ɗalibai a kuma taimaka masu.
- A gayyato rukunonin su faɗi amsoshinsu, su kuma yi bayanin idan sun yi ƙirgen su ne da ɗaiɗai ko bibbiyu ko biyar-biyar ko kuma goma-goma.
- A maimaita aikin da wasu misalai; (ƙirge da ɗaiɗai da bibbiyu da biyar-biyar da kuma goma-goma).

**Bayyanawa**

Gwajin aikin gida (minti 10)

- A buɗe littafin ɗalibai shafi na 18 sannan a karanta umurnin ciki.
- A yi aiki na farko tare da ɗalibai a aji. Ɗalibai su juyi aikin a cikin littafan rubutunsu.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 18 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

| Na. 35 | Zango na 1, Mako na 7, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi bita da gwajin abun da suka koya a cikin wannan makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Bayyanawa da Raɗa: Kirge daga 0 zuwa 100 da ɗaiɗai da bibbiyu da biyar-biyar da kuma goma-goma (minti 5)

- A yi ƙirge daga 0 zuwa 100 a kan jadawalin lambobin, tare da nuna kowace lamba a lokacin da ake faɗinta. A nemi ɗalibai su yi ƙirgen tare da malami, ana sassauyawa tsakanin bayyanawa da kuma raɗa (alal misali: daga 0 zuwa 9 dukkan ɗalibai za su karanta lambobin a bayyane. Daga 10 zuwa 19, dukkan ɗalibai za su yi karatun cikin raɗa. A cigaba da yin haka har zuwa 100..
- A maimaita ƙirgen zuwa 200 da bibbiyu da biyar-biyar da kuma goma-goma.

### Koyo

Bita da maimai (minti 8)

- A zaɓi wani darasi daga cikin darrusan da aka yi a cikin makon, wanda ake ganin ɗalibai ba su fahimce shi sosai ba. A sake koyar da darasin ko a sake koyar da shi ta wata sabuwar hanya daban.

### Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai a cikin rukuni: Zane da kuma rubutu (minti 15)

- A ba ɗalibai aikin da zai taimaka musu wajen yin gwajin darasin da aka yi bita (alal misali; ƙirge zuwa 200 da ɗaiɗai ko bibbiyu ko kuma goma-goma). Ɗalibai na iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma a cikin ƙananan rukunai.
- Yayin da ɗalibai suke gudanar da wani aikin da aka ba su, a ƙara taimaka musu a inda ba su gane sosai ba.

### Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala a lokacin Gwajin.

### Aikin Gida

A ba ɗalibai aikin gida na bita da kuma gwajin ƙwazonsu.

| Na. 36 | Zango na 1, Mako na 8, Darasi na A |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su yi amfani da kara da damin kara don su nuna kimar lamba na lambobi har zuwa lamba ta 99.
**Kayan Aiki:** Kara da zare **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.


Wasan Bayyanawa da Raɗa: Kirge daga 0 zuwa 100 da ɗaiɗai (minti 3)

- A yi ƙirge daga 0 zuwa 100 a kan jadawalin lambobin, tare da nuna kowace lamba a lokacin da ake faɗinta. A nemi ɗalibai su yi ƙirgen tare da malami, ana sassauyawa tsakanin bayyanawa da raɗa.

## Koyo

Gabatar da Gidan goma-goma da gidan ɗaya ta amfani da damin kara (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi wani abu a kan kimar lamba.*
- A bayyana labarin dake ƙasa yayin da ake gwajin ayyukan da kara.
- **Ka/ki ce:** *Musa ya kewaya ya samo wasu kara. Ya ƙirga karan. Bayan ya ƙirga karan, ya haɗa damin kara guda 10. Ya ɗauki wani ɗan zare ya ɗaure kara guda 10 wuri guda, don ya samar da damin kara goma. Daga nan sai ya sake ƙirga wasu kara guda 10, ya ɗaure su wuri guda don ya samar da wani damin 10 na biyu. Ya ƙirga sauran karan sai ya ga kara 4 kawai ne suka rage masa, waɗanda ba su isa ya samar da wani damin goma ba. Jimmilar kara nawa Musa yake dasu gaba ɗaya?*




- A ƙirga jimillar yawan karan tare da ɗalibai a bayyane, da farko a ƙirga goma-goman, sannan sai a ƙirga ɗaiɗayan.
- **Ka/ki ce:** *Damin goma-goma da Musa ya ƙirga suna iya zama a cikin gidajen gwammai. Karan ɗaiɗai kuwa suna iya zama a cikin gidajen ɗaiɗai.*
- Umurci ɗalibai 2 su zo gaban aji, su ɗaga damin kara biyu a gaban gidajen gwammai. A rubuta 2 a cikin gidajen gwammai, sannan a nuna dami 2 na ɗaurin goma-goma.
- Umurci ɗalibai huɗu su zo gaban aji, su ɗaga kara ɗaiɗai guda huɗu a gaban gidajen ɗaiɗai. A rubuta 4 a cikin gidajen ɗaiɗai.
- **Ka/ki ce:** *Musa yana da kara 24. Akwai goma-goma guda biyu a cikin 24. Akwai kuma ɗaiɗai guda hudu a cikin 24.*

## Gwaji

Aiki a cikin ƙaramin rukuni: Gidan goma-goma da gidan ɗaiɗai (minti 15)

- A sa ɗalibai su zauna a cikin ƙananan rukunai. A zaɓi jagora daga kowane rukuni da zai taimaka wajen raba damin kara da littafan yara ga rukuninsu. A sa ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai shafin dake da gidajen gwammai da kuma gidajen ɗaiɗai da ba komai a cikinsu.
- A rubuta lambobi 1-100 a kan allo, sannan sai a nemi ɗalibai su yi aiki a cikin rukunansu, su yi amfani da damin karan da karan ɗaiɗai domin su nuna lambobinsu.
- A zagaya ana lura da ɗalibai, yayin da malami yake maimaita labarin. A yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai gidan goma-goma da kuma ɗaiɗai nawa suka samu. Idan da lokaci, a maimaita da wata lamba.

## Bayyanawa

Nuna kyawawan misalai (minti 5)

- A fito da rukunin ɗalibai ɗaya ko biyu waɗanda suka kammala aikin rukuninsu da kyau. A nemi aji su tashi tsaye su kalli misalansu.

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai su zana lamba 75 a cikin littafinsu na rubutu ta amfani da ɗaurin goma goma da ɗaiɗaya.

| Na. 37 | Zango na 1, Mako na 8, Darasi na B |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi amfani da kara da gidajen gwammai da kuma gidajen ɗaiɗai don su nuna kimar lamba na lambobi har zuwa lamba ta 99.
**Kayan Aiki:** Kara da damin kara goma-goma da katunan lambobi 1-9 **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

<u>Duba aikin gida (minti 2)</u>


- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa amsu gwiwa.

<u>Wasan Kirge (minti 3)</u>

- A yi wa ɗalibai bayanin cewa za a faɗi wata lamba. Da zarar an faɗi lambar, sai su fara ƙirge daga lambar da goma-goma da sauri. Alal misali, idan aka ce "40," ɗalibai sai su fara faɗin "50, 60, 70, 80..."
- Bayan ʻyan daƙiƙai kaɗan, sai a ce "su tsaya." Daga nan sai a sake maimaita wannan tsarin da wata sabuwar lamba.

**Koyo**

<u>Kirgen da goma-goma da kuma ɗaiɗai (minti 10)</u>




- **Ka/ki ce:** *A yau za mu yi amfani da kara don nuna kimar lamba har zuwa 99.*
- A zana hoton gidajen gwammai da gidajen ɗaiɗai a kan allo. A aje teburi a gaban kowane daga cikin gidajen.
- A aje damin kara goma guda ɗaya a gaban gidajen gwammai da kuma kara ɗaiɗai guda uku, a gaban gidajen ɗaiɗai.
- A nemi ɗalibai su faɗi adadin goma nawa da adadin ɗaiɗai nawa lambar ta ƙunsa.
- A rubuta lamba 1 a gidajen gwammai da lamba 3 a gidajen ɗaiɗai.
- **Ka/ki ce:** *Akwai damin kara goma guda 1. Akwai kuma kara ɗaiɗai guda uku. Lambar ita ce 13.*
- Idan da lokaci, a maimaita da wata lamba sai a kira wani ɗalibi ya zo gaban aji ya cike gidajen gwammai da kuma gidajen ɗaiɗai.

**Gwaji**

<u>Aiki a cikin ƙaramin rukuni: Amfani da damin kara domin a gane kimar lamba (minti 15)</u>

- A sa ɗalibai su zauna a cikin ƙanana rukunai. A zaɓi jagora daga kowane rukuni da zai taimaka wajen raba katunan lamba da damin kara ga rukuninsu.
- A sa ɗalibai su aje katunan lambarsu a wuri guda a tsakiyar rukuninsu.
- Daga nan, sai a yi wa ɗalibai bayanin cewa, su buɗe katunan lambarsu guda biyu don su samar da lamba ʻyar tagwai.
- Daga na sai ɗalibai su samar da damin goma-goma da karansu domin su nuna lambar dake kan katinsu.
- A zagaya ana lura da ɗalibai. A yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai goma-goma da kuma ɗaidai nawa suka samar da lambar dake kan katinsu, sannan a duba ko sun amsa daidai.
- Idan da lokaci, a nemi ɗalibai su maimaita aikin da sababbin katuna guda biyu.

**Bayyanawa**

<u>Auna fahimta nan-take (minti 5)</u>

- A rubuta lambar a kan allo. A nemi ɗalibai su faɗi goma-goma nawa da ɗaiɗai nawa ne a wurin. Ɗalibai su ɗaga lambar adadin yatsun da suka yi daidai da kowace amsa sama.

**Aikin Gida**

A gayawa ɗalibai jimillar yawan ɗaliban dake cikin ajin. A sa ɗalibai su zana hoton gidan gwammai da kuma gidan ɗaiɗai, su kuma nuna jimillar yawan mutanen dake cikin ajin a cikinsu.

| Na. 38 | Zango na 1, Mako na 8, Darasi na C |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya amfani da gidajen gwammai da kuma gidajen ɗaiɗai don su nuna kimar lamba a rubuce har zuwa 99.
**Kayan Aiki:** Ɗaurin damin kara goma-goma da kara ɗaiɗai **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)


- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masi gwiwa.

Ni wace lamba ce? (minti 3)

- A karanta kowane daga cikin waɗannan jawaban. A nemi ɗalibai su ba da amsa ta faɗin lambar a bayyane.
- **Ka/ki ce:** *Ni damin goma-goma 3 ne da kuma ɗaiɗai guda 2. Ni wace lamba ce?*
- **Ka/ki ce:** *Ni damin goma-goma 9 ne da 0 guda ɗaya? Ni wace lamba ce?*
- **Ka/ki ce:** *Ni damin goma-goma 8 ne da kuma ɗaiɗai guda 9. Ni wace lamba ce?*

**Koyo**

Gabatar da nuna kimar lamba ta hanyar rubutu (minti 10)




- **Ka/ki ce:** *A yau za mu cigaba da nuna kimar lamba ta hanyar rubuta lambobin gidajen goma-goma da kuma gidajen ɗaiɗai da kowace lamba ta ƙunsa.*
- A kira ɗalibai biyu su zo gaban aji. A baiwa ɗalibi guda damin kara goma-goma guda 4, ɗalibin ɗayakuwa a ba shi kara ɗaiɗai guda 8.
- **Ka/ki ce:** *Goma-goma nawa kake dasu? Kara daiɗai guda nawa kake dasu?*
- A nemi ɗaliban biyu su rubuta amsoshinsu a cikin gidajen gwammai da kuma gidajen ɗaiɗai.
- **Ka/ki ce:** *Akwai goma-goma 4. Akwai kuma ɗaɗai 8. Lambar ita ce 48.*
- A maimaita da wasu ɗalibai da kuma adadin yawan wasu kara daban.

**Gwaji**

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: Rubuta lambobin gidan goma-goma da kuma lambobin gidan ɗaiɗai (minti 15)

- A nemi ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 19.
- A karanta umurni da aka rubuta da tambayar farko a bayyane ga ɗalibai.
- A yi bayanin cewa su kalli karan da aka jere a gidajen gwammai da kuma gidan ɗaiɗai. Su ƙirga jimillar yawan damin goma-goma da kuma karan da suke ɗaiɗai. Ɗaliban su rubuta amsarsu a cikin littafansu na rubutu.
- A zagaya ana lura da ɗalibai a kuma taimaka masu. Yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai yadda suka samo amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.
- Idan akwai lokaci, a kammala lissafin na gaba dake a kan shafin. Suna iya duba amsarsu da ta abokan zamansu.

**Bayyanawa**

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A sa wani ɗalibai ya rubuta amsar tambaya ta farko a kan allo.
- A nemi wasu ɗalibai su duba idan amsar daidai take ko ba daidai take ba ta hanyar ɗaga babban yatsansu sama ko kuma ƙasa. A yi gyara idan akwai buƙatar hakan.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 19 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

| Na. 39 | Zango na 1, Mako na 8, Darasi na D |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya amfani da gidajen ɗaruruwa da gidajen gwammai da kuma gidajen ɗaiɗai don su nuna kimar lamba har zuwa 200.

**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

<u>Duba aikin gida (minti 2)</u>


- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

<u>Ni wace lamba ce? (minti 3)</u>

- A karanta kowane daga cikin waɗannan jawaban. A nemi ɗalibai su ba da amsa ta faɗin lambar a bayyane.
- **Ka/ki ce:** *Ni damin goma-goma 4 ne da kuma ɗaya 1. Ni wace lamba ce?*
- **Ka/ki ce:** *Ni damin 0 ne na goma-goma da ɗaiɗai guda 6? Ni wace lamba ce?*

## Koyo

<u>Gabatar da kimar lambar gidajen ɗaruruwa (minti 10)</u>




- **Ka/ki ce:***Mun yi darrusan dake nuna kimar lamba na lambobi har zuwa 99. A yau za mu koyi yadda ake gane kimar lambobn dake gidajen ɗaruruwa.*
- A zana hoton gidan ɗaruruwa da gidan gwammai da kuma gidan ɗaiɗai a kan allo.
- A nemi ɗalibi guda ya zo gaban aji sai a ba shi kara ɗaiɗai guda goma. A nemi ɗaliban aji da su ƙirga karan a bayyane, ɗaya bayan ɗaya. A nemi su rubuta jimillar yawan karan a cikin gidajen da aka zana hotonsu a kan allo a cikin gidan ɗaiɗai.
- **Ka/ki ce:** *Ku tuna, a cikin kowane daga cikin gidajen, muna iya samun lambobi ne kawai tsakanin 1-9. Saboda haka, duk lokacin da na cimma lamba 10, a gurbin gidajen ɗaiɗai, ina shafe ta in mayar da ita 1 a cikin gurbin gidajen gwammai, ɗaiɗai guda 10, daidai suke da goma guda 1.*
- A shafe lamba ta goma a cikin gurbin gidajen ɗaidai, sannan sai a rubuta 1, a gurbin gidajen gwammai.
- A kira wani ɗalibi daban, ya zo gaban aji, sai a ba shi ɗaurin damin goma-goma guda goma. A nemi ɗalibai da su ƙirga damin goma-goman a bayyane. A nemi su rubuta adadin jimillar damin karan a cikin gidajen dake kan allo, a gurbin gidajen gwammai.
- **Ka/ki ce:** *Muna iya rubuta 1-9 kawai a cikin kowane gida. Saboda haka idan muna da ɗaurin damin goma-goma, muna iya shafe shi daga cikin gurbin gidajen gwammai, sannan sai mu rubuta 1 a cikin gidajen ɗaruruwa. Ɗari, daidai take da goma-goma sau goma.*
- A shafe lamba 10 daga gurbin gidajen gwammai, sai ka/ki rubuta 1, a cikin a gurbin gidajen ɗaruruwa.

## Gwaji

<u>Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: Nuna lambobin kimar lambobi 1-200 (minti 15)</u>

- A umurci ɗaliba su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 20. A karanta umurni da aka rubuta da tambayar farko a bayyane ga ɗalibai.
- A zagaya ana lura da ɗalibai a kuma taimaka musu. Yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai yadda suka samar da amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.
- Idan da lokaci, a umurci ɗalibai su kammala lissafi na gaba dake kan shafin. Suna iya duba amsarsu da ta abokan zamansu.

## Bayyanawa

<u>Auna fahimta nan-take (minti 5)</u>

- A sa wani ɗalibai ya rubuta amsar tambaya ta farko a kan allo.
- A nemi wasu ɗalibai su duba idan amsar daidai take ko ba daidai take ba ta hanyar ɗaga babban yatsansu sama ko kuma ƙasa. A yi gyara idan akwai buƙatar hakan.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 20 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

| Na. 40 | Zango na 1, Mako na 8, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi bita da gwajin abun da suka koya a cikin wannan makon.
**Kayan Aiki:** Jakar ƙwarorin wake ko tsakuwoyi **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Canke (minti 8)

- A nemi ɗalibai su canki jimillar tsakuwoyi ko ƙwarar wake nawa ne a cikin jakar.
- Nemi su zana hoton gidajen ɗaruruwa da gidajen gwammai da ɗaiɗai a cikin littafansu na rubutu, su kuma rubuta lambobin a cikinsu don su nuna cankan da suka yi.
- Nemi ɗalibai 2 ko 3 su bayyana cankan da suka yi ga ajin gaba ɗaya.
- A faɗi lambar jimillar ƙwarar wanke ko tsakuwoyin ta hanyar rubuta ta a kan allo.

## Koyo

Bita da maimai (minti 5)

- A zaɓi wani darasi daga cikin darrusan da aka yi a cikin makon, wanda ake ganin ɗalibai ba su fahimce shi sosai ba. A sake koyar da darasin ko a sake koyar da shi ta wata sabuwar hanya daban.

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai a cikin rukuni: Zane da kuma rubutu (minti 15)

- A baiwa ɗalibai aikin da zai taimaka musu wajen yin gwajin darasin da aka yi bita (alal misali; amfani da gidajen ɗaruruwa da gidajen gwammai da kuma gidajen ɗaiɗai wajen yin ƙirge). Ɗalibai na iya yin aiki ɗaiɗaikunsu ko kuma a cikin ƙananan rukunai.
- Yayin da ɗalibai suke gudanar da wani aikin da aka ba su, a ƙara taimaka masu a inda ba su gane sosai ba.

## Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala a lokacin Gwajin.

## Aikin Gida

A baiwa ɗalibai aikin gida na bita da kuma gwajin ƙwazonsu.

| Na. 41 | Zango na 1, Mako na 9, Darasi na A |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya ƙirgen lambobi daga 1 zuwa 1,000 da ƙirgen ɗaiɗai.
**Kayan Aiki:** Jakar tsakuwoyi ko ƙwarorin wake **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Canke (minti 3)

- A ɗaga jakar ƙwarorin wake ko tsakuwoyi a sama sai a nemi ɗalibai su canki ƙwara nawa ne a cikin jakar.
- **Ka/ki ce:** *Akwai ɗaruruwa a ciki! Za a ɗauki lokaci mai tsawo kafin a ƙirga kowane ɗaya daga cikin tsakuwoyin ko ƙwarorin waken dake ciki!*

**Koyo**

Gabatar da ɗari-ɗari: Kirgen yatsu (minti 15)

- ***Ka/ki ce:*** *A yau za mu yi ƙirge zuwa 1,000. Mafi yawa, muna yi ƙirge zuwa 1,000, idan muna ƙirga kuɗi, ko awon nauyi ko awon nisa. Alal misali, idan za mu sayi pakitin siga, muna buƙatar ₦500. Idan za mu sayi kiret ɗin ƙwai, muna buƙatar ₦1,900! Sannan kilomita daya kuwa ya ƙunshi mitoci 1,000.*
- A umurci ɗalibai su ba da wasu misalai dake buƙatar dole sai sun yi ƙirge har zuwa 1,000.
- **A ce :** *Yatsu nawa kuke tunanin akwai a cikin ajin nan? Bari mu ƙirga yatsunmu don mu ga yatsu nawa muke da.*
- A umurci ɗalibai su ɗaga yatsunsu 10 sama gwargwadon yadda suke iyawa.
- A zagaya a cikin ajin, ana nuna kowane daga cikin yatsun ɗaliban. A sa ɗalibai su ƙirga yatsa ɗaya bayan ɗaya a bayyane tare da kai/ke har sai an ƙirge yatsun gaba ɗaya. A sa ɗalibai su aje yatsunsu a ƙasa bayan an gama ƙirga su
- A rubuta lambar jimillar yawan yatsun a kan allo, sannan a maimaita karanta lambar a bayyane.
- **Ka/ki ce:** *Mu ɗauka muna da ɗalibai 100 a cikin aji daya , kowane yana da yatsu 10. A nan muna da yatsu 1,000.*

**Gwaji**

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai bibbiyu: Kirgen yatsu (minti 10)

- A umici ɗalibai su buɗe littafin ɗalibaia Shafi na 21.
- **Ka/ki ce:** *Ku duba hotunan hannuwa. Kowane hannu dake cikin wannan shafin yana da yatsu guda biyar. Ku yi aiki tare da aboka zamanku, ku ƙirga jimillar yawan yatsun dake a kan wannan shafin. Kuna iya amfani da jadawalin lambobinku dubu dake farkon bangon littafinku na yara idan kuna buƙatar taimako.*
- A sa ɗalibai su rubuta amsoshinsu a cikin littafan rubutunsu.
- A zagaya ana lura da ɗalibai a kuma taimaka musu.

**Bayyanawa**

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A sa wani ɗalibi ya rubuta amsarsa a kan allo.
- A umurci wasu ɗalibai su duba idan amsar daidai take ko ba daidai take ba ta hanyar ɗaga babban yatsansu sama ko kuma ƙasa. A yi gyara idan akwai buƙatar hakan.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su tambayi wani ɗan'uwansu ko abokinsu wane aiki ne yake yi dake sa shi yin ƙirge har zuwa 1,000.

| Na. 42 | Zango na 1, Mako na 9, Darasi na B |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya ƙirge da rubuta lambobi cikin ɗaruruwa har zuwa 1,000.
**Kayan Aiki:** Jadawalin ƙirge daga 1-1000 da aka rubuta a kan allo da takardun kuɗi na Naira 100
**Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Kirge (minti 3)

- A yi wa ɗalibai bayanin cewa za a faɗi wata lamba. Da zarar an faɗi lambar, sai su fara ƙirge daga lambar da goma-goma da sauri. Alal misali, idan aka ce "40," ɗalibai sai su fara faɗin "50, 60 70, 80..."
- Bayan 'yan daƙiƙai kaɗan, sai a ce "su tsaya." Daga nan sai a sake maimaita wannan tsarin da wata sabuwar lamba.

## Koyo

Gabatar da ƙirge zuwa 1,000 da ɗari-ɗari (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Kirge zuwa 1,000 da ɗaiɗai yana ɗaukar lokaci mai tsawo. A yau, za mu yi ƙirge zuwa 1,000 da sauri.*
- A tambayi ɗalibai idan sun san wata hanyar da ake yin ƙirge zuwa 1,000 cikin sauri.
- **Ka/ki ce:** *Muna iya yin ƙirge zuwa 1,000 da bibbiyu ko biyar-biyar ko kuma da goma-goma. Haka ma muna iya yin ƙirgen da ɗari-ɗari!*
- A yi ƙirgen tsallake daga 0 zuwa 1,000 da ɗari-ɗari, ana nuna jadawalin lambobi 1-1000 dake kan allo. Nemi ɗalibai su maimaita bayan ka/kin yi ƙirgen. Daga nan, sai a tambaye su ko sun lura da wani tsari.
- **Ka/ki ce:** *Idan muka fara da 0 muka yi ƙirge da ɗari-ɗari, gurbin goma-goma da gurbin ɗaiɗai koyaushe 0 ne, amma gurbin ɗaruruwa yana sauyawa.*
- A rubuta lambobi 100 da 200 da 300 a kan allo domin ka/ki yi gwaji.

## Gwaji

Aiki a cikin ƙaramin rukuni: Kirge da Takardun Kuɗin Naira 100 (minti 15)

- A sa ɗalibai su zauna a cikin ƙanana rukunai. A zaɓi jagora daga kowane rukuni.
- A nemi wani ɗalibi ya taimaka wajen raba takardun kuɗin wasa na Naira 100 ga kowane rukuni. A baiwa kowane rukuni aƙalla takardun kuɗin naira 100 guda biyar zuwa guda goma.
- A sa ɗalibai su ƙirga jimillar yawan kuɗin dake gare su, su yi ƙirgen da ɗari-ɗari.
- A zagaya ana lura da ɗalibai, a kuma taimaka musu. A yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai yadda suka samo amsar tasu, a kuma duba ko jimmilar kimar yawan kuɗin daidai ne.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A nuna wata lamba (100, 200, 300, 400, 500, 600, 700, 800, 900, or 1000) ba bisa tsari ba a kan Jadawalin lambobi 1-1000 sai a nemi ɗalibai su karanta lambar.


## Aikin Gida

A sa ɗalibai su rubuta lambobi daga 0 zuwa 1,000 da ɗari-ɗari a gida a cikin littafansu na aiki.

| Na. 43 | Zango na 1, Mako na 9, Darasi na C |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya rubuta lambobi daga lamba 1 zuwa 1,000.
**Kayan Aiki:** Katunan lamba 1 zuwa 9 **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi




Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan canke (minti 3)

- A nemi ɗalibai su yi canken faɗin ɗalibai nawa ne a makarantarsu.
- A nemi ɗalibai 2 ko 3 su bayyana canken da suka yi ga aji ta hanyar rubuta lambar a cikin jadawalin kimar lamba.
- A gaya wa ɗalibai jimillar yawan ɗaliban makarantar, don su  su kwatanta da canken da suka yi.

## Koyo

Rubuta kimar lambobi daga lamba 1-999 (minti 10)

- A nemi ɗalibai uku su zo gaban aji, kowannensu ya zaɓi katin lamba guda ɗaya. Za su tsaya a cikin layi don su nuna lambar katunansu ga ajin.
- A yi bayanin cewa kowane ɗalibi yana wakiltar wani kimar lamba ne. Mun san tsarin daidai da tsarin da suka tsaya a ciki. Ɗalibi guda a gurbin ɗari-ɗari da ɗalibi guda a gurbin goma-goma da kuma wani ɗalibi guda a gurbin ɗaiɗai.
- A nemi wani ɗalibi ɗayaya zo gaban allo ya rubuta lambar da take daidai a cikin gidan ɗaruruwa da gidan gwammai da kuma gidan ɗaiɗai.
- A maimaita aikin, tare da neman ɗalibai su sauya tsarin da suka tsaya ko kuma su zaɓi wasu katunan lamba na daban don su samar da wata lamba daban.

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai bibbiyu: Rubuta lambobi (minti 15)

- A umurci ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 22.
- A karanta umurnin da kuma tambaya ta farko a bayyane ga ɗalibai.
- A sa ɗalibai su warware lissafin a cikin littafansu na rubutu ta hanyar rubuta lambar da damin ɗari-ɗari da damin goma-goma da ɗaiɗai da suka nuna.
- A zagaya ana lura da ɗalibai. A yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai yadda suka samo amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu sama, su nuna abun da suka rubuta. A yabawa ɗalibai.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 22 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

| Na. 44 | Zango na 1, Mako na 9, Darasi na D |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya cike lambobi da babu daga lamba 1 zuwa 1,000.
**Kayan Aiki:** Katunan lamba 100, 200, 300, 400, 500, 600, 700, 800, 900 da kuma 1,000
**Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Ni wace lamba ce? (minti 3)

- A karanta kowane daga cikin waɗannan jawaban. A nemi ɗalibai su ba da amsa ta faɗin lambar a bayyane.
- **Ka/ki ce:** *Da 1 na fi 299. Ni wace lamba ce?*
- **Ka/ki ce:** *Da 5 na fi 825? Ni wace lamba ce?*

**Koyo**

Lambobi da babu (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu nemo lambobi da babu*
- A kira ɗalibai 10 su zo gaban aji. Kowanensu ya zaɓi ɗaya daga cikin waɗannan katunan lamba (100, 200, 300, 400, 500, 600, 700, 800, 900, 1000) su kuma jera kansu a kan tsari. Za su tsaya a cikin layi, suna fuskantar sauran ɗaliban aji, sannan sai su ɗaga lambar katin sama.
- **Ka/ki ce:** *Muna da ɗalibai 10, da aka yi wa lambobi 100-1,000.*
- A umurci ɗalibin dake ɗauke da lamba ta 600 ya ɓoye katin lambarsa. .
- **Ka/ki ce:** *Dole sai na yi tunani, wace lamba ce ta babu? Wace lamba ce ke zuwa bayan 500 ko kafin 700?*
- A maimaita aikin da wasu ɗalibai daban, su kuma ɓoye katunan lambarsu domin su nuna wasu lambobi daban da babu.

**Gwaji**

Aiki a cikin ƙaramin rukuni: Neman lamba da babu (minti 10)

- A sa ɗalibai su zauna a cikin ƙanana rukunai. A nemi kowane rukuni su zaɓi jagora.
- A rubuta lambobin 940, 950, 960, ___, 980, 990, 1,000 a kan allo sannan sai ka/ki faɗi lambobin a bayyane tare da ajin gaba ɗaya.
- **Ka/ki ce:** *Da farko, bari mu yi tunanii. Wace lamba ce na tsallake? ɗaiɗai ko bibbiyu ko biyar-biyar ko goma-goma ko kuma ɗari-ɗari?*
- Ka/ki ce: *Haka ne, mun yi ƙirgen tsallake da goma-goma. Wace lamba ce babu?*
- A umurci ɗalibai su yi aiki tare domin su gano lambar da babu. Dukkan ɗaliban su rubuta amsar a cikin littafansu na rubutu.
- A zagaya ana lura da ɗalibai, a kuma taimaka masu.
- A umurci rukunai da su bayyana amsoshinsu.
- A maimaita aikin da ƙarin wasu misalai (Na yin ƙirge da bibbiyu da biyar-biyar da goma-goma da kuma ɗari-ɗari)

**Bayyanawa**

Gwajin aikin gida (minti 10)

- A buɗe littafin ɗalibai shafi na 23 sannan a karanta umurnin ciki.
- A yi aiki na farko tare da ɗalibai a aji. Ɗalibai su juyi aikin a cikin littafan rubutunsu.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 23 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

**Na. 45** | # Zango na 1, Mako na 9, Darasi na E

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi bita da gwajin abun da suka koya a cikin wannan makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Kirgen Tsalle (minti 3)

- A umurci ɗalibai da su tashi tsaye.
- A umurci ɗalibai da su yi ƙirge daga 0 zuwa 1,000 da ɗari-ɗari, suna yin tsalle sama a duk lokacin da suka faɗi wata lamba.

## Koyo

Bita da maimai (minti 10)

- A zaɓi wani darasi daga cikin darrusan da aka yi a cikin makon, wanda ake ganin ɗalibai ba su fahimce shi sosai ba. A sake koyar da darasin ko a sake koyar da shi ta wata sabuwar hanya daban.

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai a cikin rukuni : Zane da kuma rubutu (minti 15)

- A baiwa ɗalibai aikin da zai taimaka musu wajen yin gwajin darasin da aka yi bita (alal misali; yin ƙirge zuwa 1,000 da ɗaiɗai da goma-goma ko da ɗari-ɗari ko kuma nema wata lamba da babu tsakanin lamba 1 zuwa 1,000. Ɗalibai suna iya yin aiki ɗaiɗaikunsu ko kuma a cikin ƙananan rukunai.
- Yayin da ɗalibai suke gudanar da wani aikin da aka ba su, a ƙara taimaka musu a inda ba su gane sosai ba.

## Bayyanawa

Bita da kuma bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala a lokacin Gwaji.

## Aikin Gida

A baiwa ɗalibai aikin gida na bita da kuma gwajin ƙwazonsu. A sa ɗalibai su tara kara gwargwadon yadda suke iyawa a gida, su kuma zo da su aji gobe.

| Na. 46 | Zango na 1, Mako na 10, Darasi na A |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi amfani da kara da damin kara domin su nuna kimar wurin lambobi har zuwa 999.

**Kayan Aiki:** Jakar tsakuwoyi ko ƙwarorin wake da kara da kuma zare **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)


- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

A yi Wasan Sunan Lamba (minti 3)

- A rubuta wata lamba daga 0 zuwa 1,000 a kan allo. A nemi ɗalibai su faɗi sunan lambar. A maimaita da wata lambar.

**Koyo**

Gabatar da kimar lamba har zuwa lamba ta 999 (minti 10)




- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi kimar lamba har zuwa 999!*
- A ɗaga jakar tsakuwoyi ko wake sai a tambayi ɗalibai da su canki tsakuwoyi nawa ne a cikin jakar.
- A rubuta abinda sukacanka ɗaya bayan ɗaya a kan allo, sannan sai ka/ki yi naki cankar.
- **Ka/ki ce:** *Zan canki ko akwai wake 987 a cikin wannan jakar. Lallai ko waken na da yawa! 987 tana ɗauke da lambobi uku a cikinta, wannan ya nuna cewa dole ne mu yi amfani da gidajen ɗaruruwa da gidajen gwammai da kuma gidajen ɗaiɗai. Akwai 9 a gurbin ɗaruruwa, saboda haka zan rubuta 9 a cikin gurbin gidan ɗaruruwa. Akwai 8 a gurbin gwammai, saboda haka zan rubuta 8, a gurbin gidan gwammai. Akwai 7 a gurbin gidan ɗaiɗai.*
- A kira wani ɗalibi ya zo gaban aji ya faɗi nasa canken tsakanin 1-1000 tsakuwoyi ƙwara nawa ne ke cikin jakar? Rubuta lambar a kan allo.
- A umurci wani ɗalibin ya rubuta ɗaiɗai guda nawa da goma-goma nawa da ɗari-ɗari nawa ne a cikin lambarshi.
- Idan da lokaci, a maimaita da ƙarin wasu ɗalibai da yawa, ana ba su dama suna yin canken, sannan a rubuta lambobinsu a cikin gidan ɗaruruwa da gwammai da kuma gidan ɗaiɗai.

**Gwaji**

Aiki a cikin ƙaramin rukuni: Ɗaruruwa da gwammai da kuma ɗaiɗai (minti 15)

- A sa ɗalibai su zauna a cikin ƙanana rukunai, sai su sa karan da suka zo da su daga gida a tsakiyar rukuninsu.
- **Ka/ki ce:** *Ku ƙirga dukkan karan da suke cikin rukuninku. Ku haɗa damin goma-goma na karan gwargwadon yadda kuke iyawa.*
- **Ka/ki ce:** *Da zarar kun kammala haɗa damin goma-goma, lokaci ya yi da za ku ƙirga jimillar kara nawa kuke da su. Ku tuna, kuna iya fara ƙirga damin kara goma-goma da kuke da su, sannan sai ku ƙirga sauran karan ɗaiɗai da suka rage muku.*
- A umurci ɗalibai su rubuta jimillar yawan karan da suka tattara a cikin littafansu na rubutu.
- A zagaya ana lura da ɗalibai, ana kuma taimaka masu. Dole ne kowane rukuni ya samu lambar jimillarsa ta daban.

**Bayyanawa**

Kwatancen amsoshi (minti 5)

- A nemi kowane rukuni ya bayyana adadin kara nawa ne rukunin nasu yake da su, sannan kuma ɗari-ɗari da goma-goma da ɗaiɗai nawa suke dasu. A rubuta amsoshinsu a kan allo.
- A sa ɗaliba su faɗi rukunin da ya fi kara masu yawa.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su tambayi wani ɗan'uwansu ko abokinsu ya faɗa musu wani abu dake zuwa cikin adadin ɗari-ɗari.

| Na. 47 | Zango na 1, Mako na 10, Darasi na B |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su yi amfani da hotuna domin su nuna kimar wurin lambobi har zuwa 999.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)


- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

A yi Wasan Sunan Lambar (minti 3)

- A rubuta wata lamba daga 0 zuwa 1,000 a kan allo. A nemi ɗalibai da su faɗi sunan lambar. A maimaita da wata lambar.

**Koyo**

Gabatar da kimar lamba har zuwa lamba ta 999 (minti 10)




- **Ka/ki ce:** *A yau za mu cigaba da gwajin kimar lamba har zuwa 999.*
- A zana hoton gidajen ɗaruruwa da gwammai da kuma ɗaiɗai a kan allo.
- A rubuta lambar 456 a kan allo. A kira wani ɗalibi guda ya zo gaban ajin ya cike gidajen ko kuma ya saka jadawalin kimar lamba da lambobin da suka dace.
- **Ka/ki ce:** *Lambar 456 tana da ɗari-ɗari guda 4 da gomo-goma 5 da kuma ɗaiɗai guda 6.*
- A nemi wani ɗalibi ya faɗi wata lamba. Ka/ki rubuta lambar a kan allo sai ka/ki kira ɗalibin ya zo ga allo ya cike jadawalin kimar lambar ko gidajen lambobin nata.
- Idan da lokaci, a sake maimaitawa da wasu ƙarin lambobi da kuma wasu ɗalibai daban.

**Gwaji**

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai bibbiyu: Nuna kimar lamba da bulo ko da damin kara (minti 15)

- A umurci ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 24.
- **Ka/ki ce:** *Akwai hanyoyi da yawa da ake iya nuna lambobi. A cikin wannan aikin, ana iya amfani da bulo da kuma kara don a nuna lambobin 1 da 10 da kuma 100.*
- A nuna kowane daga cikin hotunan (bulo da kuma kara) sannan a faɗi kimarsu a bayyane. Ka/ki umurci ɗalibai su maimaita faɗin kimarsu bayanka/ki.
- A karanta umurnin a kuma kammala lissafin farko tare da ajin gaba ɗaya. Ɗalibai su rubuta amsarsu a cikin littafansu na rubutu.
- A sa ɗalibai su cigaba da aiki domin su warware lissafin dake a kan shafin. Suna aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma tare da abokin zamansu.
- A zagaya ana lura da ɗalibai, a kuma taimaka musu. A yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai yadda suka samo amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.

**Bayyanawa**

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A rubuta lamba ta 259 a kan allo.
- A sa ɗalibai su ɗaga lambar yatsun da suke gurbin ɗaruruwa da gurbin gidajen gwammai da kuma gurbin ɗaiɗai a sama.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 24 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

| Na. 48 | Zango na 1, Mako na 10, Darasi na C |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su nuna kimar lambobi har zuwa ta 999 ta amfani da gidajen ɗaruruwa da gidajen gwammai da kuma gidajen ɗaiɗai.
**Kayan Aiki:** Katunan lamba 1-9 **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 3)


- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Ni wace lamba ce? (minti 2)

- A karanta kowane daga cikin waɗannan jawaban. A nemi ɗalibai su ba da amsa ta faɗin lambar a bayyane.
- **Ka/ki ce:** *Ni jeri 9 ne na bulo goma-goma da kuma ɗaiɗai guda 9? Ni wace lamba ce?*
- **Ka/ki ce:** *Ni jeri 9 ne na bulo ɗari-ɗari da jeri 9 na bulo goma-goma da ɗaiɗai guda 9. Ni wace lamba ce?*

## Koyo

Kimar lamba har zuwa lamba ta 999 (minti 10)




- **Ka/ki ce:** *A yau za mu cigaba da gwajin kimar lamba har zuwa 999.*
- A kira ɗaliba guda 3 su zo gaban aji, sannan a nemi kowannensu ya zaɓi katin lamba guda. Za su tsaya cikin layi, su nuna katunan lambarsu ga ajin. A tambayi aji su faɗi wace lamba ce, bayan sun karanta dukkan katunan lambobin nasu guda uku.
- **Ka/ki ce:** *Kowane ɗalibi yana wakiltar wani kimar lamba na daban. Mun san wannan kimar wurin lambar saboda tsarin da suka tsaya cikinsa. Ɗalibi ɗayayana cikin gurbin ɗaruruwa, ɗalibi ɗaya yana cikin gurbin gwammai, sai ɗalibi ɗayayana cikin gurbin ɗaiɗai.*
- A nemi ɗalibi ɗayaya zo gaban aji ya nuna lambobin da suke gidan ɗaruruwa da gidan gwammai da kuma gidan ɗaiɗai ta hanyar rubuta lambar da take daidai a gidajen ɗaruruwa da gwammai da kuma ɗaiɗai.
- A maimaita aikin, ta sa ɗalibai su sauya tsarin da suka tsaya, don su samar da wata lamba daban.

## Gwaji

Aiki a cikin ƙaramin rukuni: Nuna kimar lamba (minti 15)

- A sa ɗalibai su zauna a cikin ƙananan rukunai. A zaɓi jagora a kowane rukuni wanda zai taimaka wajen rarraba katunan lamba guda 3, masu lambobi daga 1-9.
- Ɗalibai su duba katunansu sau ɗaya tak, sannan sai su haɗa lamba mai lambobi 3. Su rubuta wannan lambar a cikin littafansu na rubutu.
- Daga nan sai su yi aiki tare don su gano wace lamba ce ya kamata a rubuta a cikin gidan ɗaruruwa da gidan gwammai da kuma gidan ɗaiɗai.
- A zagaya ana lura da ɗalibai, a kuma taimaka musu.
- Bayan kowane ɗalibi daga cikin rukunan ya kammala aikinsa, a baiwa jagoran kowane rukuni dama ya zaɓi ƙarin wasu katunan lamba uku sannan sai a sake maimaita aikin da wata sabuwar lamba.

## Bayyanawa

Nuna kyawawan misalai (minti 5)

- A nuna rukuni 1-2 da suka nuna kimar lamba daidai ta katunan lambobinsu. A nemi wani ɗalibi ɗayadaga cikin rukunin ya yi bayanin yadda suka samo amsar.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su rubuta lamba ta 569 a cikin littafansu na rubutu. A gida, ɗalibai su zana hoton gidan ɗaruruwa da gidan gwammai da kuma gidan ɗaiɗai, su kuma rubuta lambobin da suke daidai da kowane daga cikin gidajen.

| Na. 49 | Zango na 1, Mako na 10, Darasi na D |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su nuna kimar lambobi har zuwa ta 999 ta amfani da gidajen ɗaruruwa da gidajen gwammai da kuma gidajen ɗaiɗai.

**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 3)


- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Ni wace lamba ce? (minti 2)

- A karanta kowane daga cikin waɗannan jawaban. A nemi ɗalibai su ba da amsa ta faɗin lambar a bayyane.
- **Ka/ki ce :** *Ni jeri 2 ne na bulo goma-goma da kuma ɗaiɗai guda 6? Ni wace lamba ce?*
- **Ka/ki ce:** *Ni jeri 4 ne na bulo ɗari-ɗari da jeri 9 na bulo goma-goma da ɗaiɗai guda 8. Ni wace lamba ce?*

## Koyo

Kimar lamba: Ɗaruruwa da gwammai da kuma ɗaiɗai (minti 10)




- **Ka/ki ce:** *A yau za mu cigaba da ƙara gwajin kimar lamba har zuwa 999.*
- A rubuta lamabar 111 a kan allo. Daga nan sai a rubuta kowane yanki na lambar a cikin "gidan" da ya dace da shi
- **Ka/ki ce:** *Duk da yake akwai lamba 1 a cikin dukkan gidajen, tana da ma'anar kima daban-daban. 1 ta gurbin ɗaruruwa ta 100 ce. 1 ta gurbin gwammai, 10 ce. Sannan 1 ta gurbin ɗaidai, 1 ce.*
- A rubuta lambar 234 a kan allo. A nemi wani ɗalibi ya zo gaban aji ya sanya lambobin a gidajen da suke daidai da su. A nemi su faɗawa aji ɗaruruwa da goma-goma da kuma ɗaidai nawa ne a cikin lambar 234.
- A maimaita da wasu lambobi.

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai bibbiyu: Nuna kimar lamba daga 1-999 (minti 15)

- A umurci ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 25.
- A karanta umurnin da kuma tambayar farko a bayyane ga ɗalibai.
- A kammala lissafin farko tare da ajin gaba ɗaya. Daga nan sai a sa ɗalibai su kammala sauran lissafin a ɗaiɗaikunsu ko kuma su bibbiyu.
- A zagaya ana lura da ɗalibai, a kuma taimaka musu. A yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai yadda suka samo amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.
- Idan da lokaci, a nemi ɗalibai su kammala lissafi na gaba a cikin shafin.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A sa wani ɗalibi ya rubuta amsar tambaya ta farko a kan allo.
- A nemi wasu ɗalibai su duba idan amsar daidai take ko ba daidai take ba ta hanyar ɗaga babban yatsansu sama ko kuma ƙasa. A yi gyara idan akwai buƙatar hakan.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 25 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

| Na. 50 | Zango na 1, Mako na 10, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi bita da gwajin abun da suka koya a cikin wannan makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Ni wace lamba ce? (minti 5)

- A karanta kowane daga cikin waɗannan jawaban. A nemi ɗalibai su ba da amsa ta faɗin lambar a bayyane.
- **Ka/ki ce:** *Da 1 na fi 899? Ni wace lamba ce? (A rubuta amsar da take daidai a kan allo)*
- **Ka/ki ce:** *Da 1 na fi 200? Ni wace lamba ce? (A rubuta amsar da take daidai a kan allo)*
- A cigaba da wasu misalai.

**Koyo**

Bita da maimai (minti 10)

- A zaɓi wani darasi daga cikin darrusan da aka yi a cikin makon, wanda ake ganin ɗalibai ba su fahimce shi sosai ba. A sake koyar da darasin ko a sake koyar da shi ta wata sabuwar hanya daban.

**Gwaji**

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai a cikin rukunoni : Zane da kuma rubutu (minti 15)

- A baiwa ɗalibai aikin da zai taimaka musu wajen yin gwajin darasin da aka yi bita (alal misali; amfani da gidajen ɗaruruwa da gwammai da kuma ɗaiɗai wajen yin ƙirge. Ɗalibai suna iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma a cikin ƙananan rukunai.
- Yayin da ɗalibai suke gudanar da wani aikin da aka ba su, a ƙara taimaka musu a inda ba su gane sosai ba.

**Bayyanawa**

Bita da kuma bayyanawa (minti 3)

- A sa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala a lokacin Gwaji.

**Aikin Gida**

A baiwa ɗalibai aikin gida na bita da kuma gwajin ƙwazonsu.

**Na. 51**

# Zango na 1, Mako na 11, Darasi na A

**Manufa:** Ɗalibai za su iya nuna lambobin da suka ɗara wasu.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

A yi Wasan Ɗaga Babban yatsa ya kalli sama ko kuma ya kalli ƙasa (minti 3)

- A sa ɗalibai su amsa waɗannan tambayoyin ta hanyar ɗaga babban yatsansu sama ko kuma ƙasa.
- **Ka/ki ce:** *Idan muna son yin ƙirge daga 1 zuwa 55, shin sama za mu yi ko ƙasa? 13 zuwa 14 fa, sama ne ko ƙasa?*

## Koyo

Gabatar da lambar da ta ɗara wata (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu nuna lambobin da suka ɗara wasu yawa. Idan lamba ɗaya ta ɗara ɗaya yawa, yana nufin ta fi yawan kima.*
- A kira ɗalibai 20 su zo gaban aji sai a raba su a rukuni gida biyu na; rukunin mutane 13 da kuma rukunin mutane 7. Ka/ki ƙirga yawan ɗaliban dake cikin kowane rukunin a bayyane sannan sai ka/ki rubuta adadin yawan lambarsu a kan allo. Nemi ɗalibai su faɗi wane rukuni daga cikinsu ya ɗara wani yawan ɗalibai.
- **Ka/ki ce:** Rukunin dake da ɗalibai 13 shi ne ya ɗara, saboda 13 ta ɗara 7 yawa.
- A rubuta alamomin > da < a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Alamar > koyaushe tana nuna lambar da ta ɗara yawa. Don ku tuna da wannan, ita wannan alamar ta yi kama da sifar bakin kada. Kada koyaushe yana sha'awar cinye lambar da tafi yawa.*
- A kira ɗalibi ɗaya ya zo gaban aji sai a nemi ya cike wannan alamar: 13 ____ 7. Daga nan sai a nemi ɗalibin da ya yi gwajin buɗe bakin kada ya kuma yi kwaikwayon zai cinye 13.
- A maimaita matakan da wasu lambobi.

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai bibbiyu: Nuna lambar da ta ɗara yawa (minti 15)

- A umurci ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai inda ke da layin lamba ko kuma jadawalin lambobi a farkon bangon littafinsu domin samun taimako.
- A rubuta tagwayen lambobi da yawa a kan allo: 70 ____ 50 ; 123 ____ 41 ; 264 ___ 263
- A umurci ɗalibai su rubuta lambobin a cikin littafansu na rubutu sannan sai su cike alamar da ta dace < ko >. Ɗalibai na iya duba amsarsu da ta abokan zamansu.
- A zagaya ana lura da ɗalibai, a kuma taimaka musu. A yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai yadda suka samo amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.
- Bayan minti goma, a sa ɗalibai su karanta lissafin, a ba su dama su yi amfani da kalmomin "wadda ta ɗara" Alal misali; ɗalibai za su ce "70 ta ɗara 50 yawa."
- Idan da lokaci, a nemi ɗalibai su kammala ƙarin wasu misalai.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- Yi bayanin cewa za ka/ ki faɗi wani jawabi. Idan jawabin daidai ne, ɗalibai su ɗaga babban yatsansu sama. Idan jawabin kuskure ne, ɗalibai za su nuna babban yatsansu a ƙasa.
- **Ka/ki ce:** *5 ta ɗara 1. Daidai ne ko kuskure ne? 10 ta ɗara 100. Daidai ne ko kuskure ne?*

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su rubuta "999 ___ 123" a cikin littafansu na aiki, su kuma cike alamar da take daidai daga cikin alamomin: > ko <

| Na. 52 | Zango na 1, Mako na 11, Darasi na B |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya nuna lambobin da suka gaza wasu ko kuma waɗanda suke daidai da wasu.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

A yi Wasan Daidai ne ko ba daidai ba ne (minti 3)

- Yi bayanin cewa za ka/za ki faɗi wani jawabi. Idan jawabin daidai ne, ɗalibai su ɗaga babban yatsansu a sama. Idan jawabin ba daidai ba ne, ɗalibai su nuna babban yatsansu a ƙasa.
- **Ka/ki ce:** *100 ta ɗara 20 yawa. Daidai ne ko kuskure ne? 654 ta ɗara 100. Daidai ne ko kuskure ne?*

## Koyo

Gabatar da lambar da ta gaza wata da kuma lambar da take daidai da wata (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu nuna lambobin da suka gaza wasu yawa ko kuma waɗanda suke daidai da su. Idan lamba ɗaya ta gaza ɗaya yawa, yana nufin tana da ƙarancin kima. Idan lambobi biyu suka kasance daidai da juna, yana nufin lambobin iri ɗaya ne.*
- A kira ɗalibai 20 su zo gaban aji, sai a raba su a rukuni gida biyu na; rukunin, mutum 1 da kuma rukunin mutane 19. Ka/ki ƙirga yawan ɗaliban dake cikin kowane rukunin a bayyane sannan sai ka/ki rubuta adadin yawan lambarsu a kan allo. Nemi ɗalibai su faɗi wane rukuni daga cikinsu ya ɗara wani yawan ɗalibai.
- **Ka/ki ce:** *Rukunin dake da ɗalibai 1 shi ne ya gaza a yawa, saboda 1 ba ta kai yawan 19 ba. Ku tuna, alamar > koyaushe tana nufin lambar da ta fi yawa, saboda haka wace hanya alamar ya kamata ta nuna?*
- A kira wani ɗalibi ya zo gaban allo, a nemi ya cike wannan alamar: 1 ____ 19.
- **Ka/ki ce:** *Rukunin da ke da ɗalibi guda 1 shi ne ya gaza a yawa, saboda 1 ta gaza 19.*
- Daga nan, sai ka/ki raba rukunin ɗaliban zuwa gida goma-goma. Ka/ki karanta lambar ɗaliban kowane a bayyane sannan ka/ki rubuta 10 = 10 a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Yayin da aka samu lambobi biyu iri guda, muna amfani da alamar daidai da.*
- A maimaita matakan da wasu lambobi na ɗaruruwa da gwammai da kuma ɗaiɗai. A yi amfani da layin lamba ko jadawalin lambobi domin gwajin amsarka/ki.

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai bibbiyu: Nuna lambar da ta ɗara da lambar da ta gaza ko kuma daidai da (minti 15)

- A umurci ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 26.
- A karanta umurnin da kuma tambayar farko a bayyane ga ɗalibai. A nemi dalibai su kammala matsalar farko a cikin littafansu na rubutu. Suna iya duba amsarsu da ta abokan zamansu.
- A zagaya ana lura da ɗalibai, a kuma taimaka musu. A yayin zagayawar, a tambayi dalibai yadda suka samo amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.
- Idan da lokaci, a nemi ɗalibai su kammala lissafi na gaba a cikin shafin.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ƙwazonsu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 26 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

| Na. 53 | Zango na 1, Mako na 11, Darasi na C |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya tsara lambobin ta sigar yadda suke ƙaruwa.
**Kayan Aiki:** Katunan lambobi 1-1000 **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.


A yi Wasan Ɗaga Babban Yatsa Sama ko Ƙasa (minti 3)

- A nemi ɗalibai su amsa kowace daga cikin waɗannan tambayoyin ta hanyar ɗaga babban yatsansu ya kalli sama ko kuma ya kalli ƙasa.
- **Ka/ki ce:** *"Idan muna son ƙirge daga 5 zuwa 260 shin sama za mu yi ko ƙasa?" "111 zuwa 11, sama ne ko ƙasa?"*

## Koyo

Gabatar da tsara lambobi ta sigar yadda suke ƙaruwa (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu tsara lambobi ta sigar yadda suke ƙaruwa. Sigar yadda suke ƙaruwa na nufin lambobin su fara daga lambobi na ƙasa zuwa lambobi na sama. Duk lambar dake a kan tsarin ta ɗara wadda take bayan ta.*
- A kira ɗalibai uku su zo gaban aji. A baiwa kowanensu dama ya zaɓi katin lamba ɗayasannan sai a sa su tsaya a cikin layi, su ɗaga katin lambar sama, suna kallon sauran 'yan ajin.




- A nemi ɗalibai su karanta lambobin a bayyane.
- **Ka/ki ce:** *Wace lamba ce ta fi ƙakanta? Wadda ta fi ƙakanta sai ta koma gefen hagu. Wace lamba ce ta gaba idan aka bi tsari? Wace lamba ce ta fi girma? Wannan lambar sai ta koma gefen dama.*
- A taimakawa ɗalibai su jera kansu a kan tsari daga ƙaramar lamba zuwa babba, suna cigaba da ƙara lambobin.
- A maimaita da wasu ɗalibai daban da kuma wasu katunan lamba na daban.

## Gwaji

Aikin ƙaramin rukuni: Tsara lambobi ta sigar yadda suke ƙaruwa (minti 10)

- A sa ɗalibai su zauna a cikin ƙananan rukunai. A zaɓi jagora 1 ga kowane rukuni wanda zai taimaka wajen rarraba katunan lamba guda 5 ga kowane rukuni. A aje dukkan katunan a rufe a tsakiyar rukunan.
- A yi wa ɗalibai bayanin cewa za su buɗe katunan lamba gudu uku, sannan su yi aiki tare su tsara su ta sigar yadda suke ƙaruwa.
- A zagaya ana lura da ɗalibai, a kuma taimaka musu.
- Daga nan sai a nemi ɗalibai su sake buɗe wani kati, su gano wurin da ya dace a sanya shi bisa tsari tare da sauran katunan uku.
- A maimaita sa ɗalibai su buɗe kati na biyar.
- A zagaya ana lura da ɗalibai, a kuma taimaka musu. A yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai yadda suka samo amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.

## Bayyanawa

Gwajin aikin gida (minti 10)

- A buɗe littafin ɗalibai shafi na 27 sannan a karanta umurnin ciki.
- A yi aiki na farko tare da ɗalibai a aji. Ɗalibai su juyi aikin a cikin littafan rubutunsu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 27 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

| Na. 54 | Zango na 1, Mako na 11, Darasi na D |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya tsara lambobin ta sigar yadda suke raguwa.
**Kayan Aiki:** Katunan lambobi 1-1000 **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)


- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

A yi Wasan Ɗaga Babban Yatsa Sama ko Kasa (minti 3)

- A umurci ɗalibai su amsa kowace daga cikin waɗannan tambayoyin ta hanyar ɗaga babban yatsansu ya kalli sama ko kuma ya kalli ƙasa.
- **Ka/ki ce:** *"Idan muna son yin ƙirge daga 800 zuwa 100 shin sama za mu yi ko ƙasa?" "60 zuwa 61, sama ne ko ƙasa?"*

## Koyo

Gabatar da tsara lambobi ta sigar yadda suke raguwa (minti 10)




- **Ka/ki ce:** *A yau za mu tsara lambobi ta sigar yadda suke raguwa. Sigar yadda lambobi suke raguwa na nufin lambobin su fara daga lambobi manya zuwa lambobi ƙanana. Duk lambar dake a kan tsarin ta gaza wadda take gabanta.*
- A kira ɗalibai uku su zo gaban aji. A baiwa kowanensu dama ya zaɓi katin lamba ɗaya sannan sai a sa su tsaya a cikin layi, su ɗaga katin lambar sama, suna kallon sauran 'yan ajin.
- A umurci ɗalibai su karanta lambobin a bayyane.
- **Ka/ki ce:** *Wace lamba ce ta fi girma? Wadda ta fi ƙaƙanta sai ta koma gefen hagu. Idan muna jera lambobi ta sigar yadda suke raguwa. Wace lamba ce ta gaba idan aka bi tsari? Wace lamba ce ta fi ƙaƙanta? Wannan lambar sai ta koma gefen dama.*
- A taimakawa ɗalibai su jera kansu a kan tsari daga babbar lamba zuwa ƙarama, suna cigaba da rage kimar lambobin.
- A maimaita da wasu ɗalibai daban da kuma wasu katunan lamba na daban.

## Gwaji

Aikin ƙaramin rukuni: Tsara lambobi ta sigar yadda suke raguwa (minti 10)

- A sa ɗalibai su zauna a cikin ƙananan rukunai. A zaɓi jagora 1 ga kowane rukuni wanda zai taimaka wajen rarraba katunan lamba guda 5 ga kowane rukuni. A aje dukkan katunan a rufe a tsakiyar rukunan.
- A yi wa ɗalibai bayanin cewa za su buɗe katunan lamba gudu uku, sannan su yi aiki tare, su tsara su ta sigar yadda suke raguwa.
- A zagaya ana lura da ɗalibai, a kuma taimaka masu. Daga nan sai a nemi ɗalibai su sake buɗe wani kati, su gano wurin da ya dace a sa shi bisa tsari tare da sauran katunan uku.
- A maimaita sa ɗalibai su buɗe kati na biyar.
- A zagaya ana lura da ɗalibai, a kuma taimaka musu. A yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai yadda suka samo amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.

## Bayyanawa

Gwajin aikin gida (minti 10)

- A buɗe littafin ɗalibai shafi na 28 sannan a karanta umurnin ciki.
- A yi aiki na farko tare da ɗalibai a aji. Ɗalibai su juyi aikin a cikin littafan rubutunsu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 28 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

# Na. 55 | Zango na 1, Mako na 11, Darasi na E


**Manufofi:** Ɗalibai za su yi bita da gwajin abun da suka koya a cikin wannan makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

A yi Wasan Lambar da ta Ɗara da Lambar da ta Gaza (minti 5)



- A rubuta lambobin a kan allo. A sa ɗalibai su amsa kowace daga cikin waɗannan tambayoyin ta hanyar ɗaga babban yatsansu sama (ga lambar da ta ɗara yawa da) ko kuma nuna babban yatsansu ya kalli ƙasa (ga lambar da ta gaza ga yawa), ko kuma alamar daidai da (ga lambar da suke daidai)
- 100 ___ 2 ; 100 ___ 200 ; 200 ___ 200
- Idan da lokaci, ka/ki cigaba da ƙarin wasu misalai.

### Koyo

Bita da maimai (minti 8)

- A zaɓi wani darasi daga cikin darussan da aka yi a cikin makon, wanda ake ganin ɗalibai ba su fahimce shi sosai ba. A sake koyar da darasin ko a sake koyar da shi ta wata sabuwar hanya daban.

### Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai a cikin rukuni : Zane da kuma rubutu (minti 15)

- A baiwa ɗalibai aikin da zai taimaka musu wajen yin gwajin darasin da aka yi bita (alal misali; tsara lambobi har zuwa 999. Ɗalibai suna iya yin aiki ɗaiɗaikunsu ko kuma a cikin ƙananan rukunai.
- Yayin da ɗalibai suke gudanar da wani aikin da aka ba su, a ƙara taimaka musu a inda ba su gane sosai ba.

### Bayyanawa

Bita da kuma bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala a lokacin Gwaji.

### Aikin Gida

A baiwa ɗalibai aikin gida na bita da kuma gwajin ƙwazonsu.

| Na. 56 | Zango na 1, Mako na 12, Darasi na A |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su yi taƙaitacciyar jarrabawar gwaji ta lissafi.
**Kayan Aiki:**

## JARRABAWAR GWAJI

A yi wa ɗalibai jarrabawar gwaji ta kai-tsaye da kuma rubuta makin da suka samu a cikin littafin ajiye bayanai. Idan akwai buƙata, ka nemi taimakon shugaban makaranta da SBMC ko kuma wasu malamai domin gudanar da jarrabawar.

A bayar da wani aikin gwaji ga ɗalibai yayin da suke jiran a fara jarrabawar gwajin. Alal misali ɗalibai za su gwada nuna matsayin lambobi zuwa 999.

| **Jaha:** | | **Karamar hukuma:** | | **Makaranta:** | | **Wata:** | | **Shekara:** | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|

| Lamba | Sunan Ɗalibi | Jinsi | Shekaru | Buƙata ta musamman (Eh/A'a) | Lambar da ta ɓata | Wakilcin Lambobi | Wakilcin lamba a cikin jerin lambobi | Jimillar maki |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| | | | | | /4 | /9 | /2 | / 15 |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |
| | | | | | | | | |


## Darasin Lissafi Aji 2, Zango na 1, Mako na 12 – Jarrabawar karshen Zango


**Cike gurbin da babu lamba**. (A bayar da maki biyu ga kowace amsa)


**65, 66, 67, 68 ____, 70**

**25, ___, 35, 40, 45, 50**

**Faɗi lambar da kowane hoto yake wakilta**. (A bayar da maki uku ga kowace amsa. Jimillar maki 9 kenan)




**Faɗi darajar kowane lambar da take gidan goma a kowane rukuni.** (A bayar da maki ɗaya ga kowace amsa)

**356** **191**

| Na. 57 | Zango na 1, Mako na 12, Darasi na B |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su yi bitar ƙirge zuwa 200.
**Kayan Aiki:** Jadawalin Lambobi 1-100 da ƙwallon takarda **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

A yi Wasan Sunan Lamba (minti 3)

- A rubuta wata lamba daga 1 zuwa 200 a kan allo. A nemi ɗalibai da su faɗi sunan lambar. A maimaita sau da yawa.

## Koyo

Kirge zuwa 200 da bibbiyu da biyar-biyar da kuma goma-goma (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu yi bitar ƙirge zuwa 200 da bibbiyu da biyar-biyar da kuma goma-goma.*
- A yi ƙirgen tsallake da bibbiyu a fara daga 0 zuwa 200 yayin da ake nuna lambar daga jadawalin lambobi. Ka/ki nemi ɗalibai da ku yi ƙirgen tare da su.
- A maimaita ƙirgen da biyar-biyar da kuma goma-goma. Ka/ki nemi ɗalibai su yi ƙirgen tsallaken tare da abokan zamansu.
- A tambayi ɗalibai su faɗi wane ya fi sauƙi da kuma wane ya fi wahala gare su.

## Gwaji

Wasan aji gaba ɗaya: Kirge zuwa 200 da bibbiyu da biyar-biyar da kuma goma-goma (minti 15)

- A yi bayanin dokokin wasan ga ɗalibai. A sa ɗalibai su tsaya a cikin da'ira sai a ba su wata takarda da aka naɗe kamar ƙwallo. Ka/ki gaya musu cewa "dankali ne mai zafi" saboda haka ka da su riƙe shi ya daɗe a hannunsu saboda yana iya "ƙona" su. A fara daga 2, duk wanda ya kama ƙwallon sai a kara wasu 2 ga jimillar abin da aka faɗi sannan ya jefa ƙwallon ga wani ɗalibi daban. Idan wani ya kasa ba da amsar to rukunin gaba ɗaya za su koma farko, su sake ƙirgen daga 2, su fara daga ɗalibin da ya kasa ba da amsar.
- A fara da wata lamba sai a yi ƙirgen da bibbiyu har a kai 200. Daga nan sai a sake maimaitawa, a wannan karon sai a yi ƙirgen da biyar-biyar ko kuma goma-goma.
- Idan ɗaliban sun iya gudanar da wannan tsarin cikin sauƙI, a nemi su jefa ƙwallon ga junansu ba bisa wani tsari ba.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A faɗi wata lamba daga 1-200 a bayyane.
- A sa ɗalibai su rubuta lambar a cikin littafansu na aiki..
- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu sama, su nuna abun da suka rubuta. A yaba wa ƙwazonsu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su yi gwajin yin ƙirge da bibbiyu da biyar-biyar da kuma goma-goma zuwa 200 a gida.

| Na. 58 | Zango na 1, Mako na 12, Darasi na C |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi amfani da gidajen ɗaruruwa da gidajen gwammai da kuma gidajen ɗaiɗai su nuna kimar lamba har zuwa 999.
**Kayan Aiki:** Karamar jakar wake da tsakuwoyi 1 da katunan lamba 1-9. **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)


- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfaa masu gwiwa.

Ni wace lamba ce? (minti 3)

- A karanta kowane daga cikin waɗannan jawaban. A nemi ɗalibai su ba da amsa ta faɗin lambar a bayyane.
- **Ka/ki ce:***Ni dami 5 ne na ɗaurin goma-goma da kuma ɗaiɗai guda 2? Ni wace lamba ce?*
- **Ka/ki ce:** *Ni dami 9 ne na ɗaurin goma-goma da ɗaiɗai 0. Ni wace lamba ce?*
- **Ka/ki ce:***Ni dami 1 ne na ɗaurin ɗari da dami 5 na ɗaurin goma-goma. Ni wace lamba ce?*

**Koyo**

Bitar kimar lamba zuwa 200 (minti 10)




- A zana hoton gidajen ɗaruruwa da gidajen gwammai da kuma gidajen ɗaiɗai a kan allo.
- A nemi ɗalibai uku su zo gaban aji kownnensu ya zaɓi katin lamba guda ɗaya. Za su tsaya a cikin layi, kowannensu a gaban gida ɗaya, sai su ɗaga katin lambar sama, ta yadda ajin za su iya ganin lambobin.
- A yi musu bayanin cewa kowane ɗalibi yana tsaye ne a gaban kimar lamba daban. Daga hagu zuwa dama, ɗalibi ɗaya yana tsaye a gurbin gidan ɗaruruwa da ɗalibi ɗuda a gurbin gidan gwammai, sai ɗalibi ɗaya a gurbin gidan ɗaiɗai.
- A nemi ajin ya faɗi lambar da aka samar a bayyane sai a rubuta lambar a kan allo.
- A maimaita aikin da ƙarin wasu ɗalibai uku.
- Dukkan ɗaliban su kwatanta lambobin don su gano wace lamba ce ta ɗara wata yawa.

**Gwaji**

Aiki a cikin ƙaramin rukuni: Cankar Lamba (minti 10)

- A sa ɗalibai su zauna a cikin ƙananan rukunai. A sa ɗalibai su zana hoton gidajen ɗaruruwa da gidajen gwammai da kuma gidajen ɗaiɗai a cikin littafansu na rubutu.
- A ɗaga jakar wake da tsakuwoyi a sama, sai a tambayi ɗalibai su canka ƙwara nawa ne a cikin jakar. Su rubuta cankar da suka yi a ɗaiɗaikunsu a gurbin gidajen ɗaruruwa da gidajen gwammai da kuma gidajen ɗaiɗai.
- Bayan dukkan ɗaliban sun gama canken nasu, su tattauna da junansu cewa canken wa ya fi ɗara wa kuma canken wa ya gaza.
- Daga ƙarshe, a faɗi ainihin jimillar adadin waken ko tsakuwoyin ta hanyar rubuta lambar a kan allo.

**Bayyanawa**

Gwajin aikin gida (minti 10)

- A buɗe littafin ɗalibai shafi na 29 sannan a karanta umurnin dake ciki.
- A yi aiki na farko tare da ɗalibai a aji. Ɗalibai su juyi aikin a cikin littafan rubutunsu.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 29 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.


| Na. 59 | Zango na 1, Mako na 12, Darasi na D |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su rubuta lambobi 1 zuwa 1,000.
**Kayan Aiki:** Katunan lamba 1 zuwa 9 **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfa masu gwiwa.




Wasan Canken lamba (minti 3)

- A nemi ɗalibai su yi canken faɗin nawa ake sayar da babban burodi ɗaya .
- A nemi ɗalibai 2 ko 3 su bayyana canken da suka yi ga aji ta hanyar rubuta lambar a cikin jadawalin kimar wurin lamba.
- A gaya wa ɗalibai ainihin jimillar yawan kuɗin, don su ga yadda za su kwatanta da canken da suka yi.

## Koyo

Rubuta kimar  lamba tsakanin lamba 1 zuwa 999 (minti 10)

- A nemi ɗalibai su zo gaban aji, kowannensu ya zaɓi katin lamba guda ɗaya. Za su tsaya a kan layi su nuna katunan lambobinsu ga ajin baki ɗaya.
- A yi bayanin cewa kowane ɗalibi yana wakiltar wani kimar  lamba ne na daban. Mun san tsarin, saboda tsarin da suka tsaya a kansa. Ɗalibi ɗaya a gurbin gidan ɗaruruwa, ɗalibi ɗaya a gurbin gidan gwammai sannan kuma ɗalibi ɗaya a gurbin gidan ɗaiɗai.
- A kira ɗalibi ɗaya ya zo gaban aji ya rubuta lambar da take daidai a gidajen ɗaruruwa da gidajen gwammai da kuma gidajen ɗaiɗai.
- A maimaita aikin, tare da neman ɗalibai su sauya tsarin da suka tsaya a kansa ko su zaɓi wasu katunan lamba na daban domin su samar da wata lamba daban.

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai bibbiyu: Rubuta lambobi (minti 15)

- A nemi ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai a Shafi na 30.
- A karanta umurnin da kuma tambayar farko a bayyane ga ɗalibai.
- A nemi dalibai su kammala matsalar a cikin littafansu na aiki ta hanyar rubuta lambar da kowane damin ɗaruruwa da damin gwammai da kuma damin ɗaiɗai yake wakilta.
- A zagaya ana lura da ɗalibai. A yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai yadda suka samo  amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.
- Idan da lokaci, a nemi ɗalibai su kammala lissafi na gaba a cikin shafin.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ƙwazonsu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 30 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

| Na. 60 | Zango na 1, Mako na 12, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su nuna kimar  lamba har zuwa 999 sannan su nuna lambar da ta fi ɗara girma da kuma lambar da ta fi gaza girma.

**Kayan Aiki:** Katunan lamba **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfa masugwiwa.

Wasan Kirge (minti 2)

- A yi wa ɗalibai bayanin cewa za a faɗi wata lamba. Da zarar an faɗi lambar, sai su fara ƙirge daga lambar da goma-goma da sauri. Alal misali, idan aka ce "900," ɗalibai sai su fara faɗin "900, 910, 920, 930..."
- Bayan 'yan daƙiƙai kaɗan, sai a ce "su tsaya." Daga nan sai a sake maimaita wannan tsarin da wata sabuwar lamba.

**Koyo**

Bitar lambar da ta ɗara da lambar da ta gaza da kuma lambar da take daidai da wata har zuwa lamba ta 999 (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu nuna lambobin da suka ɗara wasu da waɗanda suka gaza wasu da kuma lambobin da suke daidai da wasu lambobin.*
- A kira ɗalibai shida su zo gaban aji kowanensu ya zaɓi katin lamba guda daya. Za su ɗaga katin lambobinsu sama ta yadda duk sauran ajin za su ga lambobin da suka zaɓa.
- A sa ɗalibai su raba kansu a cikin rukunai guda uku, domin su samar da lambobi bibbiyu daban-daban na ɗaruruwa.
- A gwada lambobin a gurbin ɗaruruwa da gurbin goma-goma da kuma gurbin ɗaiɗai don a taimakawa ɗalibai su iya gane lambar da ta ɗara wata.
- A maimaita aikin da wasu ɗalibai, ana sa ɗalibai suna sassauya muhallin da suke tsaye don a samar da wasu sababbin lambobin da za a kwatanta.

**Gwaji**

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai bibbiyu: Nuna lambar da ta ɗara girma da lambar da ta gaza ko kuma wadda take daidai da wata (minti 15)

- A nemi ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai a Shafi na 31.   A karanta umurnin da kuma tambayar farko a bayyane ga ɗalibai a kuma taimakawa dalibai su kammala tambayar farko.
- A zagaya ana lura da ɗalibai, a kuma taimaka musu. A yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai yadda suka samo amsar ta su, a kuma duba ko sun amsa daidai.
- Idan da lokaci, a nemi ɗalibai su kammala lissafi  na gaba a kan shafin da kansu. Suna iya duba amsarsu da ta abokan zamansu.

**Bayyanawa**

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga littafansu sama, su nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ƙwazonsu.

**Aikin Gida**


A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 31 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

| Na. 61 | Zango na 2, Mako na 1, Darasi na A |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya nuna ½ na rukunin wasu abubuwa.
**Kayan Aiki:** Ayaba (ko duk wani abu da ake iya rabawa gida biyu), takarda da aka raba gida biyu mai samfurin da aka naɗa, aka raba ta gida biyu (da'ira da fasali mai sifar akwati a kuma fasali mai sifar gidan dara) **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 3)




- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Labari da Hotuna (minti 2)

- Bayyana labarin hotuna a kan allo. Ali da Audu sun tafi kasuwa. Sun iske mai sayar da kayan marmari yana da ayaba guda ɗaya kacal da ta rage masa. Da farko Ali da Audu sun yi muhawarar wanda za a sayar wa ayabar daga cikinsu. Daga baya, sai suka yanke shawarar cewa za su raba ayabar daidai su biyu.
- A kira ɗalibai guda biyu, su zo gaban aji su yi gwajin kwaikwayon labarin. Idan akwai ayaba ta gaskiya, ka/ki ba su su raba tsakaninsu.

## Koyo

Gabatar da Kaso ɗaya: ½ (minti 10)



- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi wani abu game da kaso ɗaya, na rabin abu ɗaya. An raba ayabar gaba ɗaya gida biyu daidai. Kowane kaso ɗayaana kiransa da rabi, wanda ke nufin kaso biyu waɗanda girmansu yake daidai.*
- A zana sifar akwati mai kusurwa huɗu (ractangul) a kan allo, sai a zana layi tsakiyar sifar daga sama zuwa ƙasa, sannan sai a tusa kaso ɗaya ya yi duhu.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu muna da cikakken sifar akwati mai kusurwa huɗu (ractangul). Idan aka raba shi gida biyu, za mu samu kaso biyu waɗanda girmansu ɗaya. Na saka kala ga rabin sifar akwati mai kusurwa huɗu (ractangul).*
- A rubuta lamba 1 a kan allo. A ja layi a ƙasan lambar.
- **Ka/ki ce:** *Ina da rabi guda biyu, ko kuma kaso biyu, jimilla.*
- A rubuta lamba ta '2' a kan allo a ƙasan layin.
- **Ka/ki ce:** *A kaso na 1/2, lambar dake sama tana nuna mana kason da muke da su gaba ɗaya. Lambar da take ƙasa kuwa tana nuna jimillar yawan kaso da muke da su waɗanda girmansu yake iri ɗaya. Saboda haka, muna nuna kason mu na ½ ta hanyar rubuta 1 bisa 2.*
- A maimaita da wasu sifofin kamar sifar akwati da da'ira da kuma fasalin dala.

## Gwaji

Wasan aji gaba ɗaya: A nemo rabi (minti 15)

- A gaya wa ɗalibai cewa kowannensu zai samu rabin wani sifa. Su nemi wani ɗalibi wanda yake da sauran rabin cikon sifar. A tunawa ɗaliban cewa rabin sifar da za su nema ya kasance daidai sifar nasu.
- Bayan kowane ɗalibi ya gano sauran rabin sifar nasa, a sa dukkan ɗalibai su tsaya su bibbiyu. Ɗaliban su haɗa sifofinsu wuri ɗaya domin su samu cikakken sifa ɗaya. Su faɗawa junansu sunan sifar tasu.
- A zagaya ana lura da aikin ɗaliban. A yayin zagayawar, ka/ki tambayi ɗaliban ko sun gane waɗanne sifofi ne ake iya haɗawa a samu cikakken sifa ɗaya. A duba ko sun amsa daidai.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A ɗaga wata surar 1/2 sama. A nemi dukkan ɗalibai dake da rabin cikon surar da su ɗaga surarsu a sama, sannan su faɗi sunan surar a bayyane. A maimaita da sauran rabin surorin.


## Aikin Gida

A sa ɗalibai su zana hoton sura mai kusurwa huɗu a cikin littafansu na rubutu sannan su sanya kala ga rabinta.

| Na. 62 | Zango na 2, Mako na 1, Darasi na B |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya nuna ¼ na rukunin wasu abubuwa.
**Kayan Aiki:** Lemo (ko wani abu da ake iya rabawa gida huɗu) samfurin takardar da aka naɗa, aka raba a cikin kaso 1/4 (da'ira da sifar akwati da sifar gidan dara) **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi




Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Labari da Hotuna (minti 3)

- Bayyana labarin hotuna a kan allo. Ɗalibai huɗu sun tafi kasuwa. Sun iske mai sayar da kayan marmari yana da lemo guda ɗaya da ya rage mashi. Da farko, duk sun yi muhawarar wanda za a sayar wa lemun daga cikinsu. Daga baya, sai suka yanke shawarar cewa za su raba lemun daidai su huɗu.
- A kira ɗalibai guda huɗu, su zo gaban aji su yi gwajin kwaikwayon labarin. Idan akwai lemu na gaskiya, ka/ki ba su su raba tsakaninsu.

## Koyo



Gabatar da Kaso ɗaya: ¼ (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi wani abu game da kaso ɗaya, bisa huɗu.*
- A zana hoton da'ira a kan allo, sai a zana layin da zai raba ta gida biyu daidai. Daga nan sai a kuma zana wani layi da zai raba da'irar zuwa gida huɗu.
- A nemi wani ɗalibi ya zo gaban aji ya tusa kashi ¼ na da'irar da kala.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu an raba cikakkiyar da'irarmu zuwa kaso huɗu waɗanda duk girmansu ɗaya. An cike ¼ na da'irar.*
- A rubuta lamba 1 a kan allo. A ja layi a ƙasan lambar. Daga nan sai a rubuta lamba 4 a ƙasan layin.
- **Ka/ki ce:** *A kaso guda na ¼, lambar dake sama tana nuna muna kaso da muke da su gaba ɗaya. Lambar dake ƙasa kuwa tana nuna muna jimillar yawan kaso da muke da su waɗanda girmansu yake iri ɗaya.*
- A maimaita da wasu sifofi kamar sifar gidan dara da da'ira da sifar akwati ko kuma sifar lu'u'lu'u.

## Gwaji

Wasan aji gaba ɗaya: Nemo Cikakkiyar Surar Gaba Ɗaya (minti 15)

- A gaya wa ɗalibai cewa kowanensu zai samu ¼ na wata sifa. Su nemi wasu ɗalibai guda uku wanɗanda suke da sifa iri guda da su. Bayan kowane ɗalibi ya gano sauran cikon sifar guda huɗu, a sa ɗalibai su tsaya tare. Su ɗaga sifofinsu wuri guda, domin su samu cikakkiyar sifa ɗaya, mai ɓangarori guda 4.
- A nemi rukunin mutane 4 su zo gaban aji su haɗa kansu wuri ɗaya, su nuna ¼ (ɗalibi ɗayaya tsaya gefe daban da sauran ɗaliban). Daga nan sai, a nemi rukunin su tsara kansu yadda za su nuna ½ (ɗalibai biyu su tsaya gefe daban da sauran ɗaliban). A tambayi 'yan aji su faɗi wane ɓangare ne ya fi wani girma.
- Idan da lokaci, a maimaita da wani rukunin ɗalibai.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A ɗaga wani sifar 1/4 sama. A nemi dukkan ɗalibai dake da ɗaya bisa huɗu na cikon sifar da su ɗaga sifofinsu sama, sannan su faɗi sunan fasalin a bayyane. A maimaita da wasu sauran sifofin.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su zana hoton sifar akwati a cikin littafansu na rubutu sannan su sanya kala ga kashi ɗaya bisa huɗu na sifar.


Na. 63

# Zango na 2, Mako na 1, Darasi na C

**Manufa:** Ɗalibai za su iya nuna ¾ na rukunin wasu abubuwa.
**Kayan Aiki:** Lemo (ko wani abu da ake iya rabawa a cikin gida huɗu) **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)



- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Labari da Hotuna (minti 5)

- Bayyana labarin hotuna a kan allo. Ɗalibai huɗu sun tafi kasuwa. Sun iske mai sayar da kayan marmari yana da lemo guda ɗaya kacal da ya rage masa. Da farko, duk sun yi muhawarar wanda za a sayar wa lemun daga cikinsu. Daga baya, sai suka yanke shawarar cewa za su raba lemun daidai su huɗu. Kowannensu ya samu ¼ na lemun. Daga nan sai ga wani kare dake jin yunwa ya zo wurin sai ya ɗauke kashi ɗaya. Yanzu, an bar kashi uku kawai da suka rage!
- A kira ɗalibai guda huɗu, su zo gaban aji su yi gwajin kwaikwayon labarin. Idan akwai lemu na gaskiya, ka/ki ba su su raba tsakaninsu. Idan babu shi, a ba su sifar da'ira, su raba cikin gida huɗu.
- A yi wa ɗaliban bayanin cewa kowane ɗalibi yana da kason ¼ na lemun. Amma bayan da kare ya cinye kashi 1/4, an bar kaso guda 3 ne kawai. Wannan yana nufin akwai kashi ¾ na lemun kawai da ya rage. A rubuta kowane daga cikin kason a kan allo, yayin da ka/kike yin bayaninsu.

## Koyo


Gabatar da kaso ɗaya: 3/4 (minti 8)




- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi wani abu game da kaso ɗaya, na ¾. Wannan yana nuna akwai jimillar kaso huɗu waɗanda duk girmansu ɗaya, amma uku kawai ne aka tusa da baƙi.*
- A zana hoton surar da'ira a kan allo, sai a raba ta cikin gida huɗu.
- **Ka/ki ce:** *Muna da cikakkiyar da'ira ɗaya. Amma idan aka raba ta zuwa gida huɗu, za mu samu kaso hudu waɗanda duk girmansu ɗaya.*
- A saka lambobi ga kowane kaso, 1, 2, 3, 4 sai ka/ki ƙirga kowane kaso tare da ɗalibai a bayyane. Daga nan sai ka/ki tusa kaso guda uku na da'irar da baƙi.
- A rubuta lamba 3 a kan allo. A ja layi a ƙasan lambar. Daga nan sai a rubuta lamba 4 a ƙasan layin.
- **Ka/ki ce:** *A kaso ɗaya na ¾ , lambar dake sama tana nuna mana kason da muke da su gaba ɗaya. Lambar dake ƙasa kuwa tana nuna muna jimillar yawan kason da muke da su waɗanda girmansu yake iri guda.*
- A maimaita da wasu sifofi kamar; sifar gidan dara da kuma sifar lu'u'lu'u ko rukunin wasu sifofi.

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai bibbiyu: Zane (minti 15)



- A zana sifar akwati da sifar da'ira a kan allo.
- A nemi ɗalibai su rubuta sifofin a cikin littafansu na rubutu, su kuma tusa kashi ¾ na kowace daga cikin sifofin da baƙi.
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai a kuma taimaka musu.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga littafansu na rubutu sama, su nuna abun da suka sanya wa kala.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su zana hoton sifar gidan dara a cikin littafansu na aiki sannan su sanya kala ga ƙabinsa.

| Na. 64 | Zango na 2, Mako na 1, Darasi na D |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya rarrabewa tsakanin ¼ da ½ da kuma ¾
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)


- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Naɗe Rabi-rabi da kuma Kashi Ɗaya bisa Huɗu (minti 3)

- A sa ɗalibai su ɗauko fallen takarda guda ɗaya. A nunawa ɗalibai yadda ake naɗe takardar a rabi. Sannan sai a sa ɗalibai su buɗe takardar su gani idan kowane rabin daidai yake da ɗan'uwwansa.
- Da zarar an naɗe takardar a rabinta, a nunawa ɗalibai yadda za su sake naɗe ta, su samu ninki huɗu. A sa ɗalibai su buɗe takardunsu, sai su rubutawa kowane ɓangare na kason mai sifar gidan dara lambobi 1, da 2 da 3 da 4 domin su nuna kowane ɓangaren takardar 4 da girmansu yake daidai.

## Koyo


Rarrabewa tsakanin Ɓangarorin: ¼, ½, ¾ (minti 10)




- **Ka/ki ce:** *A wannan makon mun koyi yadda ake gane ɓangare guda na ½ da ¼ da kuma ¾.*
- A zana hoton da'ira sannan sai a raba da'irar cikin ɓangarori guda biyu waɗanda girmansu ɗaya. A yi wa kowane ɓangare daga cikinsu rubutu.
- **Ka/ki ce:** *Muna da da'ira guda gaba ɗaya. Idan aka raba ta gida biyu, za mu samu ɓangarori guda biyu waɗanda girmansu iri* ɗaya.
- A tusa rabin ɓangaren da'irar da kala.
- **Ka/ki ce:** *Na sanya kala ga rabin da'ira ta. Ɓangare na shi ne ½.*
- A rubuta ɓangaren a ƙasan da'irar. Daga nan sai a sake maimaita tsarin domin a nuna ɓangaren ¼ da kuma ¾.
- **Ka/ki ce:***Idan aka kalli waɗannan hotunan guda uku za alura da, ¼ shi ne mafi ƙarancin wurin da aka tusa da baƙi. ½ kuwa ya fi ¼ yawa amma bai kuma kai yawan ¾ ba. ¾ shi ne kason da ya fi kowane yawa.*

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai bibbiyu: Zana Hoton Kashi ¾ (minti 10)




- A zana kaso mai sifar gidan dara guda uku a kan allo sannan a rubutawa kowannensu A, B da kuma C.
- A umurici ɗalibai su rubuta siffofi a cikin littafansu na rubutu.
- A umurci ɗalibai su tusa kashi ¼ na siffofi mai sifar gidan dara na A da ½ na fasali mai sifar gidan dara na B da kuma ¾ na soffofi mai sifar gidan dara na C. Ɗalibai na iya duba amsarsu da ta abokan zamansu.
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai a kuma taimaka musu.
- A nemi ɗalibai su faɗi wane daga cikin kaso masu sifar daira ne ke da yawan ɓangarensa da aka tusa da baƙi kuma wane ne yake da mafi ƙaranci.
- **Ka/ki ce:** *Fasali mai sifar gidan dara na A yana da kashi ¼ da aka tusa. Wannan shi ne mafi ƙarancin inda aka tusa da baƙi, saboda haka kashi ¼ shi ne mafi ƙarancin ɓangaren. A kaso mai sifar gidan dara na B, an tusa kashi 1/2. Wanda ya fi ¼ yawa amma kuma bai kai yawan ¾ ba. Kason ¾ shi ne ya fi kowane yawa.*

## Bayyanawa

Gwajin aikin gida (minti 10)

- A buɗe littafin ɗalibai shafi na 32 sannan a karanta umurnin ciki.
- A yi aiki na farko tare da ɗalibai a aji. Ɗalibai su kwafi j aikin a cikin littafan rubutunsu.

## Aikin Gida



A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 32 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.


| Na. 65 | Zango na 2, Mako na 1, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi bita da gwajin abun da suka koya a cikin wannan makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.




Wasan Daidai ne ko Kuskure ne (minti 8)

- A zana hoton wasu siffofi a kan allo. Yi wa ɗalibai bayanin cewa za ka/za ki faɗi wasu jawabai guda uku. Ga kowane daga cikin jawaban, ɗalibai su ɗaga babban yatsansu sama idan jawanin daidai ne su kuma nuna babban yatsansu ƙasa idan jawabin kuskure ne.
- **Ka/ki ce:** *A na nuna ¼. Daidai ne ko Kuskure ne?*
- **Ka/ki ce:** *B na nuna ¾. Daidai ne ko Kuskure ne?*
- **Ka/ki ce:** *C na nuna ¾. Daidai ne ko Kuskure ne?*

**Koyo**

Bita da maimai (minti 5)

- A zaɓi wani darasi daga cikin darrusan da aka yi a cikin makon, wanda ake ganin ɗalibai ba su fahimce shi sosai ba. A sake koyar da darasin ko a sake koyar da shi ta wata sabuwar hanya ta daban.

**Gwaji**

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai a cikin rukuni: Zane da kuma rubutu (minti 15)

- A ba ɗalibai aikin da zai taimaka masu wajen yin gwajin darasin da aka yi bita (alal misali; su bambanta tsakanin kaso ½ da ¼, da kuma ¾). Ɗalibai na iya yin aiki ɗaiɗaikunsu ko kuma a cikin ƙananan rukunai.
- Yayin da ɗalibai suke gudanar da wani aikin da aka ba su, a ƙara taimaka masu a inda ba su gane sosai ba.

**Bayyanawa**

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala a lokacin Gwajin.

**Aikin Gida**


A baiwa ɗalibai aikin gida na bita da kuma gwajin ƙwazonsu.

| Na. 66 | Zango na 2, Mako na 2, Darasi na A |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya nuna 1/3 na rukunin wasu abubuwa.
**Kayan Aiki:** Ayaba (ko kuma duk wani abu da ake iya rabawa gida uku), samfurin takardar da aka naɗa, aka raba ta gida uku (da'ira da s akwati mai kusurwa huɗu da gidan dara) **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

<u>Duba aikin gida (minti 2)</u>




- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfaf masu gwiwa.

<u>Labari da Hotuna (minti 3)</u>

- Bayyana labarin hotuna a kan allo. Ali da Audu da Nazir sun tafi kasuwa. Sun iske mai sayar da kayan marmari yana da ayaba guda ɗaya kacal da ta rage masa. Da farko, sun yi muhawarar wanda za a sayar wa ayabar daga cikinsu. Daga baya, sai suka yanke shawarar cewa za su raba ayabar daidai.
- A kira ɗalibai guda uku, su zo gaban aji su yi kwaikwayon labarin. Idan akwai ayaba ta gaskiya, ka/ki ba su su raba tsakaninsu.

## Koyo

<u>Gabatar da Kaso ɗaya: 1/3 (minti 10)</u>



- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi wani abu game da kaso na 1/3. Mun ga yadda ake raba ayaba guda ɗaya zuwa kaso uku. Ɗaya daga cikin waɗannan kaso daidai yake da 1/3, saboda kaso daya ne daga cikin, kaso guda uku.*
- **Ka/ki ce:** *Haka ma muna iya raba rukunin wasu abubuwa zuwa gida uku.Muna da fasalin da'ira guda uku a kan allo. A wannan misalin, da'ira ukun suna wakiltar cikakken abu guda ɗaya, saboda muna kallon rukunin abubuwa a matsayin guda ɗaya ne.*
- A nemi wani ɗalibi ɗayaya zo gaban allo ya tusa ɗaya daga cikin da'irorin.
- **Ka/ki ce:** *Ɗaya daga cikin da'irorin nan uku na da kala. 1 shi ne kaso na kuma3 ita ce ni gaba ɗaya.*
- A rubuta kaso 1/3 a kan allo domin a nuna da'ira nawa aka tusa.
- **Ka/ki ce:** *Lambar da take sama, 1, tana nuna kason da muke da su gaba ɗaya. Lambar take ƙasa kuwa tana nuna yawan kaso masu girma iri ɗaya da aka samu a jimillar, 3.*
- A maimaita matakan ta hanyar zana hoton sififon gidan dara guda uku ko sifar akwati guda uku a kan allo. A sa wani ɗalibi ya zo gaban aji ya tusa kashi ɗaya bisa uku na sifar, sannan ya rubuta lissafin kason kusa da inda ya tusa.

## Gwaji

<u>Wasar aji gaba ɗaya: A nemo kashi uku (minti 15)</u>

- A gaya wa ɗalibai cewa kowanensu zai samu 1/3 na wata sifar. Su nemi wasu ɗalibai wanɗanda ke da sauran cikon sifofin uku.
- Bayan kowane ɗalibi ya gano cikon sifar tasu, a sa dukkan ɗalibai su tsaya a cikin rukuninsu. Ɗaliban su ɗaga sifofinsu wuri ɗayadomin su samu cikakken sifa ɗaya. Su faɗawa junansu sunan sifar tasu.
- A zagaya ana lura da aikin ɗaliban. A yayin zagayawar, ka/ki tambayi ɗaliban ko sun gane waɗanne sifofi ne ake iya haɗawa a samu cikakkiyar sifar ɗaya. A duba ko sun amsa daidai.

## Bayyanawa

<u>Auna fahimta nan-take (minti 5)</u>

- A ɗaga wata sifa 1/3 sama. A nemi dukkan ɗalibai dake da sauran rabin cikon sifar da su ɗaga siffansu sama, sannan su faɗi sunan siffar a bayyane. A maimaita da sauran rabin siffofin.


## Aikin Gida

A sa ɗalibai su zana hoton sifar akwati a cikin littafansu na rubutu sannan su sanya kala a kashi 1/3 na siffar.

| Na. 67 | Zango na 2, Mako na 2, Darasi na B |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya nuna 2/3 na rukunin wasu abubuwa.
**Kayan Aiki:** Ayaba (ko kuma duk wani abu da ake iya rabawa gida uku) **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**




Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Labari da Hotuna (minti 3)

- Bayyana labarin hotuna a kan allo. Malami yana rarraba biskit guda uku, amma ɗalibai biyu kawai ne ke wurin; Amina da Ali. Amina tana jin yunwa sosai, saboda haka sai Ali ya ce tana iya ɗaukar biskit guda biyu, shi kuma sai ya ɗauki guda ɗaya.
- A kira ɗalibai guda biyu, su zo gaban aji su yi kwaikwayon labarin.
- A yi wa ɗalibai bayanin cewa akwai jimillar biskit guda 3. Amina tana da biskit 2 daga cikin guda 3, saboda haka tana da kashi 2/3 na biskit ɗin. Ali yana da biskit guda 1 daga cikin ukkun. Saboda haka yana da kashi 1/3.
- Rubuta kowane ɗaya daga cikin siffofin a kan allo, yayin da kake/kike yin bayani.


**Koyo**



Gabatar da kaso ɗaya: 1/3 (minti 15)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi kason 2/3.*
- A zana hoton sifar da'ira guda uku a kan allo, sai a yi bayanin cewa kamar jiya, da'irorin nan guda 3 suna nuna cikakkiyar sifa ɗaya. A nemi wani ɗalibi ya zo gaban aji ya tusa kashi ɗaya bisa uku na da'irorin.
- **Ka/ki ce:** *An tusa ɗaya daga cikin da'irorin uku. A wannan misalin, 1 shi ne kaso na, sannan 3 ita ce ni gaba ɗaya. Saboda haka, kason shi ne 1/3.*
- A umurci wani ɗalibi ya zo gaban aji ya tusa wani daga cikin da'irorin.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu an tusa da'irori biyu daga cikin ukun. A kaso 2/3, lambar da take sama, 2, tana nuna kason da muke da su gaba ɗaya. Lambar dake ƙasa kuwa tana nuna yawan kaso masu girma iri ɗaya da aka samu a jimillar. Muna nuna kasonmu na 2/3, ta hanyar rubuta 2 bisa 3.*
- A maimaita matakan ta hanyar zana hoton sifar gidan dara guda uku ko sifar akwati guda uku a kan allo. A sa wani ɗalibi ya zo gaban aji ya tusa kashi ɗaya bisa uku na sifar, sannan sai ya rubuta lissafin kason kusa da inda ya tusa.

**Gwaji**



Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: Zana Hoton Kashi 2/3 (minti 10)

- A zana hoton sifofin akwati a kan allo sannan sai a sa ɗalibai su rubuta sifofin a cikin littafansu na rubutu. A nemi ɗalibai su tusa kashi 1/3 a sifar akwati na farko da kuma 2/3 a sifar akwati na biyu. Ɗalibai na iya duba amsarsu da ta abokan zamansu.
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai a kuma taimaka masu. A nemi ɗalibai su faɗi wane kaso ne ya fi girma a cikinsu.

**Bayyanawa**

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga littafansu na rubutu sama, su nuna abun da suka sanya wa kala.

**Aikin Gida**


A sa ɗalibai su zana hoton da'ira a cikin littafansu na rubutu sannan su sanya kala a kashi 2/3.

| Na. 68 | Zango na 2, Mako na 2, Darasi na C |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya rarrabewa tsakanin 1/3 da kuma 2/3.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)





- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masugwiwa.


Wasan Daidai ne ko Kuskure ne (minti 5)

- A zana hoton wasu sifofi a kan allo. Yi wa ɗalibai bayanin cewa za ka/za ki faɗi wasu jawabai guda uku. Ga kowane daga cikin jawaban, ɗalibai su ɗaga babban yatsansu sama idan jawabin daidai ne su kuma nuna babban yatsansu ƙasa idan jawabin kuskure ne.
- **Ka/ki ce:** *A na nuna 1/4. Daidai ne ko Kuskure ne?*
- **Ka/ki ce:** *A na nuna 1/3. Daidai ne ko Kuskure ne?*
- **Ka/ki ce:** *B na nuna 1/3. Daidai ne ko Kuskure ne?*

### Koyo

Kwatanta kaso na: 1/3 da kuma 2/3 (minti 8)




- **Ka/ki ce:** *A yau za mu kwatanta kaso na 1/3 da kuma 2/3.*
- Ka/ki yi rubutu ga da'irorin guda biyu da ka/kika zana hotonsu a lokacin fara darasi.
- A tambayi ɗalibai su faɗi wane daga cikin kason ya fi girma, ma'ana wane daga cikinsu aka fi tusa mafi yawan ɓangarensa.
- **Ka/ki ce:** *Kashi 2/3 ya fi girma a kan kashi 1/3. A kashi 2/3 akwai kaso guda biyu da aka tusa. A kashi 1/3, kaso ɗayane kawai aka tusa.*
- A maimaita da sifar akwati guda biyu. A gayyato ɗalibai biyu su zo gaban aji su tusa kowace ɗaya daga cikin siffofin akwatin, ta farkon a tusa 1/3 nata, ta biyun kuwa a tusa 2/3 nata.

### Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: Zana Hoton Kashi 2/3 (minti 15)

- A nemi dukkan ɗalibai su zana ɗaya daga cikin siffofin da suka zaɓa a cikin littafansu na rubutu su kuma tusa sifar ta yadda za su nuna 1/3 ko 2/3. Suna iya zaɓar duk kaso da suke son su zana hotonsa.
- Bayan minti biyar, a sa ɗalibai su juya su kalli abokan zamansu. Kowane ɗalibi ya bayyana kaso da sifar da ya zana hotonta ga ɗan'uwansa. Abokan zamansu su bayyana idan 1/3 ne ko kuma 2/3 ne.
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai a kuma taimaka musu. A yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai ta yaya suka gane zanen ya nuna 1/3 ko kuma 2/3.

### Bayyanawa

Nuna kyawawan misalai (minti 5)

- A sa wani ɗalibi/ɗaliba su nuna hoton da suka zana ga aji.
- A nemi sauran ɗalibai su faɗi ko ya yi daidai da 1/3 ko kuma 2/3.
- Idan da lokaci, a maimaita da wasu ɗalibai.

### Aikin Gida

A sa ɗalibai su zana hoton sifofi guda biyar, su kuma sanya wa kowanensu kala ta yadda zai nuna ɗaya daga cikin kason da suka koya zuwa yanzu na: ½, ¼, 1/3, ¾, da kuma 2/3. Ɗalibai su nuna aikin da suka yi ga wani ɗan'uwansu ko wani abokinsu.

| Na. 69 | Zango na 2, Mako na 2, Darasi na D |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya rarrabewa tsakanin 1/3 da kuma 2/3
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwarsu.

Gina ɓangarori (minti 3)

- A kira ɗalibai guda uku su zo gaban aji.
- **Ka/ki ce:** *Duk mai son ya ci goro ya ɗaga hannunsa sama.*
- **Ka/ki ce:***Muna iya rubuta lambar adadin ɗaliban dake son su ci goro a matsayin kason. Da farko, sai mu rubuta 3 a ƙasa, domin ita ke nuna cikakken abun da muke da shi. Daga nan, sai mu sanya lambar adadin ɗaliban dake son su ci goro a saman layin.*
- A rubuta kason da yake daidai a kan allo domin ɗalibai su gani. A maimaita da wasu nau'o'in abinci ko wasu ayyuka kamar; (shan miyar kuka ko wasan ƙwallon ƙafa).

**Koyo**

Kwatanta kaso na: ½ da ¼ da ¾ da 1/3 da kuma 2/3 (minti 10)

- **Ka/ki ce**: *A wannan makon mun koyi darusa a kan kason : 1/3 da 2/3. Mun kuma san ½ da ¼ da kuma ¾.*
- A kira ɗalibai 6 su zo gaban aji.
- **Ka/ki ce:** *Kuna da daƙiƙai 20, da za ku raba babban rukuninku na ɗalibai shida a cikin kashi uku, ko kuma rukunai uku waɗanda yawansu yake daidai. Kashi ɗaya bisa uku, na rukunin farko, ya tsaya a gefe ɗaya na ajin, kashi ɗaya bisa uku guda kuwa ya tsaya a tsakiyar ajin, sannan rukuni guda na kashi ɗaya bisa ukun ya tsaya a wani gefe daban na aji. Kun shirya, to ku fara!*
- Umurci wasu ɗalibai su yi ƙirge tare da kai/ke a bayyane zuwa 20, yayin da rukunin ɗaliban 6 suke rarraba kansu a cikin rukunai uku waɗanda yawansu yake daidai.
- Bayan daƙiƙa 20, a nemi ɗalibai su duba idan an rarraba rukunin a cikin rukunai uku na ɗalibai bibbiyu waɗanda yawansu yake daidai ta hanyar ɗaga babban yatsansu sama ko nuna babban yatsansu ya kalli ƙasa.
- A maimaita aikin da wasu adadin ɗalibai daban da kuma wasu kason na daban. Alal misali; kana/kina iya kiran ɗalibai 8 su zo gaban aji, sannan ka/ki nemi su rarraba kansu a cikin kaso huɗu.

**Gwaji**

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: Kwatanta ɓangarori (minti 15)

- A umurci ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 33.
- A karanta umurnin da aka rubuta a bayyane ga ɗalibai a kuma kammala lissafin farko da ajin.
- Ɗalibai su kammala sauran lissafin da kansu, amma suna iya duba amsarsu da ta abokan zamansu.
- A zagaya ana lura da ɗalibai a kuma taimaka musu.

**Bayyanawa**

Nuna amsoshi (minti 5)

- A umurci wani ɗalibi ya rubuta ɗaya daga cikin amsoshinshi a kan allo.
- A nemi wasu ɗalibai su nuna amsar ta hanyar ɗaga babban yatsansu sama idan amsar daidai ce ko kuma su nuna babban yatsansu ƙasa idan ba daidai ba ce. Ka/ki yi musu gyara idan akwai buƙata.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 33 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

**Na. 70**

# Zango na 2, Mako na 2, Darasi na E

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi bita da gwajin abun da suka koya a cikin wannan makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Naɗe Ɓangarori Uku (minti 3)

- A sa ɗalibai su ɗauko fallen takarda ɗaya. A nunawa ɗalibai yadda ake naɗe fallen takardar tasu a cikin ɓangarori 3. Sannan sai a sa ɗalibai su buɗe takardar su gani idan kowane rabin daidai yake da ɗan'uwwanshi.
- A sa ɗalibai su buɗe takardunsu, sai su rubutawa kowane ɓangare lambobin 1, da 2 da kuma 3 domin su nuna ɓangarorin takardar girmansu ɗaya.

## Koyo

Bita da maimai (minti 10)

- A zaɓi wani darasi daga cikin darrusan da aka yi a cikin makon, wanda ake ganin ɗalibai ba su fahimce shi sosai ba. A sake koyar da darasin ko a sake koyar da shi ta wata sabuwar hanya ta daban.

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai a cikin rukuni: Zane da kuma rubutu (minti 15)

- A ba ɗalibai aikin da zai taimaka musu wajen yin gwajin darasin da aka yi bita (alal misali; rarrabewa tsakanin 1/3 da kuma 2/3). Ɗalibai na iya yin aiki ɗaiɗaikunsu ko kuma a cikin ƙananan rukunai.
- Yayin da ɗalibai suke gudanar da wani aikin da aka ba su, a ƙara taimaka musu a inda ba su gane sosai ba.

## Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala a lokacin Gwajin.

## Aikin Gida

A ba ɗalibai aikin gida na bita da kuma gwajin ƙwazonsu.

**Na. 71**

# Zango na 2, Mako na 3, Darasi na A

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane 1/5 na abubuwa.

**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)


- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Labari (minti 3)

- A kira ɗalibai biyar su zo gaban aji. Faɗi masu cewa za ka/za ki faɗi wata lamba da sauri, su kuma za su nuna lambar da yatsunsu cikin sauri, gwargwadon yadda suke iyawa.
- Kira lambobi da yawa, misali: 2 da 3 da kuma 4. A ƙarshe ka/ki kira lamba ta 1.
- **Ka/ki ce:** *Yatsu nawa kuka ɗaga sama? Jimillar yatsu nawa gare ku a hannu guda?*
- **Ka/ki ce:** *Kuna da yatsa guda a sama daga cikin jimillar yatsunku guda biyar. Saboda haka muna iya rubuta wannan a matsayin 1/5.*

## Koyo


Gabatar da kaso ɗaya na: 1/5 (minti 10)



- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi wani abu game da kaso* ɗaya *na 1/5. Muna da da'irori guda biyar a kan allo. A wannan misalin, da'irorin nan guda biyar suna wakiltar cikakken abu* ɗaya*, saboda hoton cikakken abu* ɗaya *ne.*
- A umurci wani ɗalibi ɗaya ya zo gaban allo ya tusa ɗaya daga cikin da'irorin.
- **Ka/ki ce:** *Ɗaya daga cikin da'irorin biyar yana da kala. 1 shi ne kaso na, sannan 3 ita ce ni gaba ɗaya.*
- A rubuta kaso na 1/5 a kan allo domin a nuna da'ira nawa aka tusa.
- **Ka/ki ce:** *Lambar da take sama, 1, tana nuna kason da muke da su gaba ɗaya. Lambar take ƙasa kuwa tana nuna yawan kaso masu girma iri ɗaya da aka samu a jimillar, 5.*
- A maimaita matakan ta hanyar zana hoton sifar gidan dara ko sifar akwati guda biyar a kan allo. A sa wani ɗalibi ya zo gaban aji ya tusa kashi ɗaya bisa biyar na sifar, sannan ya rubuta kason kusa dasifar.

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: Zana Hoton Kashi 1/5 (minti 15)



- A zana hoton sifar akwati ko sifar da'ira a kan allo.
- A umurci ɗalibai su rubuta sifofin a cikin littafansu na rubutu, su kuma tusa 1/5 na kowane daga cikin sifofin.
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai a kuma taimaka masu.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga littafansu na rubutu sama, su nuna abun da suka sanya wa kala.

## Aikin Gida


A sa ɗalibai su zana hoton dake nuna 1/5 a cikin littafansu na rubutu.

| Na. 72 | Zango na 2, Mako na 3, Darasi na B |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya gane 1/6 na abubuwa.
**Kayan Aiki:** Ayaba (ko wani abu da ake rabawa a cikin gida shida) **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)




- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.


Labari da Hotuna (minti 3)

- Bayyana labarin hotuna a kan allo. Abokai shida sun tafi kasuwa suna neman dunkulen ayaba.Mai sayar da kayan marmarin dunkulen ayaba ɗaya kacal ya rage masa. Akwai ayaba shida a dunkulen, saboda haka sai abokan suka yi shawarar kowannensu ya ɗauki ayaba ɗaya, don ya kasance kowa ya samu yawan ayabar iri ɗaya.
- A kira ɗalibai guda shida, su zo gaban aji su yi kwaikwayon labarin. Idan akwaidunkelen ayaba na gaskiya a ba su su raba. Idan babu a ba su fallen takarda da za su raba gida shida.
- A yi wa ɗalibai bayanin cewa kowanensu yana da kashi 1/6 na dunkulen ayabar.
- Rubuta kowane ɗaya daga cikin kason a kan allo 1/6, yayin da kake/kike yin bayani.

**Koyo**

Gabatar da kaso ɗaya: 1/6 (minti 10)





- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi wani abu game da kaso ɗaya, na 1/6.*
- A zana hoton da’ira guda shida a kan allo, sai a yi bayanin cewa, da’rorin guda shida suna nuna cikakkiyar sura guda. A nemi wani ɗalibi ya zo gaban aji ya tusa kashi ɗaya bisa shida na da’irorin.
- **Ka/ki ce:** *An tusa ɗaya daga cikin da’irorin shida. A wannan misalin, 1 shi ne ɓangare na, sannan 6 ita ce ni gaba ɗaya. Saboda haka, kaso shi ne 1/6.*
- A maimaita matakan ta hanyar zana gidan dara shida ko dala shida a kan allo. A sa wani ɗalibi ya zo gaban aji ya tusa kashi ɗaya bisa shida na zanen, sannan sai ya rubuta kason kusa da zanen.

**Gwaji**

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: Zana Hoton 1/6 (minti 15)

- A umurci ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 34.
- A karanta umurni da aka rubuta a bayyane ga ɗalibai a kuma kammala lissafin farko da ajin.
- Ɗalibai su kammala sauran lissafin da kansu, amma suna iya duba amsarsu da ta abokan zamansu.
- A zagaya a duba ko sun amsa daidai a kuma taimaka masu. A yayin zagayawar, a tambaye su yadda suka samo amsar ta su, a kuma duba ko sun amsa daidai.

**Bayyanawa**

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga littafansu na rubutu sama, su nuna abun da suka sanya wa kala.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 34 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

Na. 73


# Zango na 2, Mako na 3, Darasi na C

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya rarrabewa tsakanin 1/5 da kuma 1/6.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.





Wasan daidai ne ko kuskure ne (minti 5)

- A zana hoton wasu surori a kan allo. Yi wa ɗalibai bayanin cewa za ka/za ki faɗi wasu jawabai guda uku. Ga kowane daga cikin jawaban, ɗalibai su ɗaga babban yatsansu sama idan jawabin daidai ne, su kuma nuna babban yatsansu ƙasa idan jawabin kuskure ne.
- **Ka/ki ce:** *A na nuna 1/5. Daidai ne ko Kuskure ne?*
- **Ka/ki ce:** *A na nuna 1/6. Daidai ne ko Kuskure ne?*
- **Ka/ki ce:** *B na nuna 1/5. Daidai ne ko Kuskure ne?*

## Koyo

Kwatanta Kaso na: 1/5 da kuma 1/6 (minti 8)




- **Ka/ki ce:** *A yau za mu kwatanta kaso ɗaya na 1/5 da kuma 1/6.*
- A yi rubutu ga da'irorin biyu da aka zana hotonsu a lokacin fara darasi.
- A tambayi ɗalibai su faɗi wane daga cikin kason ya fi girma, ma'ana wane daga cikinsu aka fi tusa mafi yawan kasonsa.
- **Ka/ki ce:** *Kashi 1/5 ya fi girma a kan kashi 1/6 saboda an fi tusa mafi yawan da'irarsa.*
- A maimaita da sura mai sifar gidan siga biyu. A gayyato ɗalibai biyu su zo gaban aji su tusa kowace ɗaya daga cikin surorin masu sifar gidan siga, ta farkon a tusa 1/5 nata, ta biyun kuwa a tusa 1/6 nata.

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: Zana Hoton Kashi 1/5 ko 1/6 (minti 15)

- A umurci dukkan ɗalibai su zana ɗaya daga cikin sifofin da suka zaɓa a cikin littafansu na rubutu su kuma tusa sifar ta yadda za su nuna 1/5 ko 1/6. Suna iya zaɓar kason da suke son su zana hotonsa.
- Bayan minti biyar, a sa ɗalibai su juya, su kalli abokan zamansu. Kowane ɗalibi ya bayyana kason sifar da ya zana hotonta ga ɗan'uwansa. Abokin zamansu ya bayyana idan 1/5 ne ko kuma 1/6 ne.
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai a kuma taimaka masu. A yayin zagayawar, a tambayi ɗalibai ta yaya suka gane zanen ya nuna 1/5 ko kuma 1/6.

## Bayyanawa

Nuna kyawawan misalai (minti 5)

- A sa wani ɗalibi/ ɗaliba su nuna hoton da suka zana a aji.
- A umurci sauran ɗalibai su faɗi ko ya yi daidai da 1/5 ko kuma 1/6.
- Idan da lokaci, a maimaita da wasu ɗalibai.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su zana hoton sifofi guda biyar, su kuma sanya wa kowanensu kala ta yadda zai nuna ɗaya daga cikin kason da suka koya zuwa yanzu na: ½ da ¼ da 1/3 da ¾, da 2/3 da 1/5 da kuma 1/6. Ɗalibai su nuna aikin da suka yi ga wani ɗan'uwansu ko wani abokinsu.

| Na. 74 | Zango na 2, Mako na 3, Darasi na D |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya rarrabewa tsakanin ½ da ¼ da ¾ da 1/3 da 2/3 da 1/5 da kuma 1/6.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Gina ɓangarora (minti 3)

- A kira ɗalibai guda shida su zo gaban aji.
- **Ka/ki ce:** *Duk mai son ya ci tuwo ya ɗaga hannunsa sama.*
- **Ka/ki ce:** *Muna iya rubuta lambar adadin ɗaliban dake son su ci tuwo a matsayin wani kaso. Da farko, sai mu rubuta 6 a ƙasa, domin ita ke nuna cikakken abun da muke dashi. Daga nan, sai mu sanya lambar adadin ɗaliban dake son su ci tuwo a saman layin.*
- A rubuta kason da yake daidai a kan allo domin ɗalibai su gani.
- A maimaita da wasu nau'o'in abinci ko wasu ayyuka kamar; (cin masa ko wasan ƙwallon ƙafa).

**Koyo**

Kwatanta Kaso na: ½ da ¼ da ¾ da 1/3 da 2/3 da 1/5 da kuma 1/6 (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi darussa a kan kwatanta dukkan kason da muka koya a darrusanmu na baya. Suna da yawa sosai!*
- A kira ɗalibai 10 su zo gaban aji.
- **Ka/ki ce:** *Kuna da diƙaƙa 20, da za ku raba babban rukuninku na ɗalibai goma a cikin kashi biyar, ko kuma rukunai biyar waɗanda yawansu yake daidai. Kun shirya? to ku fara!*
- Umurci wasu ɗalibai su yi ƙirge tare da kai/ke a bayyane zuwa 20, yayin da rukunin ɗaliban 10 suke rarraba kansu a cikin rukunai biyar waɗanda yawansu yake daidai.
- Bayan daƙiƙa 20, a umurci ɗalibai su duba idan an rarraba rukunin a cikin rukunai biyar na ɗalibai bibbiyu, su nuna idan an yi daidai ta hanyar ɗaga babban yatsansu sama ko nuna babban yatsansu ya kalli ƙasa.
- A maimaita aikin da wasu adadin ɗalibai daban da kuma wasu kaso na daban. Alal misali, kana/kina iya kiran ɗalibai 20 su zo gaban aji, sannan ka/ki umurce su da su raba kansukasogida huɗu ko kuma gida biyu.

**Gwaji**

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: Kwatanta kaso (minti 15)

- A umurci ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 35.
- A karanta umurni da aka rubuta a bayyane ga ɗalibai a kuma kammala lissafin farko da ajin.
- Ɗalibai su kammala sauran lissafin da kansu, amma suna iya duba amsarsu da ta abokan zamansu.
- A zagaya ana lura da ɗalibai a kuma taimaka masu. A yayin zagayawar, a tambaye su yadda suka samo amsar ta su, a kuma duba ko sun amsa daidai.

**Bayyanawa**

Nuna amsoshi (minti 5)

- A umurci wani ɗalibi ya rubuta ɗaya daga cikin amsoshinsa a kan allo.
- A umurci wasu ɗalibai su nuna amsar ta hanyar ɗaga babban yatsansu sama idan amsar daidai ce ko kuma su nuna babban yatsansu ƙasa idan ba daidai ba ce. Ka/ki yi masu gyara idan akwai buƙata.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 35 a cikin littafin rubutunsu a matsayin aikin gida.

**Na. 75** | # Zango na 2, Mako na 3, Darasi na E

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi bita da gwajin abun da suka koya a cikin wannan makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Naɗe Ɓangarori Uku (minti 3)

- A sa ɗalibai su ɗauko fallen takarda ɗaya. A nunawa ɗalibai yadda ake naɗe fallen takardar tasu a cikin ɓangarori 3. Sannan sai a sa ɗalibai su buɗe takardar, su gani idan kowane rabin daidai yake da ɗan'uwwansa.
- A sa ɗalibai su buɗe takardunsu, sai su rubutawa kowane ɓangaren lambobin 1, da 2 da kuma 3 domin su nuna ɓangarorin takardar girmansu ɗaya.

**Koyo**

Bita da maimai (minti 10)

- A zaɓi wani darasi daga cikin darrusan da aka yi a cikin makon, wanda ake ganin ɗalibai ba su fahimce shi sosai ba. A sake koyar da darasin ko a sake koyar da shi ta wata sabuwar hanya ta daban.

**Gwaji**

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai a cikin rukuni: Zane da kuma rubutu (minti 15)

- A baiwa ɗalibai aikin da zai taimaka masu wajen yin gwajin darasin da aka yi bita (alal misali; rarrabewa tsakanin 1/3 da kuma 2/3). Ɗalibai na iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma a cikin ƙananan rukunai.
- Yayin da ɗalibai suke gudanar da wani aikin da aka ba su, a ƙara taimaka masu a inda ba su gane sosai ba.

**Bayyanawa**

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala a lokacin Gwajin.

**Aikin Gida**

A baiwa ɗalibai aikin gida na bita da kuma gwajin ƙwazonsu.

| Na. 76 | Zango na 2, Mako na 4, Darasi na A |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su rubuta ƙwallin lambobi 2 a cikin fasali mai faɗi.
**Kayan Aiki:** Kara **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Kirge (minti 3)

- Da ajin gaba ɗaya, a yi ƙirge a bayyane zuwa 100, a yi ƙirgen tsallake da biyar-biyar. Sannan sai a yi ƙirgen tsallake da goma-goma zuwa 100.

**Koyo**

Gabatar da faɗaɗa lissafin lambobi 'yan tagwai (minti 10)

| |
|---|
| ☐ Goma-goma + ☐ ɗaiɗai = 25 |

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi wani abu a kan faɗaɗa lissafi. Faɗaɗa lissafi shi ne yayin da muka nuna kimar kowace lamba: ɗaiɗai da goma-goma da ɗari-ɗari da kuma waɗanda suka fi haka.*
- A rubuta lambar 25 a kan allo, a kuma yi wa ɗalibai bayanin cewa wannan ƙwallin lamba 2 ce.
- A ajiye kara 25 gaban allo a kan tebur sai a kira wani ɗalibi ya zo gaban aji. A sa ɗalibin ya rarraba karan a cikin damin kara goma-goma. A yi ƙirge a bayyane da goma-goma, don a gano jimillar karan dake cikin dami-damin.

| |
|---|
| Goma-goma 2 + 5 ɗaiɗai = 25<br>20 + 5 = 25 |

- **Ka/ki ce:** *Akwai dami 2 na gwammai, saboda haka muna iya sanya lamba 2 a cikin akwati. Goma 2 daidai suke da 20.*
- A ƙirga adadin karan da suka rage a bayyane da aji gaba ɗaya.
- **Ka/ki ce:** *Akwai kara guda biyar da suka rage, saboda haka a rubuta lamba 5 a gurbin ɗaiɗai. Ɗaiɗai 5 daidai suke da 5.*
- **Ka/ki ce:** *Yanzu, muna iya tara ƙwallin lambobi 2 wuri guda don mu gano jimillar yawan karan da muke da su.*
- A warware lissafin 20 + 5 = a kan allo da ajin.

**Gwaji**

Aiki a cikin ƙaramin rukuni: Rubuta lambobi a cikin fasali mai faɗi (minti 15)

- A umurci ɗalibai su zauna a cikin ƙananan rukunai.
- A rubuta lambobi biyar a kan allo: 44 da 17 da 81 da 62 da kuma 39.
- A sa ɗalibai su rubuta dukkan lambobin a cikin littafansu na rubutu sannan su yi aiki tare da wasu 'yan'uwansu ɗaliban dake cikin rukunan, su rubuta lambobin a cikin fasali mai faɗi.
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai. A yayin zagayawar, a tambaye su yadda suka samo amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.

**Bayyanawa**

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu sama, su nuna abun da suka rubuta. A yaba wa ƙwazonsu.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran Gwajin da suka fara a aji, a matsayin aikin gida.

| Na. 77 | Zango na 2, Mako na 4, Darasi na B |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su rubuta su kuma tara ƙwallin lambobi 2 a cikin fasali mai faɗi.
**Kayan Aiki:** Kara **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

<u>Duba aikin gida (minti 2)</u>

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

<u>Waƙa (minti 3)</u>

- Rera waƙar tare da ɗalibai sau da yawa.
- A umurci ɗaya daga cikin ɗalibai ya zo gaban aji ya rera waƙar.

> <u>Waƙar Tarawa</u>
> Ana batun tarawa /
> Komai a tara da ɗaya /
> 1+1= 2 / 2+1= 3 / 3+1= 4 /
> 4+1= 5 / 5+1= 6 / 6+1= 7 /
> 7+1= 8 / 8+1= 9 / 9+1= 10

## Koyo

<u>Gabatar da tara lambobi a cikin fasali mai faɗi (minti 10)</u>

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu koyi yadda ake tara lambobi a cikin fasali mai faɗi.*
- A rubuta fasalin lissafi na 45 + 23 a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Domin tara 45 +23, da farko muna buƙatar rubuta kowace lamba a cikin fasali mai faɗi.*
- A yi wa ɗaliban gwajin yadda ake rarraba 45 a cikin gwammai 4 da kuma ɗaiɗai guda 5.
- Daga nan sai a nemi wani ɗalibi ya zo gaban aji ya rubuta 23 a cikin fasali mai faɗi.
- Bayan dukkan lambobin sun kasance a cikin fasali mai faɗi, sai a fara tara su wuri guda.
- **Ka/ki ce:** *Idan muka tara lambobi a cikin fasali mai faɗi, da farko muna buƙatar lambobin gurbin gidan ɗaiɗai wuri guda. Za mu yi amfani da lissafin tsaye mu yi haka. Waɗanne lambobi ne suke a gurbin gidan ɗaiɗai?*
- A tara 5 + 3 wuri guda, sai a rubuta 8 a ƙasan layin. A yi wa ɗalibai bayanin cewa suna iya ɗaukar alamarsu ta + su kai ta kai tsaye a ƙasan layin.
- **Ka/ki ce:** *Abu na gaba sai mu tara goma-goma wuri guda. Mene ne amsar 40 + 20?*
- A rubuta 60 a ƙasan layin, a ƙarkashin 40 + 20.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu fasalin lissafinmu ya kammla, muna iya tara lambobinmu wuri guda. Mene ne amsar 60 + 8?*
- Idan ɗalibai suna buƙatar taimako, a yi ƙirge da su a bayyane daga 60, ko a umurce su da su duba jadawalin lambobi 1-100 dake gaban aji. A yi bayanin cewa 60 +8 daidai yake da 45 +23. Sai dai mun nemo hanya mafi sauƙi ce ta warware shi kawai!

> 45 + 23
>
> 40 + 5
> <u>20 + 3</u>
>
> 40 + 5
> <u>20 + 3</u>
> + 8
>
> 40 + 5
> <u>20 + 3</u>
> 60 + 8
>
> 40 + 5
> <u>20 + 3</u>
> 60 + 8 = 68

## Gwaji

<u>Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: Tara Lambobi 'Yan tagwai a cikin Fasali Mai Faɗi (minti 15)</u>

- A umurci ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 36. A karanta umurni da aka rubuta a bayyane ga ɗalibai a kuma kammala lissafin farko da ajin.
- A umurci ɗalibai su kammala sauran lissafi 2 na gaba dake kan shafin. Suna iya aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma tare da abokan zamansu.
- A zagaya ana lura da ɗalibai a kuma taimaka musu.

## Bayyanawa

<u>Nuna kyawawan misalai (minti 5)</u>

- A bayyana wa sauran ɗalibai ƙwararan misalan da ɗalibi ya bayar.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 36 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

**Na. 78**

# Zango na 2, Mako na 4, Darasi na C

**Manufofi:** Ɗalibai za su tara ƙwallin lambobi 2 a cikin lissafin tsaye da kuma lissafin kwance.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai sau da yawa.

Waƙar Tarawa
Ana batun tarawa /
Komai a tara da ɗaya /
1+1= 2 / 2+1= 3 / 3+1= 4 /
4+1= 5 / 5+1= 6 / 6+1= 7 /
7+1= 8 / 8+1= 9 / 9+1= 10

## Koyo

Tarawa ta lissafin kwance (minti 7)

34 + 15 = 49

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu yi gwajin tara ƙwallin lambobi 2 ta lissafin kwance da kuma lissafin tsaye.*
- A Rubuta : 34+ 15 = ____ a kan allo.
- ***Ka/ki ce:*** *Idan za mu ba da amsar fasalin daidaito a cikin lissafin kwance, da farko za mu fara tara lambobin da suke gidan ɗaidai wuri guda. Lambobi ɗaidai nawa gare mu?*
- A yi da’ira ga 5 da kuma 4 a cikin dukkan lambobin biyu, sannan a tambayi ɗalibai mene ne amsar 5 + 4. A rubuta lambar 9 a gurbin gidan ɗaiɗai a kan layin da ake sa amsa.
- **Ka/ki ce:** *Abu na gaba, sai mu tara lambobin dake gurbin gidan gwammai wuri ɗaya. Gwammai nawa ne a wurin?*
- A yi da’ira ga 1 da kuma 3 a cikin dukkan lambobin biyu sai a tambayi ɗalibai mene ne amsar 3+1. A rubuta lamba ta 4 a gurbin gidan gwammai a kan layin da ake sa amsa.
- **Ka/ki ce:** *34 a tara da 15 zai ba da 49.*

$$\begin{array}{r} 34 \\ +\ 15 \\ \hline 49 \end{array}$$

Tarawa ta lissafin tsaye (minti 8 minutes)

- **Ka/ki ce:** *Kamar dai yadda yake idan mun yi lissafin kwance, za mu fara da tara lambobin dake gurbin gidan ɗaiɗai wuri ɗaya.*
- A nuna lambobin 4 da kuma 5 sannan sai a rubuta lamba 9 a muhallin da yake daidai a ƙarƙashin fasalin lissafin.
- **Ka/ki ce:** *Abu na gaba, sai mu tara lambobin dake gurbin gidan gwammai wuri ɗaya.*
- A nuna lambobin 3 da kuma 1 sannan sai a rubuta lamba 4 a muhallin da yaje daidai a ƙarƙashin fasalin lissafin.
- **Ka/ki ce:** *34 a tara da 15 zai ba da 49.*

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: Tara Lambobi ta lissafin tsaye ko lissafin kwance (minti 15)

- A umurci ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 37.
- A karanta umurni da aka rubuta a bayyane ga ɗalibai a kuma kammala lissafin farko da ajin.
- A umurci ɗalibai su kammala sauran lissafi 2 na gaba dake kan shafin. Suna iya aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma tare da abokan zamansu.
- A zagaya ana lura da ɗalibai a kuma taimaka musu.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu sama, su nuna abun da suka rubuta. A yaba wa ƙwazonsu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 37 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 79 | Zango na 2, Mako na 4, Darasi na D |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su warware lissafi da aka rubuta da kalmomi ta amfani da tarawa.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai sau da yawa.

Waƙar Tarawa
Ana batun tarawa /
Komai a tara da ɗaya /
1+1= 2 / 2+1= 3 / 3+1= 4 /
4+1= 5 / 5+1= 6 / 6+1= 7 /
7+1= 8 / 8+1= 9 / 9+1= 10

## Koyo

Gabatar da warware lissafi na kalmomi ta amfani da tarawa (minti 10)

- Bayyana labarin: Yakaka da Laraba sun tattaro kara da ganyen itace da duwatsu da duk wasu abubuwa masu ƙwarori da ake samu a kusa da su. A yau Yakaka ta tattaro duwatsu 43 ta haɗa su da waɗanda Laraba ta samo guda 13. Guda nawa gare su a jimilla gaba ɗaya?
- A kira ɗalibai guda biyu su zo gaban aji, su yi kwaikwayon labarin. A sa kowane daga cikin ɗaliban ya rubuta yawan duwatsun da suka tattara a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Yakaka ta tattara duwatsu 43 Laraba kuma ta tattara duwatsu 13. Idan muna son mu gano ko duwatsu nawa suka tara gaba ɗaya, dole ne sai mun tara waɗannan lambobin wuri guda.*
- A umurci wani ɗalibi ya zo gaban aji ya rubuta fasalin lissafin dake bayyana labarin.
- Ka/ki tabbata an rubuta 43 + 13 = a kan allo.
- A umurci wani ɗalibi ya zo gaban aji ya yi gwajin yadda ake tara lambobin ta lissafin kwance.
- A umurci wani ɗalibi ya zo gaban aji ya yi gwajin yadda ake tara lambobin ta lissafin tsaye.
- A yi amfani da jadawalin lambobi 1-100, a yi ƙirgen 43 a tara da 13 tare da ajin gaba ɗaya domin a tabbatar da amsar.

## Gwaji

Aiki a cikin ƙaramin rukuni: Warware lissafi na rubutu ta amfani da tarawa (minti 15)

- A nemi ɗalibai su zauna a cikin ƙananan rukunai su kuma buɗe littafansu na rubutu a shafin da jadawalin lambobi yake.
- **Ka/ki ce:** *Salim yana da alewa 24 waɗanda yake son ya rabawa 'yan ajinsu. Kafin ya bar gida zuwa makaranta mamarsa ta ba shi karin wasu 60! Yanzu alewa nawa Salim yake dasu?*
- A maimaita faɗin lissafin ta kalmomi sau da yawa don tabbatar da ɗalibai sun ji lambobin da aka faɗi.
- A sa ɗalibai su rubuta fasalin lissafin a cikin littafansu na rubutu a ɗaiɗaikunsu.
- Da zarar ɗaliban sun gama rubuta fasalin lissafin, a sa ɗalibai su yi aiki tare don su warware lissafin. Za su yi gwajin warware lissafin na kalmomi a fasalin lissafin kwance da kuma lissafin tsaye.
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai a kuma taimaka masu. Idan da lokaci, a maimaita da wani lissafin daban.

## Bayyanawa

Bita da Bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su bayyana amsoshinsu ga wani rukuni, su kuma tattauna yadda suka warware lissafin.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su warware lissafin 11 + 81 = a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 80 | Zango na 2, Mako na 4, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi bita da gwajin abun da suka koya a cikin wannan makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai sau da yawa.

> Waƙar Tarawa
> Ana batun tarawa /
> Komai a tara da ɗaya /
> 1+1= 2 / 2+1= 3 / 3+1= 4 /
> 4+1= 5 / 5+1= 6 / 6+1= 7 /
> 7+1= 8 / 8+1= 9 / 9+1= 10

**Koyo**

Bita da maimai (minti 10)

- A zaɓi wani darasi daga cikin darrusan da aka yi a cikin makon, wanda ake ganin ɗalibai ba su fahimce shi sosai ba. A sake koyar da darasin ko a sake koyar da shi ta wata sabuwar hanya ta daban.

**Gwaji**

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai a cikin rukuni: Zane da kuma rubutu (minti 15)

- A ba ɗalibai aikin da zai taimaka musu wajen yin gwajin darasin da aka yi bita (alal misali; tara lambobi ʻyan tagwai ta lissafin tsaye da kuma lissafin kwance).
- Ɗalibai na iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma a cikin ƙananan rukunai.
- Yayin da ɗalibai suke gudanar da wani aikin da aka ba su, a ƙara taimaka masu a inda ba su gane sosai ba.

**Bayyanawa**

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala a lokacin Gwajin.

**Aikin Gida**

A ba ɗalibai aikin gida na bita da kuma gwajin ƙwazonsu.

| Na. 81 | Zango na 2, Mako na 5, Darasi na A |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su rubuta ƙwallin lambobi uku a cikin fasali mai faɗi.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Kirge (minti 3)

- Da ajin gaba ɗaya, a yi ƙirge a bayyane zuwa 1000, a yi ƙirgen tsallake da ɗari-ɗari. Sannan sai a yi ƙirgen tsallake da bibbiyu zuwa 100.

**Koyo**

Gabatar da Faɗaɗa Lissafin Kwallin Lambobi Uku (minti 10)

- **Ka/ki ce:** A yau zamu koyi wani abu a kan faɗaɗa lissafin ƙwallin lambobi 3.

☐ɗari-ɗari+ ☐ goma-goma + ☐ɗaiɗai = 157

- A rubuta 157 a kan allo sannan sai a tambayi ɗalibai adadin lambobi guda nawa ne a cikin lambar 157. A yi wa ɗalibai bayanin cewa da zarar an samu lamba, mai ƙwallin lambobi 3, koyaushe akwai gurbin gidan ɗaruruwa da gurbin gidan goma-goma da kuma gurbin gidan ɗaiɗai.
- A umurci ɗalibai su faɗi ɗaruruwa nawa ake samu a cikin lambar 157. A umurci ɗalibai su koma ga jadawalinsu na lambobi 1-100, idan suna buƙatar raimako.
- **Ka/ki ce:** *Haka ne, akwai ɗari guda a cikin 157, saboda haka muna iya rubuta 1 a cikin akwatin farko. Ɗari ƙwara 1, daidai take da 100.*

Ɗari 1 + goma-goma 5 + Ɗaiɗai 7 = 157
100 + 50 + 7 = 157

- **Ka/ki ce:** *Abu na gaba, wace lamba ce muke da gurbin gidan goma-goma? Goma-goma nawa muke da?*
- A kira wani ɗalibi ɗayaya zo gaban aji sannan a ba shi dama ya sa lamba 5 a gurbin gidan gwammai.
- **Ka/ki ce:** *Haka ne, muna da goma-goma guda 5. Goma-goma 5 daidai suke da 50.*
- **Ka/ki ce:** *Daga ƙarshe, ɗaiɗai nawa muke dasu? Wace lamba ce ya kamata a sa a gurbin gidan ɗaiɗai?*
- A kira wani ɗalibi ya zo gaban aji sannan a ba shi dama ya sa lamba 7 a gurbin gidan ɗaiɗai.
- **Ka/ki ce:** Haka ne, ɗaiɗai guda bakwai daidai suke da *7. Yanzu, kasancewar duk muna da lambobin mu da aka rubuta a cikin fasali mai faɗi, muna iya tara ƙwallin lambobin 3 wuri ɗayadomin samun jimillar yawan karan.*
- A warware lissafin 100 + 50 + 7 a kan allo tare da ajin gaba ɗaya.

**Gwaji**

Aiki a cikin ƙaramin rukuni: Rubuta lambobi a cikin fasali mai faɗi (minti 15)

- A umurci ɗalibai su zauna a cikin ƙananan rukunai. A rubuta lambobi uku a kan allo: 842 da 276 da 391.
- A sa ɗalibai su rubuta dukkan lambobin a cikin littafansu na rubutu sannan su yi aiki tare da wasu 'yan'uwansu ɗaliban dake cikin rukunan, su rubuta lambobin a cikin fasali mai faɗi.
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai.

**Bayyanawa**

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu sama, su nuna abun da suka rubuta. A yaba wa ƙwazonsu.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin Gwajin da suka fara a cikin aji, a matsayin aikin gida.

| Na. 82 | Zango na 2, Mako na 5, Darasi na B |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su rubuta, su kuma tara ƙwallin lambobi 3 a cikin fasali mai faɗi.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai sau da yawa.

> Waƙar Tarawa
> Ana batun tarawa /
> Komai a tara da ɗaya /
> 1+1= 2 / 2+1= 3 / 3+1= 4 /
> 4+1= 5 / 5+1= 6 / 6+1= 7 /
> 7+1= 8 / 8+1= 9 / 9+1= 10

## Koyo

Gabatar da tara ƙwallin lambobi 3 a cikin fasali mai faɗi (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Za mu koyi yadda ake tara ƙwallin lambobi 3 a cikin fasali mai faɗi.*
- A rubuta fasalin lissafi na 452 + 231 a kan allo sannan sai a yi bayanin cewa da farko dole ne a rubuta kowace lamba a cikin fasali mai faɗi.
- A yi wa ɗaliban gwajin yadda ake rarraba 452 a cikin ɗaruruwa 4 da gwammai biyar da kuma ɗaiɗai guda 2. Wannan daidai yake da 400 + 50 + 2.
- A umurci wani ɗalibi ya zo gaban aji ya rubuta 231 a cikin fasali mai faɗi.
- Bayan an mayar da dukkan lambobin biyu a cikin fasali mai faɗi, sai a tara su wuri guda.
- **Ka/ki ce:** *Idan muka tara lambobi a cikin fasali mai faɗi, da farko muna buƙatar tara lambobin gurbin gidan ɗaiɗai wuri ɗaya. Waɗanne lambobi ne suke a gurbin gidan ɗaiɗai?*
- A tara 1 + 2 wuri ɗayasai a rubuta 3 a ƙasan layin.
- **Ka/ki ce:** *Abu na gaba sai mu tara gwammanmu wuri guda. Mene ne amsar 50 + 30?*
- A rubuta 80 a ƙasan layin, a ƙarkashin 50 + 30.
- **Ka/ki ce:** *A ƙarshe, za mu tara ɗaruruwan wuri guda. Mene ne amsar 400 + 200?*
- A rubuta 600 a ƙasan layin.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu fasalin lissafinmu ya kammala, muna iya tara lambobinmu wuri guda. Mene ne amsar 600 + 80 + 3?*
- Idan ɗalibai suna buƙatar taimako, a umurce su da su duba jadawalin lambobi 1-100 dake kan allo a gaban aji. A yi bayanin cewa 452 + 231 daidai yake da 600 + 80 + 3.

```
452 + 231

 400 + 50 + 2
 200 + 30 + 1

  400 + 50 + 2
+ 200 + 30 + 1
             3

  400 + 50 + 2
+ 200 + 30 + 1
        80 + 3

  400 + 50 + 2
+ 200 + 30 + 1
   600+ 80 + 3

  400 + 50 + 2
+ 200 + 30 + 1
   600+ 80 + 3 = 683
```

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: Tara Kwallin Lambobi 3 a cikin Fasali Mai Faɗi (minti 15)

- A umurci ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 38. A karanta umurni da aka rubuta a bayyane ga ɗalibai a kuma kammala lissafin farko da ajin.
- A umurci ɗalibai su kammala sauran lissafi 2 na gaba dake kan shafin. Suna iya aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma tare da abokan zamansu. A zagaya ana lura da ɗalibai a kuma taimaka musu.

## Bayyanawa

Nuna kyawawan misalai (minti 5)

- A bayyana wa sauran ɗalibai ƙwararan misalan da ɗalibi ya bayar.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 38 a cikin littafansu na aiki a matsayin aikin gida.

| Na. 83 | Zango na 2, Mako na 5, Darasi na C |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su tara ƙwallin lambobi 3 ta lissafin tsaye da kuma lissafin kwance.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)
- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)
- Rera waƙar tare da ɗalibai sau da yawa.

Waƙar Tarawa
Ana batun tarawa /
Komai a tara da ɗaya /
1+1= 2 / 2+1= 3 / 3+1= 4 /
4+1= 5 / 5+1= 6 / 6+1= 7 /
7+1= 8 / 8+1= 9 / 9+1= 10

**Koyo**

Tarawa ta lissafin kwance (minti 7)

346 + 152 = 498

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu yi gwajin tara ƙwallin lambobi 3 ta lissafin kwance da kuma lissafin tsaye.*
- A rubuta : 346+ 152 = ____ a kan allo.
- ***Ka/ki ce:*** *Da farko, a tara lambobin dake gurbin gidan ɗaiɗai wuri guda. Lambobi ɗaiɗai nawa gare mu?*
- A yi da'ira ga 6 da kuma 2 a cikin dukkan lambobin biyu, sannan a tambayi ɗalibai mene ne amsar 6 + 2. A rubuta lambar 8 a gurbin gidan ɗaiɗai a kan layin da ake sa amsa.
- **Ka/ki ce:** *Abu na gaba, sai mu tara lambobin dake gurbin gidan gwammai wuri guda. Gwammai nawa ne a wurin?*
- A yi da'ira ga 4 da kuma 5. A nemi ɗalibai su faɗi mene ne amsar 4 + 5. A rubuta lamba ta 9 a gurbin gidan gwammai.
- **Ka/ki ce:** *Daga ƙarshe, a tara lambobin dake gurbin gidan ɗaruruwa. Ɗaruruwa nawa ne wurin?*
- A yi da'ira ga 3 da kuma 1. A umurci ɗalibai su faɗi mene ne amsar 3 +1 . A rubuta lamba 4 a gurbin gidan ɗaruruwa.
- **Ka/ki ce:** *346 a tara da 152 zai ba da 498.*

Tarawa ta lissafin tsaye (minti 8)

$$\begin{array}{r} 346 \\ +\ 152 \\ \hline 498 \end{array}$$

- **Ka/ki ce:** *A matakin farko na warware fasalin lissafin tsaye shi ne tara lambobin dake gurbin gidan ɗaiɗai wuri ɗaya, sannan a tara na gurbin gidan goma-goma, sannan sai a tara na gurbin gidan ɗari-ɗari wuri guda.*
- A nuna lambobin 2 da kuma 6 sannan sai a rubuta lamba 8 a ƙarƙashin fasalin lissafin.
- A nuna lambobin 4 da kuma 5 sannan sai a rubuta lamba 9 a ƙarƙashin fasalin lissafin.
- A nuna lambobin 3 da kuma 1 sannan sai a rubuta lamba 4 a ƙarƙashin fasalin lissafin.
- **Ka/ki ce:** *346 a tara da 152 zai ba da 498.*

**Gwaji**

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: Tara Lambobi ta lissafin tsaye ko lissafin kwance (minti 10)
- A umurci ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 39. A karanta umurni da aka rubuta a bayyane ga ɗalibai a kuma kammala lissafin farko da ajin.
- A umurci ɗalibai su kammala sauran lissafi 2 na gaba dake kan shafin. Suna iya aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma tare da abokan zamansu. A zagaya ana lura da ɗalibai a kuma taimaka musu.

**Bayyanawa**

Auna fahimta nan-take (minti 5)
- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu sama, su nuna abun da suka rubuta. A yaba wa ƙwazonsu.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 39 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

**Na. 84**

# Zango na 2, Mako na 5, Darasi na D

**Manufofi:** Ɗalibai za su warware matsalolin da aka rubuta da kalmomi ta amfani da tarawa.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai sau da yawa.

Waƙar Tarawa
Ana batun tarawa /
Komai a tara da ɗaya /
1+1= 2 / 2+1= 3 / 3+1= 4 /
4+1= 5 / 5+1= 6 / 6+1= 7 /
7+1= 8 / 8+1= 9 / 9+1= 10

## Koyo

Gabatar da Warware Lissafi na Kalmomi ta Amfani da Tarawa (minti 10)

- Bayyana wannan labarin: *An baiwa Nura da Rabiu aikin raba biskit ga ɗalibai. A ranar Litinin sun bayar da biskit 341, a ranar Talata suka bayar da biskit 313. Biskit nawa suka bayar gaba ɗaya?*
- A kira ɗalibai guda biyu su zo gaban aji, su yi kwaikwayon labarin. A sa ɗalibi ɗaya ya rubuta jimillar yawan biskit ɗin da suka raba a ranar Litinin, wani ɗalibin ɗaya kuwa ya rubuta jimillar yawan biskit ɗin da aka raba a ranar Talata.
- **Ka/ki ce:** *Nura da Rabiu sun bayar da biskit 341 a rana farko da kuma 313 a rana ta biyu. Idan muna son mu gano yawan biskit din da aka raba gaba daya, dole ne sai mun tara wadannan lambobin wuri guda.*
- A kira wani ɗalibi ya zo gaban aji ya kuma rubuta fasalin lissafin dake nuna wannan labarin.
- Ka/ki tabbata an rubuta 341 + 313 = a kan allo.
- A umurci wani ɗalibi ya zo gaban aji ya yi gwajin yadda ake tara lambobin ta lissafin kwance, sannan a umurci wani ɗalibi daban ya yi gwajin yadda ake tara lambobin ta lissafin tsaye.
- A yi bitar yadda 341 + 313 = 654 tare da ɗalibai.

## Gwaji

Aiki a cikin ƙaramin rukuni: Warware lissafi na rubutu ta amfani da tarawa (minti 15)

- A umurci ɗalibai su zauna a cikin ƙananan rukunai.
- **Ka/ki ce:** *A ƙauyensu Naija akwai mata 334. Wasu mata 202 sun zo ƙauyensu Naija daga wani ƙauye da suke maƙwabtaka wajen biki. Mata nawa ne suke wurin bikin gaba ɗaya?* (Amsa: 536)
- A maimaita faɗin lissafi ta kalmomi sau da yawa don tabbatar da ɗalibai sun ji lambobin da aka faɗi.
- A sa ɗalibai su rubuta fasalin lissafi a cikin littafansu na rubutu a ɗaiɗaikunsu.
- Da zarar ɗaliban sun gama rubuta fasalin lissafin, a sa ɗalibai su yi aiki tare don su warware lissafi. Za su yi gwajin warware lissafin na kalmomi a fasalin lissafin kwance da kuma lissafin tsaye.
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai a kuma taimaka masu. Idan da lokaci, a maimaita da wata lissafin daban.

## Bayyanawa

Bita da Bayyanawa (minti 5)

- A samu wasu 'yan sa-kai su warware lissafin a kan allo, su kuma yi bayanin yadda suka warware ta. A umurci ɗalibai su ɗaga babban yatsansu sama idan sun aminta da amsar.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su warware lissafin 111 + 181 = a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

**Na. 85**

# Zango na 2, Mako na 5, Darasi na E

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi bita da gwajin abun da suka koya a cikin wannan makon.
**Kayan Aiki:** Littafan Yara **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai sau da yawa.

Waƙar Tarawa
Ana batun tarawa /
Komai a tara da ɗaya /
1+1= 2 / 2+1= 3 / 3+1= 4 /
4+1= 5 / 5+1= 6 / 6+1= 7 /
7+1= 8 / 8+1= 9 / 9+1= 10

## Koyo

Bita da maimai (minti 10)

- A zaɓi wani darasi daga cikin darrusan da aka yi a cikin makon, wanda ake ganin ɗalibai ba su fahimce shi sosai ba. A sake koyar da darasin ko a sake koyar da shi ta wata sabuwar hanya daban.

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai da aikin ɗalibai a cikin rukuni: Tara Lambobi ‘Yan Uku (minti 15)

- A ba ɗalibai aikin da zai taimaka masu wajen yin gwajin darasin da aka yi bita (alal misali; tara lambobi ‘yan uku ta lissafin tsaye ko kuma lissafin kwance).
- Ɗalibai na iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma a cikin ƙananan rukunai.
- Yayin da ɗalibai suke gudanar da wani aikin da aka ba su, a ƙara taimaka masu a inda ba su gane sosai ba.

## Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala a lokacin Gwajin.

## Aikin Gida

A ba ɗalibai aikin gida na bita da kuma gwajin ƙwazonsu.

| Na. 86 | Zango na 2, Mako na 6, Darasi na A |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su yi taƙaitacciyar jarabawar gwaji ta lissafi.
**Kayana Aiki:**

**JARRABAWAR GWAJI**

Ka yi wa ɗalibai jarabawar gwaji ta kai-tsaye da kuma rubuta makin da suka samu a cikin littafinka na ajiye bayanai. Idan akwai buƙata, ka nemi taimakon Jagoran Malamai da SBMC ko kuma wasu malamai domin gudanar da jarabawar.

Ka bayar da wani aikin gwaji ga ɗalibanka yayin da suke jiran a fara jarabawar gwajin. Alal misali; ɗalibai suna iya yin gwajin ɓangare ɗayako tara ƙwallin lambobi 2 ko kuma ƙwallin lambobi 3.

| **Jaha:** | | **Karamar hukuma:** | | **Makaranta:** | | **Wata:** | | **Shekara:** | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|


| Lamba | Sunan Ɗalibi | Jinsi | Shekaru | Buƙata ta musamman (Eh/A'a) | Tarawa | Juzu'i | Jimillar maki |
|---|---|---|---|---|---|---|---|
| | | | | | /6 | /9 | / 15 |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |


**Darasin Lissafi Aji 2, Zango na 2, Mako na 6 – Jarrabawar tsakiyar Zango**


**Tara waɗannan lambobi za a iya amfani da fensiri da takarda.** (A bayar da maki uku ga kowace amsa)

| | |
|---|---|
| 82 | 34 |
| + 12 | + 21 |

**Tantance yawan ɓangaren da aka tura.** (A bayar da maki uku ga kowace amsa)







| Na. 87 | Zango na 2, Mako na 6, Darasi na B |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su raba abubuwa a cikin kashi ½ da kuma 1/4.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)
- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa gwiwa.


Naɗe kashi 1/2 da kuma 1/4 (minti 3)
- A sa ɗalibai su fito da fallen takarda ɗaya. A sa ɗalibai su naɗe takardarsu rabi. Daga nan sai su yi musaya da abokan zamansu su kuma naɗe fallen takardar a cikin ɓangarori huɗu.

**Koyo**

Wasan aji gaba ɗaya: Rarraba abubuwa a cikin rabi-rabi da kuma kashi ɗaya bisa huɗu (minti 10)
- A kira ɗalibai 20 su zo gaban aji. A umurcirukunin ɗaliban da su raba kansu gida biyu. A tuna masu cewa dole ne yawansu ya zama daidai.
- A umurci ɗalibai su faɗi ɗalibai nawa ne ke cikin kowane rukuni.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu mun ga cewa ½ na 20 shi ne 10.*
- Yanzu, a sake neman rukunin ɗaliban biyu da su tsaya tare wuri guda su samar da 20. A umurci ɗaliban da su raba kansu a cikin gida huɗu. A tuna masu cewa dole ne yawan kowane gida huɗun ya zama daidai.
- A maimaita da wasu lambobi (alal misali; a kira ɗalibai 12 ko ɗalibai 4 su zo gaban aji).

**Gwaji**

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: Zana Hotunan rabi-rabi da kuma kwata-kwata (minti 15)



- A zana hotunan sifofi a kan allo.
- A umurci ɗalibai su rubuta sifofin a cikin littafansu na rubutu.
  Bayan sun gama rubuta dukkan sifofin, a sa ɗalibai su sa kala a kashi ɗaya bisa huɗu na kowane daga cikin sifofin.
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai. A yayin zagayawar, a tambaye su yadda suka samo amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.
- Abu na gaba, a sa ɗalibai su sanya kala ga rabin kowane ɗaya daga cikin sifofin.
- A umurci dalibai su duba amsarsu da ta abokan zamansu.

**Bayyanawa**

Auna fahimta nan-take (minti 5)
- A sa ɗalibai su ɗaga littafansu na rubutu sama, su nuna abun da suka sanya wa kala. A yaba wa ƙwazonsu.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su zana hoton da'ira a cikin littafansu na rubutu su kuma sa kala ga kashi ɗaya bisa huɗu na hoton.

**Na. 88**

# Zango na 2, Mako na 6, Darasi na C

**Manufofi:** Ɗalibai za su raba abubuwa a cikin kashi 1/3 da 2/3 da 1/5 da kuma 1/6.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

<u>Duba aikin gida (minti 2)</u>

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

<u>Naɗe 1/3 (minti 3)</u>

- A sa ɗalibai su fito da fallen takarda ɗaya. A sa ɗalibai su naɗe takardarsu uku. Daga nan sai su yi musaya da abokan zamansu sannan sai a nemi su zana hoton da’ira a kan kashi 2/3 na takardar.


## Koyo

<u>Wasan aji gaba ɗaya: Rarraba abubuwa a cikin kashi ɗaya bisa uku da kashi ɗaya bisa biyar da kuma kashi ɗaya bisa shida (minti 10)</u>

- A sa ɗalibai su fita waje. Ka/ki kira ɗalibai 30 su tsaya a gabanka/ki. Nemi rukunin su raba kansu a cikin kashi uku. A tuna masu cewa dole ne yawan rukunan uku ya zama daidai.
- A umurci ɗalibai su faɗi ɗalibai nawa ne ke cikin kowane rukuni.
- **Ka/ki ce:** *Mun ga cewa 1/3 na 30 shi ne 10. Nawa 2/3 na 30 zai kasance? Ɗalibai nawa ne ke cikin rukunai biyu?*
- A gaba, a sa rukunin ɗaliban su sake tsayawa tare wuri ɗaya su samar da 30. A sa ɗaliban su raba kansu a cikin kashi biyar. A yi ƙirge a bayyane tare da ɗalibai don a tabbatar da akwai ɗalibai 6 a cikin kowane rukuni.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu mun ga cewa 1/5 na 30 shi ne 6.*
- Ka/ki sake maimaitawa, ta hanyar neman ɗalibai su raba kansu a cikin gida shida.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu mun ga cewa 1/6 na talatin shi ne 5.*

## Gwaji

<u>Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: Zana Hotunan kashi ɗaya bisa uku da kashi ɗaya bisa biyar da kuma kashi ɗaya bisa shida (minti 15)</u>



- A zana hotunan sifofi a kan allo.
- A nemi ɗalibai su rubuta sifofin a cikin littafansu na rubutu.
  Bayan sun gama rubuta dukkan sifofin, a sa ɗalibai su sa kala ga kashi 1/3 na da’ira da ɗaya bisa biyar na sifar akwati da kuma kashi 1/6 na sifar gidan dara. Ɗalibai na iya duba amsarsu da ta abokan zamansu.
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai. A yayin zagayawar, a tambaye su yadda suka samo amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.

## Bayyanawa

<u>Auna fahimta nan-take (minti 5)</u>

- A sa ɗalibai su ɗaga littafansu na aiki sama, su nuna abun da suka sanya wa kala. A yaba wa ƙwazonsu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su zana hoton da’ira a cikin littafansu na rutubutusu kuma sa kala ga 2/3 na hoton.

| Na. 89 | Zango na 2, Mako na 6, Darasi na D |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su rubuta ƙwallin lambobi 2 da kuma ƙwallin lambobi 3 a cikin fasali mai faɗi.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai sau da yawa.

Waƙar Tarawa
Ana batun tarawa /
Komai a tara da ɗaya /
1+1= 2 / 2+1= 3 / 3+1= 4 /
4+1= 5 / 5+1= 6 / 6+1= 7 /
7+1= 8 / 8+1= 9 / 9+1= 10

## Koyo

Bita: Rubuta ƙwallin lamba 3 a cikin fasali mai faɗi (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu yi bitar rubuta lambobi a cikin fasali mai faɗi. Za mu yi lissafi ɗaya tare daga nan sai ku yi aikin sauran lissafin da kanku ko tare da abokan zamanku.*

☐ɗari-ɗari + ☐ goma-goma + ☐ɗaiɗai = 365

- A rubuta 365 a kan allo sai a nemi ɗalibai su faɗi ƙwallin lambobi nawa ke ciki.
- **Ka/ki ce:** *Akwai ƙwallin lambobi 3 a ciki, saboda haka muna da lamba a gurbin ɗari-ɗari da gurbin goma-goma da kuma gurbin ɗaiɗai.*
- A umurci ɗalibai su faɗi ɗaruruwa nawa ke ciki.
- **Ka/ki ce:** *Haka ne, akwai ɗaruruwa 3 a cikin 365, saboda haka muna iya rubuta lambar 3 a cikin akwatin farko. Ɗari-ɗari 3, daidai suke da 300.*

Ɗari-ɗari 3 + goma-goma 6 + Ɗaiɗai 5 = 365
300 + 60 + 5 = 365

- **Ka/ki ce:** *A gaba, wace lamba ce ke gurbin gidan gwammai? Goma-goma nawa muke da su?*
- A kira wani ɗalibi ya zo gaban aji sannan a ba shi dama ya sa lamba ta 6 a gurbin gidan gwammai.
- **Ka/ki ce:** *Haka ne, muna da 6 guda goma. 6 guda goma daida suke da 60.*
- **Ka/ki ce:** *A ƙarshe, ɗaiɗai guda nawa muke da su? Wace lamba ce za a sa a gurbin gidan ɗaiɗai?*
- A kira wani ɗalibi ya zo gaban aji sannan a ba shi dama ya sa lamba ta 5 a cikin gurbin ɗaiɗai.
- **Ka/ki ce:** *Haka ne, ɗaiɗai guda 5 daidai suke da 5. Yanzu kasancewar duk mun kammala rubuta lambobinmu a cikin fasali mai faɗi, muna iya haɗa lambobinmu uku wuri ɗaya, don mu gano yawan karan da muke da su.*
- A warware lissafin a300 + 60 + 5 kan allo tare da ajin.

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu: Rubuta Kwallin Lambobi 2 da kuma Kwallin Lambobi 3 a cikin Fasali mai Faɗi (minti 15)

- A umurci ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 40. A karanta umurni da aka rubuta a bayyane ga ɗalibai a kuma kammala lissafin farko da ajin.
- A umurci ɗalibai su kammala sauran lissafi 2 na gaba dake cikin littafin rubutu.
- A zagaya ana lura da aikin ɗalibai. A yayin zagayawar, a tambaye su yadda suka samo amsar tasu, a kuma duba ko sun amsa daidai.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga littafansu na rubutu sama, su nuna abun da suka rubuta. A yaba wa ƙwazonsu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 40 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 90 | Zango na 2, Mako na 6, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi bitar tara ƙwallin lambobi 2 da kuma ƙwallin lambobi 3 a cikin fasalin lissafin tsaye da kuma lissafin kwance.

**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Rera waƙar tare da ɗalibai sau da yawa.

Waƙar Tarawa
Ana batun tarawa /
Komai a tara da ɗaya /
1+1= 2 / 2+1= 3 / 3+1= 4 /
4+1= 5 / 5+1= 6 / 6+1= 7 /
7+1= 8 / 8+1= 9 / 9+1= 10

## Koyo

Tara ƙwallin lambobi 3 ta lissafin kwance (minti 7)

- **Ka/ki ce:** *A yau za mu yi gwajin tara ƙwallin lambobi 2 da kuma 3 ta lissafin kwance da kuma lissafin tsaye. Za mu yi lissafi ɗaya tare daku daga nan sai ku yi sauran ayyukan a ɗaiɗaikunku ko kuma tare da abokan zamanku.*
- A rubuta: 214 + 562 = a kan allo.

214 + 562 = 776

- ***Ka/ki ce:*** *Da farko, a tara lambobin dake gurbin gidan ɗaiɗai wuri ɗaya. Lambobi ɗaiɗai nawa gare mu?*
- A saka da'ira ga 4 da kuma 2 a cikin dukkan lambobin biyu. A tambayi ɗalibai mene ne amsar 4 + 2. A rubuta lambar 6 a gurbin gidan ɗaiɗai a kan layin da ake sa amsa.
- **Ka/ki ce:** *Abu na gaba, sai mu tara lambobin dake gurbin gidan Goma-goma wuri guda. Goma-goma nawa ne a wurin?*
- A yi da'ira ga 1 da kuma 6. A umurci ɗalibai su faɗi mene ne amsar 1 + 6. A rubuta lamba ta 7 a gurbin gidan goma-goma.
- **Ka/ki ce:** *Daga ƙarshe, a tara lambobin dake gurbin gidan ɗari-ɗari. Ɗari-ɗari nawa ne wurin?*
- A umurci da'ira ga 2 da kuma 5. A umurci ɗalibai su faɗi mene ne amsar 2 + 5. A rubuta lamba 7 a gurbin gidan ɗaruruwa.
- **Ka/ki ce:** *214 a tara da 562 zai ba da 776.*

```
  214
+ 562
  776
```

Tarawa ta lissafin tsaye (minti 8)

- **Ka/ki ce:** *A matakin farko muna warware lissafin tsaye ta hanyar tara lambobin dake gurbin gida ɗaiɗai wuri ɗaya, sannan mu tara na gurbin gidan goma-goma, sannan sai mu tara na gurbin gidan ɗari-ɗari wuri ɗaya.*
- A nuna lambobin 4 da kuma 2 sannan sai a rubuta lamba 6 a ƙarƙashin fasalin lissafin.
- A nuna lambobin 1 da kuma 6 sannan sai a rubuta lamba 7 a ƙarƙashin fasalin lissafin.
- A nuna lambobin 2 da kuma 5 sannan sai a rubuta lamba 7 a ƙarƙashin fasalin lissafin.
- **Ka/ki ce:** *214 a tara da 562 zai ba da 776.*

## Gwaji

Aikin ɗaiɗaikun ɗalibai ko aikin ɗalibai bibbiyu:Tarawa ta Lissafin tsaye da kuma lissafin kwance (minti 15)

- A umurci ɗalibai su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 41. A karanta umurni da aka rubuta a bayyane ga ɗalibai a kuma kammala lissafin farko da ajin.
- A umurci ɗalibai su kammala sauran lissafi 2 na gaba dake cikin littafin ɗalibai dake shafin. Suna iya aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma tare da abokan zamansu. A zagaya ana lura da aikin ɗalibai a kuma taimaka musu.

## Bayyanawa

Auna fahimta nan-take (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga littafansu na rubutu sama, su nuna abun da suka rubuta. A yaba wa ƙwazonsu.

## Aikin Gida



A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 41 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 91 | Zango na 2, Mako na 7, Darasi na A |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su rubuta tagwayen lambobi da 3 ta hanyar faɗaɗawa.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Waƙar Tarawa
Ana batun tarawa /
Komai a tara da ɗaya /
1+1= 2 / 2+1= 3 / 3+1= 4 /
4+1= 5 / 5+1= 6 / 6+1= 7 /
7+1= 8 / 8+1= 9 / 9+1= 10

**Koyo**

Bita: Rubuta tagwayen lambobi 3 ta hanyar faɗaɗawa (minti 10)

☐ɗari-ɗari + ☐ goma-goma + ☐ɗaiɗaya = 113

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi bitar rubutun lambobi ta hanyar faɗaɗawa. Za mu samo amsa ɗaya tare da ku sannan za ku gano sauran amsoshin da kanku ko da abokan aikinku.*
- Rubuta lamba 113 a kan allo, sannan a tambayi ɗalibai ƙwallin lamba nawa ne.
- **Ka/ki ce:** *Akwai ƙwalli 3, saboda haka muna da lamba a gidan ɗari-ɗari da gidan goma-goma da kuma gidan ɗaiɗaya.*
- A tambayi ɗalibai ɗari-ɗari nawa ake da su.
- **Ka/ki ce:** *Haka ne, akwai ɗari 1 a cikin 113, saboda haka za mu saka lamba 1 a cikin akwatin farko. ɗari 1 daidai yake da 100.*

ɗari 1 + goma 1 + ɗaiɗaya 3 = 113
100 + 10 + 3 = 113

- **Ka/ki ce:** *Daga nan kuma, wace lamba ce a gidan goma-goma? Goma-goma nawa muke da su?*
- Kira ɗalibi/ɗaliba ɗaya ya/ta fito gaban allo don saka lamba 1 a gidan goma-goma.
- **Ka/ki ce:** *Haka ne muna da goma 1. Goma 1 daidai take da 10.*
- **Ka/ki ce:** *Daga ƙarshe, ɗaiɗaya nawa muke da su? Wace lamba za mu saka a gidan ɗaiɗaya?*
- Kira ɗalibi/ɗaliba ɗaya ya/ta fito gaban allo don saka lamba 3 a gidan ɗaiɗaya.
- **Ka/ki ce:** Haka ne*, ɗaiɗaya 3 shi ne 3. Tun da yanzu muna da dukkan lambobinmu a rubuce ta hanyar faɗaɗawa, za mu iya tara dukkan lambobi uku a wuri guda mu samo jimillar tsinken da ake da su.*
- A gano wannan amsar 100 + 10 + 3 a kan allo tare da 'yan aji.

**Gwaji**

Aiki a ɗaiɗaiku da kuma cikin bibiyu: Rubutun tagwayen lambobi da 3 ta hanyar faɗaɗawa (minti 15)

- A ce ɗaliban su buɗe Shafi na 42. A karanta wa ɗalibai umurni sannan a samo amsar aikin lissafin farko tare da su.
- A sa ɗalibai su gano amsar fasalin lissafi biyu na gaba da ke cikin littafin ɗalibai.
- A zagaya domin lura da ɗalibai. Yayin da ake zagayawa, a riƙa tambayar ɗalibai yadda suka sami amsoshinsu. A tabbatar masu idan amsarsu daidai ne.

**Bayyanawa**

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu don su nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 42 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 92 | Zango na 2, Mako na 7, Darasi na B |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su tara tagwayen lambobi tare da ragowa.
**Kayan Aiki:** Daurin tsinke **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.


Rerawa (minti 3)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

> Waƙar Tarawa
> Yi ƙari har zuwa har
> sannan komai zai yi kyau.
> 10 ko sama da haka sai a
> kai gida na gaba!
> Za mu iya! Za mu iya!

**Koyo**

Tara tagwayen lamba tare da ragowa – tsarin kwance (minti 10)




- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi yadda za a tara tagwayen lambobi tare da ragowa. Sauya suna ana nufin tara lambobi daidaya yadda za su koma goma-goma.*
- Rubuta wannan fasalin lissafin 25 + 26 = ___ a kan allo.
- Nuna lamba 25 kamar yadda suka fito a wurin ƙimar lamba ta hanyar saka dami 2 na tsinke a wurin goma-goma (wanda take wakiltar siffar akwati) da kuma tsinke guda 5 a gidan ɗaiɗaya ( wanda ake wakiltar siffar gidan dara).
- Gwada yadda za a tara da ƙarin 26, ta hanyar zana siffar akwati guda 2 su wakilci dami guda wato goma da kuma sifar gidan dara 6 ya wakilci ɗaiɗaya guda 6.
- **Ka/ki ce:** *Tun da yanzu an sami wakilci lambobi 25 da 26 a cikin jaddawalin, sai kuma mu tara su wuri guda.*
- A sa ɗalibai su ƙirga adadin siffar gidan dara da ke gidan ɗaiɗaya.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu akwai tsinke 11 a gidan ɗaiɗaya. Me ya kamata mu yi?*
- **Ka/ki ce:** *Ku tuna, duk lambar da ta wuce 9 ba za ta zauna a gidan ɗaiɗaya ba. ɗaiɗaya guda goma daidai suke da goma 1, saboda haka sai mu canza gidan dara 10 zuwa sifar akwati 1.*
- **Ka/ki ce:** *Saboda haka za a sami goma 5 a gidan goma-goma da kuma 1 a gidan ɗaiɗaya. Saboda haka 25 + 26 = 51.*

**Gwaji**

Aikin ƙananan rukunoni: Tara tagwayen lamba tare da ragowa (minti 15)

- A sa ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunoni sannan su buɗe litattafansu zuwa jaddawalin ƙimar lamba da ke farkon littafin. A zaɓi shugaba ɗaya daga kowane rukuni don su taimaka wajen raba dami-damin tsinke ga ʻyan rukuninsu.
- Rubuta lissafi na 43 + 38 a kan allo, sannan a sa ɗalibai su gano amsar wannan fasalin lissafin a cikin litattafansu na rubutu ta hanyar amfani da jaddawalin ƙimar lamba.
- Zagaya domin lura da ɗalibai sannan a tallafa masu.

**Bayyanawa**

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu don su nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su samo amsar 22 +39 a cikin litattafansu na rubutu a gida.

| Na. 93 | Zango na 2, Mako na 7, Darasi na C |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su tara tagwayen lambobi ta hanyar jera lambobin a tsaye da kuma kwance.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Rerawa (minti 3)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Waƙar Tarawa
Yi ƙari har zuwa har
sannan komai zai yi kyau.
10 ko sama da haka sai a
kai gida na gaba!
Za mu iya! Za mu iya!

## Koyo

Tara tagwayen lambobi da ragowa – ta hanyar jera lambobin a tsaye (minti 10)

- Ka/ki ce: Yau za mu gwada tara tagwayen lambobi tare da ragowa. Mun gwada tara tagwayen lambobi ta hanyar jera su a tsaye jiya. A yau kuma za mu tara lambobin a kwance.
- Rubuta wannan fasalin lissafin 25 + 26 = ___ a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Kada a manta, yayin da muka zo tara lambobi a kwance, a kullum muna farawa da lambobin da ke gidan ɗaiɗaya. Mene ne 5 + 6?*
- A yi bayanin ɗaiɗaya guda 11 yana nufin goma guda ɗaya da kuma ɗaiɗaya guda ɗaya. Nuna wa ɗalibai yadda za a gane "1" na ɗaiɗaya, sannan a ɗauki wata "1" zuwa gidan goma-goma.
- A sa wani ɗalibi/ ɗaliba ya/ta fito gaban allo domin tara 1 + 2 + 2 wuri guda a gidan goma-goma. A tabbatar an rubuta 5 a ƙasan layi a hagun da 1.
- **Ka/ki ce:** *25 + 26 = 51.*

## Gwaji

Aiki a ɗaiɗaiku ko cikin bibiyu: Tara tagwayen lambobi da mayar da ɗaiɗaiku goma-goma (minti 15)

- A ce ɗaliban su buɗe Shafi na 43. A karanta wa ɗalibai umurni sannan a samo amsar aikin lissafin farko tare da su.
- A sa ɗalibai su gano amsar fasalin lissafi biyu na gaba da ke cikin littafin ɗalibai. Za su iya aiki a ɗaiɗaiku ko da abokin aiki
- A zagaya domin lura da ɗalibai. Yayin da ake zagayawa, a riƙa tambayar ɗalibai yadda suka sami amsoshinsu. A tabbatar masu idan amsarsu daidai ne.

## Bayyanawa

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu don su nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 43 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 94 | Zango na 2, Mako na 7, Darasi na D |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya warware aikin lissafi ta hanyar tarawa.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Wakar Tarawa
Yi kari har zuwa har
sannan komai zai yi kyau.
10 ko sama da haka sai a
kai gida na gaba!
Za mu iya! Za mu iya!

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a karfafa masu gwiwa.

Rerawa (minti 3)

- A yi ta rera wakar tare da ɗalibai.

**Koyo**

Warware aikin lissafi tare da ragowa (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi lissafi ta hanyar tarawa da kuma ragowa.*
- Faɗa wa ɗalibai labarin da ke biye: Shugaban makaranta ya sa Zahra da Auwal su kirga ɗaliban da ke cikin ajinsu. Zahra ta kirga yara mata 38 shi kuma Auwal ya kirga yara maza 36. Jimillar ɗalibai nawa ake da su?
- Umurci ɗalibai biyu su fito gaban aji su kwatanta aiwatar da labarin. A sa ɗaya ya/ta rubuta adadin yara mata sannan ɗayan kuma ya/ta rubuta adadin yara maza a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Akwai yara mata 38 da yara maza 36. Idan muna son gano jimillar yara sai mu tara waɗannan lambobi wuri ɗaya.*
- A sa wani ɗalibi/ ɗaliba ya/ta fito fito gaban allo ya/ta rubuta fasalin lissafin da labarin ya kunsa.
- A tabbatar an rubuta 38 + 36 = a kan allo.
- A sa ɗalibi/ ɗaliba ɗaya ya/ta fito gaban aji ya gwada yadda za a tara lambobin yayin da aka jera su a tsaye ta hanyar ragowa, sannan ɗaya kuma ya/ta gwada tara lambobin yayin da aka jera su a kwance ta hanyar ɗaukar lamba.
- A yi bita tare da ɗalibai 38 + 36 = 74.

**Gwaji**

Aiki a kananan rukunoni: Warware aikin lissafi tare da ragowa (minti 15)

- A sa ɗalibai su zauna cikin kananan rukunoni.
- **Ka/ki ce:** *Akwai shanu 29 a gona. Mai gonar ya karo wasu 18. Yanzu duka-duka shanunsa sun zama nawa?* (Amsa: 47)
- Yi ta maimaita lissafin da aka bayar don a tabbatar ɗalibai sun ji dukkan lambobin da ake magana a kai.
- A sa ɗalibai su rubutafasalin lissafin a cikin littafansu na rubutu a ɗaiɗaikunsu.
- Da zarar ɗaliban su rubuta lissafin, su haɗa kai wajen gano amsoshin. Su gwada gano amsoshin lissafin ta hanyar zuba lissafin a tsaye da kwance.
- A zagaya domin lura da ɗalibai sannan a ba su tallafi. Idan akwai lokaci, a maimaita da wani lissafin.

**Bayyanawa**

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa wasu 'yan sa kai su gano amsar wannan lissafin da ke kan allo sannan su yi bayanin yadda suka gano amsoshinsu. A sa ɗalibai su ɗaga babban yatsansu sama idan sun aminta da amsar.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su gano amsar wannan aikin lissafin 77 + 14 = a cikin litattafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 95 | Zango na 2, Mako na 7, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za suyi bita da gwajin aikin da aka gabatar a makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)
- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa. (Amsa: 91)

Rerawa (minti 3)
- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Waƙar Tarawa
Yi ƙari har zuwa har
sannan komai zai yi kyau.
10 ko sama da haka sai a
kai gida na gaba!
Za mu iya! Za mu iya!

**Koyo**

Bita da maimaitawa (minti 10)
- Zaɓi wani batu daga ayyukan mako da ake ganin kamar ɗalibai suna fama da shi. A sake maimaita koyar da shi ko kuma a koyar da shi ta wata hanyar daban.

**Gwaji**

Aiki a ɗaiɗaiku da kuma cikin ƙungiyoyi: Tara tagwayen lambobi tare da sake ragowa (minti 15)
- A ba wa ɗalibai wani aiki wanda zai taimaka masu gwajin abin da ake bita a kansa (Misali, gano amsar lissafin ta hanyar tarawa). Ɗalibai za su iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma cikin rukunoni.
- Yayin da ɗalibai suke mayar da hankalinsu a kan aikinsu, a samar da taimako ga masu buƙata.

**Bayyanawa**

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)
- A sa ɗalibai su nuna ayyukan da suka kammala a lokacin gwaji.

**Aikin Gida**

A ba ɗalibai aikin gida don bita da gwajin abin da suka koya.

| Na. 96 | Zango na 2, Mako na 8, Darasi na A |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su tara tagwayen lambobi tare da ragowa.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.


Rerawa (minti 3)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Waƙar Tarawa
Yi ƙari har zuwa har
sannan komai zai yi kyau.
10 ko sama da haka sai a
kai gida na gaba!
Za mu iya! Za mu iya!

## Koyo

Tara tagwayen lamba tare da ragowa – tsarin kwance (minti 10)




- **Ka/ki ce:** *Yau za mu tara tagwayen lambobi lokacin da aka zuba lambobi a tsaye tare da ragowa.*
- Rubuta wannan fasalin lissafin 47 + 26 = ___ a kan allo.
- Nuna lamba 47 kamar yadda suka fito a wurin ƙimar lamba ta hanyar saka dami 4 na tsinke a wurin goma-goma (wadda aka wakiltar da siffar akwati) da kuma tsinke guda 7 a gidan ɗaiɗaya ( wadda aka wakiltar da siffar gidan dara).
- Gwada yadda za a tara da ƙarin 26, ta hanyar zana siffar akwati guda 2 su wakilci dami guda wato goma da kuma sifar gidan dara 6 ya wakilci ɗaiɗaya guda 6.
- **Ka/ki ce:** *Tun da yanzu an sami wakilci lambobi 47 da 26 a cikin jaddawalin, sai kuma mu tara su wuri guda.*
- A sa ɗalibai su ƙirga adadin siffar gidan dara da ke gidan ɗaiɗaya.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu akwai tsinke 13 a gidan ɗaiɗaya. Me ya kamata mu yi?*
- **Ka/ki ce:** *Ku tuna, duk lambar da ta wuce 9 ba za ta zauna a gidan ɗaiɗaya ba. ɗaiɗaya guda goma daidai suke da goma 1, saboda haka sai mu canza gidan dara 10 zuwa sifar akwati 1.*
- **Ka/ki ce:** *Saboda haka za a sami goma 7 a gidan goma-goma da kuma 3 a gidan ɗaiɗaya. Saboda haka 47 + 26 = 73.*

## Gwaji

Aikin ƙananan ƙungiyoyi: Tara lamba mai ƙwalli 2 tare da sake musu suna (minti 15)

- A sa ɗalibai su zauna cikin ƙananan ƙungiyoyi sannan su buɗe litattafansu zuwa jaddawalin ƙimar wurin lamba da ke farkon littafin. A zaɓi shugaba ɗaya daga kowane rukuni don su taimaka wajen raba dami-damin tsinke ga ʻyan rukuninsu.
- Rubuta lissafi na 64 + 18 a kan allo, sannan a sa ɗalibai su gano amsar wannan lissafin a cikin litattafansu na rubutu ta hanyar amfani da jaddawalin ƙimar lamba. (Amsa:82)
- Zagaya domin lura da ɗalibai sannan a tallafa musu.

## Bayyanawa

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu don su nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su samo amsar 45 + 76 a cikin litattafansu na rubutu a gida.

| Na. 97 | **Zango na 2, Mako na 8, Darasi na B** |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su tara tagwayen lambobi idan an jera su a tsaye ko kwance.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Rerawa (minti 3)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

> Waƙar Tarawa
> Yi ƙari har zuwa har
> sannan komai zai yi kyau.
> 10 ko sama da haka sai a
> kai gida na gaba!
> Za mu iya! Za mu iya!

### Koyo

Tara tagwayen lambobi idan an jera su a kwance da ragowa (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu tara tagwayen lambobi da ragowa. Jiya munga yadda aka jera lambobi a tsaye, yau kuma za mu tara lambobin da aka jera su a kwance.*
- Rubuta wannan fasalinlissafin 39 + 41 = ___ a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Kada a manta, yayin da za mu tara lambobi a kwance, a kullum muna farawa da wurin ɗaiɗaya ne. Mene ne 9 + 1?*
- A yi bayanin cewa ɗaiɗaya guda 10 yana nufin goma 1 kuma babu ɗaiɗaya. A nuna wa ɗalibai yadda za a ajiye "0" na ɗaiɗaya da kuma yadda za a tafi da "1" gidan goma-goma.
- **Ka/ki ce:** *Akwai goma 1 sannan babu ɗaiɗaya da ya rage. Saboda haka, sai a saka 0 a gidan ɗaidaya, sannan sai mu ɗauki 1 da muke da ita zuwa gidan goma-goma, sai mu ajiye ta a saman 3 da 4 da muke da su a a gidan goma-goma. Daga nan sai mu tara su gabaɗaya.*
- A sa ɗalibi ko ɗaliba ya/ta zo gaban allo domin tara 1 + 3 + 4 da ke gidan goma-goma. A tabbatar an rubuta 8 a ƙasan layin a hagun da 0.
- **Ka/ki ce:** *39 + 41 = 80.*
- Idan akwai lokaci a maimaita waɗannan matakan da fasalin lissafin 28 + 57.

```
  39
+ 41
----

 1
  39
+ 41
----
   0

 1
  39
+ 41
----
  80
```

### Gwaji

Aiki ɗaiɗaya ko cikin bibiyu: Tara tagwayen lambobi idan an jera su a tsaye ko a kwance (minti 15)

- A ce ɗaliban su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 44. A karanta wa ɗalibai umurni a bayyane. A ƙarasa gano lissafi na farko tare da su.
- A sa ɗalibai su gano amsar fasalin lissafi na gaba da ke cikin littafin ɗalibai. Za su iya aiki a ɗaiɗaiku ko da abokan aiki
- A zagaya domin lura da ɗalibai. Yayin da ake zagayawa, a riƙa tambayar ɗalibai yadda suka sami amsoshinsu. A tabbatar masu idan amsarsu daidai ne.

### Bayyanawa

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu don su nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai.

### Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 44 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 98 | Zango na 2, Mako na 8, Darasi na C |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su tara tagwayen lambobi guda 3 ko fiye da haka idan an jera su a tsaye ko a kwance.

**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.


Rerawa (minti 3)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

> Waƙar Tarawa
> Yi ƙari har zuwa har
> sannan komai zai yi kyau.
> 10 ko sama da haka sai a
> kai gida na gaba!
> Za mu iya! Za mu iya!

## Koyo

Tara tagwayen lambobi guda 3 ko fiye da haka idan an jera su a tsaye ko a kwance tare da ragowa (minti 15)




- **Ka/ki ce:** *Yau za mu tara tagwayen lambobi guda 3.*
- Rubuta wannan fasalinlissafin 13 + 16 + 62 = ___ a kan allo.
- A sa ɗalibai uku su fito gaban allo su cike jaddawalin wuraren ƙimar lamba da lambobin da suka dace na gidan goma-goma da ɗaiɗaya na kowace daga cikin waɗannan lambobi: 13 da 16 da kuma 62.
- **Ka/ki ce:** *Tun da yanzu an rubuta dukkan lambobin a jere, za mu iya tara su. Mu fara da lambobin da suke gidan ɗaiɗaya.*
- A sa ɗalibai su ƙirga yawan gidan dara da suke gidan ɗaiɗaya.
- **Ka/ki ce:** *Akwai tsinke 11 a gidan ɗaiɗaya. Yaya za mu yi kenan?*
- A tambayi ɗalibi/ ɗaliba ɗaya ya/ta fito gaban allo domin gwada aiwatar da yadda ake canza ɗaiɗaya guda 10 su koma goma 1.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu ya zama akwai goma-goma guda 9 da kuma ɗaiɗaya guda 1. Saboda haka 13 + 16 + 62 = 91.*
- Daga nan a rubuta wannan lissafin a kwance. A fara da ɗaiɗaya, a tambayi ɗalibai nawa ne 3+6+2.
- A sa ɗalibi/ɗaliba ɗaya ya/ta fito gaban allo domin nuna yadda za a tara ɗaiɗayan, a rubuta 1 a wurin ɗaiɗaya da ke ƙasan, sannan a tafi da 1.
- A sa wani ɗalibi/ ɗaliba ɗaya ya/ta fito gaban allo domin nuna yadda za a tara lambobin da ke gidan goma-goma.

## Gwaji

Aiki ɗaiɗaya ko cikin bibiyu: Tara tagwayen lambobi guda 3 idan an jera su a tsaye ko a kwance (minti 10)

- A ce ɗaliban su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 45. A karanta wa ɗalibai umurni a bayyane. A ƙarasa gano aikin lissafin na farko tare da su.
- A sa ɗalibai su gano amsar fasalinlissafi na gaba da ke cikin littafin ɗalibai. Za su iya aiki a ɗaiɗaiku ko da abokan aiki
- A zagaya domin lura da ɗalibai. Yayin da ake zagayawa, a riƙa tambayar ɗalibai yadda suka sami amsoshinsu. A tabbatar masu idan amsarsu daidai ne.

## Bayyanawa

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu don su nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai.

## Aikin Gida



A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 45 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 99 | Zango na 2, Mako na 8, Darasi na D |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su warware lissafi ta amfani da tarawa
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Rerawa (minti 3)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Waƙar Tarawa
Yi ƙari har zuwa har
sannan komai zai yi kyau.
10 ko sama da haka sai a
kai gida na gaba!
Za mu iya! Za mu iya!

**Koyo**

warwareaikin lissafi da tagwayen lambobi guda uku (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi lissafi ta hanyar tarawa da kuma ragowa.*
- Faɗa wa ɗalibai labarin da ke biye: Malam ya ce wa Musa da Lawan da Amina da su ƙirga adadin fensuran da suke cikin aji. Musa ya ƙirga 29, Lawan ya ƙirga 45 sannan Amina ta ƙirga 18. Duka-duka fensira nawa suka ƙirga?
- Umurci wani ɗalibi/ ɗaliba ya/ta zo gaban allo ya/ta rubuta fasalin lissafin da ya dace da labarin.
- A tabbatar an rubuta 29 + 45 +18 = a kan allo.
- A sa ɗalibi/ ɗaliba ɗaya ya/ta fito gaban aji ya gwada yadda za a tara lambobin yayin da aka Jera su a tsaye ta hanyar ragowa, sannan ɗaya kuma ya/ta gwada tara lambobin yayin da aka jera su a kwance.
- **Ka/ki ce:** *Yayin da aka tara ɗaiɗaya, wani lokaci jimillar takan zarce goma. A wannan misalin, 9 + 5 + 8 = 22. Akwai ɗaiɗaya guda 2 da kuma goma-goma 2, wannan yana nuna sai mun yi tafiya da 2!*

**Gwaji**

Aiki a ƙananan rukunoni: Gano amsar lissafi tare da ragowa (minti 15)

- A sa ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunoni.
- **Ka/ki ce:** *Ɗalibai uku suka sai alewa domin rabawa 'yan aji. ɗaya daga cikinsu ya sai guda 21, ɗaya kuma ya sai 19 sannan ɗayan kuma ya sai guda 26. Duka-duka alewa nawa za a samu?* (Amsa: 66)
- Yi ta maimaita lissafin da aka bayar don a tabbatar ɗalibai sun ji dukkan lambobin da ake magana a kai.
- A sa ɗalibai su rubuta fasalin lissafin a cikin littafansu na rubutu a ɗaiɗaikunsu.
- Da zarar ɗaliban sun rubuta fasalin lissafin, a su haɗa kai wajen gano amsoshin. Su gwada gano amsoshin lissafin ta hanyar jera lissafin a tsaye da kwance.
- A zagaya domin lura da ɗalibai sannan a ba su tallafi. Idan akwai lokaci, a maimaita da wani aikin lissafin.

**Bayyanawa**

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A nemi wani ɗalibi/ ɗaliba ya/ta fito domin gano amsar aikin lissafin a kan allo, sannan kuma tare da bayyana yadda aka gano amsar. A sa ɗalibai su ɗaga babbar yatsarsu sama idan sun yarda da amsar.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su gano amsar 43 + 12 + 38 cikin litattafansu na rubutu.

| Na. 100 | Zango na 2, Mako na 8, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi bita da gwajin aikin da aka gabatar a makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.(Amsa: 93)

Rerawa (minti 3)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

> Waƙar Tarawa
> Yi ƙari har zuwa har sannan komai zai yi kyau.
> 10 ko sama da haka sai a kai gida na gaba!
> Za mu iya! Za mu iya!

**Koyo**

Bita da maimaitawa (minti 10)

- Zaɓi wani labari daga ayyukan mako da ake ganin kamar ɗalibai suna fama da shi. A sake maimaita koyar da shi ko kuma a koyar da shi ta wata hanyar daban.

**Gwaji**

Aiki a ɗaiɗaiku ko cikin ƙananan rukunoni: Tarawa na tagwayen lambobi da ragowa (minti 15)

- A ba ɗalibai wani aiki wanda zai taimaka masu gwajin abin da ake bita a kansa (Misali, tara tagwayen lambobi guda 3 ko fiye waɗanda aka zuba su a kwance ko a tsaye). Ɗalibai za su iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma cikin rukunoni.
- Yayin da ɗalibai suke mayar da hankalinsu a kan aikinsu, a samar da taimako ga masu buƙata

**Bayyanawa**

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna ayyukan da suka kammala a lokacin gwaji.

**Aikin Gida**

A ba ɗalibai aikin gida don bita da gwajin abin da suka koya.

**Na. 101** 

# Zango na 2, Mako na 9, Darasi na A

**Manufa:** Ɗalibai za su yi lissafin ɗebewa ta hanyar amfani da abubuwan ƙirge.
**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge (wake da tsakuwoyi) **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

| | |
|---|---|
| Oyoyo oyoyo<br>Oyoyo Baba ya dawo<br>Ya dawo daga kasuwa<br>Ya sawo muna goriba<br>Ni an bani guda huɗu | Na ci ɗaya saura uku<br>In ya ci ɗaya saura biyu<br>In ta ci ɗaya saura ɗaya<br>In ka ci ɗaya ba ko ɗaya |

## Koyo

Gabatarwa a kan lissafin ɗebewa da tagwayen lambobi ta hanyar amfani da abubuwan ƙirge (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau, za mu yi ɗebewa da tagwayen lambobi ta hanyar amfani da abubuwan ƙirge.*
- Ɗora abubuwan ƙirge guda 25 a kan teburi a gaban aji. A sa wani ɗalibi ko wata ɗaliba ya/ta fito gaban aji domin ƙirga abubuwan ƙirgen. A sa ya/ta rubuta adadin a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu kuma ina so in ɗebe abubuwan ƙirge guda 21.*
- A sa wani/wata ɗalibi/aɗaliba daban ya/ta fito gaban aji a kwashe 21 daga cikin abubuwan ƙirgen da ke kan teburi.
- A tambayi ɗalibai saura nawa ne suka rage.
- **Ka/ki ce:** *Mun fara da abubuwan ƙirge guda 25, sannan muka ɗauke 21. Yanzu saura abubuwna ƙirge guda 4.*
- Rubuta fasalin lissafi 25 – 21 = 4 a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *25 a ɗebe 21 ya zama 4.*
- Idan akwai sauran lokaci a maimaita da wani fasalin lissafin.

## Gwaji

Aiki a ƙananan ƙungiyoyi: Lissafin ɗebewa ta hanyar amfani da abubuwan ƙirge (minti 15)

- A sa ɗalibai su zauna cikin ƙananan ƙungiyoyi. Zaɓi shugaba daga kowane rukuni don su taimaka wajen raba abubuwan ƙirge wa 'yan ƙungiyoyinsu. Rubuta wannan fasalin lissafin 38 – 12 = ___ a kan allo (Amsa:26)
- **Ka/ki ce:** *Dukkanku za ku yi aiki tare a matsayin rukuni domin gano amsar lissafin a kan allo. Da farko, akwai buƙatar ku samar da tarin abubuwan ƙirge da adadinsu ya kai lambar farko da take cikin fasalin lissafin.* (Amsa: 26)
- Yi ta maimaita lissafin da aka bayar don a tabbatar ɗalibai sun ji dukkan lambobin da ake magana a kai.
- A sa ɗalibai su rubuta fasalin lissafin a cikin littafansu na rubutu a ɗaiɗaikunsu.
- Da zarar ɗaliban su rubuta fasalin lissafin, a su haɗa kai wajen gano amsoshin. Su gwada gano amsoshin lissafin ta hanyar jera lissafin a tsaye da kwance.
- A zagaya lokacin da ɗalibai suke tara abubuwan ƙirgensu. A tabbatar da cewa a kowane tarin abubuwan ƙirge an samu 38.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu kuma sai ɗaya daga cikin ɗaliban kowane rukuni ya/ta ɗauke abubuwan ƙirge 12.*
- **Ka/ki ce:** *Kirga abin da ya rage sannan a rubuta fasalin lissafin a cikin litattafan rubutu.*

## Bayyanawa

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu don su nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su yi amfani da tsakuwoyi ko wake a gida domin gano amsar wannan fasalin lissafi 20 – 10. Su rubuta amsoshinsu a cikin littafin rubutunsu.

| Na. 102 | Zango na 2, Mako na 9, Darasi na B |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su yi lissafin ɗebewa ta hanyar amfani da layin lamba.
**Kayan Aiki:** Layin lambobi daga 0 zuwa 100 **Lokaci:** Minti 35


## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masugwiwa. (Amsa: 10)

Kidaya ta baya a kan layin lambobi (minti 5)

- Zana layin lambobi a kan allo daga 0 zuwa 100, tare da tsallaken 5.
- A sa ɗalibai su ƙirga daga baya su fara daga 10. Daga nan sai a ce su ƙidaya ta baya su fara daga 20.




## Koyo

Gabatarwa a kan lissafin ɗebewa na tagwayen lambobi ta hanyar amfani da layin lamba (minti 8)

- **Ka/ki ce:** *Yau, za mu ci gaba da ɗebewa a tagwayen lambobi ta hanyar amfani da layin lamba.*
- Rubuta wannan fasalin lissafi 80 – 20 = a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Muna lissafin ɗebewa ta hanayr amfani da layin lamba, za mu fara da zagaye lamba ta farko a cikin fasalin lissafin. Daga nan, sai mu fara ƙidaya ta baya a kan layin lambobin har sai mun ƙidaya yawan adadin da muke son ɗebewa.*
- A sa wani ɗalibi ko wata ɗaliba daban ya/ta fito gaban aji ya/ta zagaye lamba 80.
- A ƙidaya ta baya daga 80 tare da dukkan aji, ana motsa yatsa ko kuma alli a ƙarƙashin kowace lamba aka ambata.
- Yayin da yatsa ta zo kan lamba 60, a zagaye ta a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *A cikin 80 a ɗebe 20 saura 60.*
- Rubuta fasalin lissafi a kan allo.
- Idan akwai sauran lokaci a maimaita da wata aikin lissafin. A bar ɗalibai su zo gaban allo su rubuta fasalin lissafin.

## Gwaji

Aiki ɗaiɗaya ko cikin bibiyu: Ɗebewa ta hanyar amfani da layin lambobi (minti 15)

- A ce ɗaliban su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 46. A karanta wa ɗalibai umurni a bayyane. A ƙarasa gano aikin  lissafin na farko tare da su.
- A sa ɗalibai su gano amsar fasalin lissafi na gaba da ke cikin littafin ɗalibai. Za su iya aiki a ɗaiɗaiku ko da abokan aiki
- A zagaya domin lura da ɗalibai. Yayin da ake zagayawa, a riƙa tambayar ɗalibai yadda suka sami amsoshinsu. A tabbatar masu idan amsarsu daidai ne.

## Bayyanawa

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu don su nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 46 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 103 | Zango na 2, Mako na 9, Darasi na C |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su yi lissafin ɗebewa idan aka zuba lambobi a kwance ko a tsaye.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

| | |
|---|---|
| Oyoyo oyoyo<br>Oyoyo Baba ya dawo<br>Ya dawo daga kasuwa<br>Ya sawo muna goriba<br>Ni an bani guda huɗu | Na ci daya saura uku<br>In ya ci ɗaya saura biyu<br>In ta ci ɗaya saura ɗaya<br>In ka ci ɗaya ba ko daya |

**Koyo**

Ɗebe lambobi masu ƙwalli 2 ta hanyar fasalin lissafi da za a jera lambobi a kwance (minti 7)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu gwada ɗebe lambobi masu ƙwalli 2 idan an jera su a kwance ko a tsaye.*
- Rubuta wannan fasalin lissafi 34 – 13 = a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Yayin da za a yi lissafin ɗebewa a kwance, muna bi daga hagu zuwa dama kuma muna farawa da wuraren ɗaiɗaya. Ɗaiɗaya guda nawa ake da su?*
- A kewaye 4 da 3. A tambayi ɗalibai nawa ne 4 – 3. A rubuta lamba 1 a wurin ɗaiɗaya a kan layi.
- **Ka/ki ce:** *Daga nan kuma, sai mu ɗebe lambobi da suke gidan goma-goma. Nawa ne 3 – 1?*
- Kewaye 3 da 1. A tambayi ɗalibai nawa ne 3 – 1. Rubuta lamba 2 a gidan goma-goma a kan layin.
- **Ka/ki ce:** *34 a ɗebe 13 ya zama 21.*

34 – 13 = 21

Ɗebewa idan an zuba lambobi a tsaye (minti 8)

- **Ka/ki ce:** *Kamar yadda muka yi lissafin debewa a kwance, muna farawa da ɗebe lambobin da ke gidan ɗaiɗaya.*
- Rubuta wannan fasalin lissafin 45 – 23 = a kan allo, sannan a tambayi ɗalibai nawa ne 5 – 3. Rubuta 2 a ƙasan layi a gidan ɗaiɗaya.
- **Ka/ki ce:** *Daga nan kuma, sai mu ɗebe lambobi da suke gidan goma-goma daga sama zuwa ƙasa. Nawa ne 4 – 2?*
- Rubuta lamba 2 a ƙasan layi a gidan goma-goma.
- **Ka/ki ce:** *45 a ɗebe 23 ya zama 22.*

$$\begin{array}{r} 45 \\ -\ \underline{23} \\ 22 \end{array}$$

**Gwaji**

Aiki ɗaiɗaya ko cikin bibiyu: Ɗebewa a cikin lambobin da aka jera su a kwance da kuma a tsaye (minti 10)

- A ce ɗaliban su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 47. A karanta wa ɗalibai umurni a bayyane. A ƙarasa gano aikin lissafi na farko tare da su.
- A sa ɗalibai su gano amsar fasalin lissafi na gaba da ke cikin littafin ɗalibai. Za su iya aiki a ɗaiɗaiku ko da abokan aiki
- A zagaya domin lura da ɗalibai. Yayin da ake zagayawa, a riƙa tambayar ɗalibai yadda suka sami amsoshinsu. A tabbatar musu idan amsarsu daidai ne.

**Bayyanawa**

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu don su nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 47 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 104 | Zango na 2, Mako na 9, Darasi na D |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su gano amsar lissafi ta hanyar ɗebewa.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

| | |
|---|---|
| Oyoyo oyoyo<br>Oyoyo Baba ya dawo<br>Ya dawo daga kasuwa<br>Ya sawo muna goriba<br>Ni an bani guda huɗu | Na ci ɗaya saura uku<br>In ya ci ɗaya saura biyu<br>In ta ci ɗaya saura ɗaya<br>In ka ci ɗaya ba ko daya |

**Koyo**

Gano amsar lissafi ta hanyar ɗebewa (minti 10)

- Bayar da wannan labarin: Yakaka da Laraba suna yini suna wasa a filin gida. Suka ɗebi itatuwa da ganyayyakin bishiya da wuri da dai tarkacen ƙananan abubuwa tsubi-tsubi a filin gidan. Wani lokaci sukan gayyato abokansu don su yi wasa sannan su bayar da waɗannan wurin. A yau Yakaka da Laraba sun tara wuri 97 sannan kuma suka ba ma abokansu 35. Yanzu sauransu wuri nawa?
- A nemi ɗaliban su fito gaban aji domin kwatanta aiwatar da labarin. A sa ɗaliban su fitar da fasalin lissafin da ya dace da labarin, sannan a ce su rubuta a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *An tara wuri 97 gabaɗaya, amma kuma an bayar da 35 ga abokai. Idan muna so mu gano nawa ne ya rage, sai mu ɗebe 35 daga cikin 97.*
- A tabbatar fasalin lissafin da aka rubuta  ya zama kamar haka 97 – 35 = ___.
- A umurci wani ɗalibi ko wata ɗaliba ya/ta fito gaban allo domin nuna yadda za a tara lambobin idan aka zuba su a kwance.
- A sa wani ɗalibi ko wata ɗaliba kuma ya/ta fito gaban allo domin nuna yadda za a tara lambobin idan aka zuba su a kwance
- A yi amfani da jaddawalin ɗari-ɗari ko layin lambobi wajen ƙirge ta baya tare da dukkan ʻyan aji don a tabbatar da amsar: 97 - 35 = 62.

**Gwaji**

Aikin ƙananan rukunoni: Gano amsar lissafita hanyar ɗebewa (minti 15)

- A sa ɗalibai su zauna cikin ƙananan ƙungiyoyi sannan su buɗe littafin ɗalibai wurin da aka yi maganar jaddawalin lambobi ko layin lambobi.
- **Ka/ki ce:** *Ado yana da alawa 68 wadda ya sayo domin ya raba wa ʻyan ajinsu. Ya raba alewa 41 wa ʻyan ajin nasu a wannan ranar. Yanzu alewa nawa ne ta rage wa Ado?* (Amsa: 27)
- Yi ta maimaita lissafin da aka bayar don a tabbatar ɗalibai sun ji dukkan lambobin da ake magana a kai.
- A sa ɗalibai su rubuta fasalin lissafin a cikin littafansu na rubutu a daiɗaikunsu.
- Da zarar ɗaliban su rubuta fasalin lissafin,  su haɗa kai wajen gano amsoshin. Su gwada gano amsoshin lissafin ta hanyar jeralissafin a tsaye da a kwance.
- A zagaya domin lura da ɗalibai don a bayar da tallafi. Idan akwai lokaci, a maimaita da wata wani aikin lissafin.

**Bayyanawa**

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna amsoshinsu gaʻyan wani rukuni  sannan su tattauna  yadda suka sami amsar.

**Aikin Gida**



A sa ɗalibai  su gano amsar wannan lissafin 81 - 10 = a cikin litattafansu na rubutu.

## Na. 105 | Zango na 2, Mako na 9, Darasi na E

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi bita da gwajin aikin da aka gabatar a makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa. (Amsa: 71)

| | |
|---|---|
| Oyoyo oyoyo<br>Oyoyo Baba ya dawo<br>Ya dawo daga kasuwa<br>Ya sawo muna goriba<br>Ni an bani guda huɗu | Na ci daya saura uku<br>In ya ci ɗaya saura biyu<br>In ta ci ɗaya saura ɗaya<br>In ka ci ɗaya ba ko daya |

Waƙa (minti 2)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

### Koyo

Bita da maimaitawa (minti 10)

- Zaɓi wani labari daga ayyukan mako da ake ganin kamar ɗalibai suna fama da shi. A sake maimaita koyar da shi ko kuma a koyar da shi ta wata hanyar daban.

### Gwaji

Aiki a ɗaiɗaiku ko cikin ƙananan ƙungiyoyi: Tara lambobi masu ƙwalli 2 da ragowa (minti 15)

- A ba ɗalibai wani aiki wanda zai taimaka musu gwajin abin da ake bita a kansa (Misali, ɗebewa ta hanyar amfani da layin lambobi). Ɗalibai za su iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma cikin ƙungiyoyi.
- Yayin da ɗalibai suke mayar da hankalinsu a kan aikinsu, a samar da taimako ga masu bukata.

### Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna ayyukan da suka kammala a lokacin gwaji.

### Aikin Gida

A ba ɗalibai aikin gida don bita da gwajin abin da suka koya.

| Na. 106 | Zango na 2, Mako na 10, Darasi na A |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai su iya lissafin ɗebewa da damin sanda da kuma iya ragowa.
**Kayan Aiki:** Damin sanduna **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Rera waƙa (minti 3)

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

> Rera waƙar ɗebewa
> Manyan lambobin a sama, ɗebe a ciki!
> Manyan lambobin a ƙasa, tsaya mu yi aro.
> Lambobin da suke iri ɗaya?
> Amsar ta zamo sifil!

**Koyo**

Gabatar da ɗebewa ta tagwayen-lamba ta amfani da sanduna da gidan goma (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau, za mu gwada ɗebe tagwayen-lambobi da kuma ragowa. Za mu yi amfani da damin goma ya taimaka mana.*
- Kira wani ɗalibi zuwa gaban aji a ba shi damin goma na sanduna. A ce masa ya ƙirga su ɗauri ɗauri a samu jimillar sandunan.
- **Ka/ki ce:** *Muna da sanduna 40, ko kuma damin goma guda 4. Ina son bayar da sanda 28 daga cikinsu. Yaya zan rubuta fasalin lissafin?*
- A kira wani ɗalibin ya je kan allo ya rubuta fasalin lissafin 40 – 28 =__.
- Nuna wa ɗalibai yadda za a cire sanda 20 (ɗaurin dami 2) daga 40 (ɗaurin dami 4). Za a sami sauran sanda 20 (ɗaurin dami 2). Sannan sai a nuna masu yadda za a ƙunce sauran damin goma 2 su koma sanduna 20 sai a cire sanda 8. Za a sami sanda 12 da za su yi saura. Amsar ta zama 12 kenan.
- A kuma kira wani ɗalibi ya ƙirga sauran sandunan.
- Rubuta fasalin lissafin 40 – 28 = 12 a kan allo.

**Gwaji**

Aiki cikin ƙaramin rukuni : ɗebewa da ragowa ta amfani da damin goma (minti 15)

- Ɗalibai su zazzauna a ƙananan ƙungiyoyi. Zaɓi shugaba a kowane rukuni ya taimaka wajen ba rukuninsu saunduna ɗaurin damin goma guda 3.
- Rubuta fasalin lissafin 21 – 12 = ___ a kan allo sai ɗalibai su kwafa.
- Ɗalibai su san cewa za su yi aiki tare ta amfani da ɗaurin dami wajen samun amsa.
- **Ka/ki ce:** *Da farko, mutum zai yi tunanin adadin sandunan da ake buƙata. Sannan, sai a ɗebe 12 daga ciki.*
- A kewaya a ga abin da ɗaliban ke yi da kuma taimaka masu .

**Bayyanawa**

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A ce ƙungiyoyin su nuna wa juna amsarsu sannan su tattauna kan yadda suka samo amsa.

**Aikin Gida**

A ce ɗalibai su ba da amsar 42 – 33 cikin littafin rubutunsu.

| Na. 107 | Zango na 2, Mako na 10, Darasi na B |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya lissafin ɗebewa ta amfani da faɗaɗa fasalin lamba.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa. (Amsa: 9)

Rera waƙa (minti 3)

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Rera waƙar ɗebewa
Manyan lambobin a sama, ɗebe a ciki!
Manyan lambobin a ƙasa, tsaya mu yi aro.
Lambobin da suke iri ɗaya?
Amsar ta zamo sifil!

### Koyo

Gabatar da lissafin ɗebewa ta amfani da faɗaɗa fasalin lamba (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi ɗebe lambobi ta hanyar faɗaɗa fasalin lamba da kuma ragowa.*
- Rubuta fasalin lissafin 82-14 a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Idan za mu yi lissafin ɗebewa na 82 – 14, za mu fara da kowace lamba ta hanyar faɗaɗa fasalinta.*
- Nuna wa ɗalibai yadda za a faɗaɗa 82 zuwa gidan goma 8 da gidan ɗaya 2. Sannan, a kira wani ɗalibin ya je kan allo ya rubata faɗaɗa fasalin 14.
- **Ka/ki ce:** *Idan muna son mu yi lissafin ɗebe lambobi fasalinsu a faɗaɗe, da farko za mu buƙaci mu ɗebe a cikin lambobi biyu da ke gidan ɗaya. Mene ne amsar 2 - 4? Kash ba zai yiwu ba!*
- Yi amfani da yatsu a nuna wa ɗalibai cewa ba za su iya ɗebe 4 daga cikin 2 ba.
- **Ka/ki ce:** *Tun da lambar da ke gidan ɗaya na ƙasa ta ɗara wadda take a gida na sama, dole mu yi wani abu da ake kira aro. Kamar dai yadda muke faɗaɗa gidan goma mu sami ɗaiɗai, haka za mu yi aron goma ɗaya daga gidan goma.*
- Bayyana wa ɗalibai cewa yadda za a sami goma, shi ne za su cire goma daga gidan goma sai su ƙara wa gidan ɗaya.
- **Ka/ki ce:** *80 – 10 shi ne 70, kuma 2 +10 shi ne 12. Yanzu za a sami ɗaiɗai a gidan ɗaya na sama da za su ɗara na gidan ƙasa, sai a ci gaba da lissafi! Nawa ne 12-4?*
- Rubuta 8 a layin ƙasa ƙarƙashin gidan ɗaya.
- **Ka/ki ce:** *Nawa ne 70 – 10?*
- Rubuta 60 a layin ƙasa ƙarƙashin gidan goma, sai a yi lissafin fasalin: 60 + 8 = 68

82 – 14

80 + 2
- 10 + 4

70 12
~~80~~ + ~~2~~
- 10 + 4
60 + 8 = 68

### Gwaji

Aiki ɗaiɗai ko bibbiyu: Ɗebewa ta amfani da faɗaɗa lamba (minti 15)

- A sa su buɗe Shafi na 48 da ke littafinsu. Karanta wa ɗalibai umarnin su ji. Ku amsa tambayar farko tare.
- Sa ɗalibai su amsa tambaya ta gaba. Za su iya aiki ɗaiɗai ko kuma su bibbiyu.
- A kewaya a ga abin da ɗaliban ke yi da kuma taimaka masu.

### Bayyanawa

Gaggauta auna fahimci (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardarsu sama su nuna abin da suka rubuta. A yaba musu.

### Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 48 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 108 | Zango na 2, Mako na 10, Darasi na C |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya lissafin ɗebewa ta tsaye.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

<u>Duba aikin gida (minti 2)</u>

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

<u>Rera waƙa (minti 3)</u>

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

> <u>Rera waƙar ɗebewa</u>
> Manyan lambobin a sama, ɗebe a ciki!
> Manyan lambobin a ƙasa, tsaya mu yi aro.
> Lambobin da suke iri ɗaya?
> Amsar ta zamo sifil!

### Koyo

<u>Gabatar da lissafin ɗebewa ta tsaye (minti 10)</u>

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi yadda ake ɗebe lambobi da ragowa.*
- Rubuta fasalin lissafin 55 – 26 = ___ a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Idan za mu ɗebe lambobi, za mu fara da ɗebewar da lamba biyu da ke gidan ɗaya. Za mu bi hanyar tsaye wajen ɗebewar. Nawa ne 5 - 6? Kash, ba zai yiwu ba! Lambar da ke ƙasa ta ɗara ta sama, dole mu je gidan goma mu yi aro!*
- Nuna wa ɗalibai yadda za a share 5 ɗin da ke gidan goma a rubuta 4. Muna da goma 5 a gidan goma, yanzu saura 4. Gaba, sai mu tara goma ɗaya da 5. 10 + 5 = 15.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu gidan ɗaya na sama ya ɗara na ƙasa, sai mu ci gaba da lissafi! Nawa ne 15 - 6?*
- Rubuta 9 a layin ƙasa ƙarƙashin gidan ɗaya.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu, sai mu ɗebe na gidan goma. Mun rage goma ɗaya a sama saɓanin kafin mu fara lissafi, don haka nawa ne 4-2?*
- Rubuta 3 a layin ƙasa ƙarƙashin gidan, sai mu yi lissafin fasalin: 55 – 26 = 29.

55 – 26

  55
- 26

4 15
~~55~~
- 26
  29

### Gwaji

<u>Aiki ɗaiɗai ko bibbiyu: Ɗebewa ta tsaye da ragowa (minti 15)</u>

- A sa su buɗe Shafi na 49 da ke littafinsu. Karanta wa ɗalibai umarnin su ji. Ku amsa tambayar farko tare.
- Sa ɗalibai su amsa tambaya ta gaba. Za su iya aiki ɗaiɗai ko kuma su bibbiyu.
- A kewaya a ga abin da ɗaliban ke yi da kuma taimaka masu.

### Bayyanawa

<u>Gaggauta auna fahimci (minti 5)</u>

- A sa ɗalibai su ɗaga takardarsu sama su nuna abin da suka rubuta. A yaba masu.

### Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 49 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 109 | Zango na 2, Mako na 10, Darasi na D |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai su iya warware aikin lissafin ɗebewa na cikin labari.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Rera waƙa (minti 3)

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

> Rera waƙar ɗebewa
> Manyan lambobin a sama, ɗebe a ciki!
> Manyan lambobin a ƙasa, tsaya mu yi aro.
> Lambobin da suke iri ɗaya?
> Amsar ta zamo sifil!

## Koyo

Warware aikin lissafin ɗebewa da ragowa (minti 10)

- Ba ɗalibai wannan labari: Malami yana da ƙarin fensira 51. Ɗalibai 28 suka buƙaci aron fensir a wannan rana. Fensura nawa za su rage a gun malamin?
- Kira ɗalibi 1 ku gwada aiwatar da labarin tare. Sa ɗalibin ya rubuta fasalin lissafin da ake buƙata wajen warware aikin lissafin a kan allo.
- ***Ka/ki ce:*** *Malamin yana da fensur 51 sai ya bai wa ɗalibai 28 su yi amfani da su. Idan muna son sanin nawa suka yi masa saura, sai mu cire 28 daga 51.*
- Tabbata fasalin nan 51 – 28 = ___ yana rubuce a kan allo.
- A kira wani ɗalibin ya je kan allo ya samar da amsar fasalin.
- Taimaka yayin yin aro.

$$\begin{array}{r} 51 \\ -\ 28 \\ \hline \end{array}$$

$$\begin{array}{r} {}^{4}\,{}^{11} \\ \not{5}\not{1} \\ -\ 28 \\ \hline 23 \end{array}$$

## Gwaji

Aiki cikin ƙaramin rukuni : Warware aikin lissafi ta ɗebewa (minti 15)

- Ɗalibai su zazzauna a ƙananan rukunoni.
- **Ka/ki ce:** *Ɗan Jummai yana da alewa guda 68 da ya kawo ya raba shi da 'yan aji. Ya raba wa 'yan ajinsa alewa 39 a wannan rana. Alewa nawa suka rage ma Ɗan Jummai?* (Amsa: 29)
- Yi ta maimaita lissafin da ke cikin labarin ta yadda za su fahimci abin da ake faɗa.
- Sa kowane ɗalibi ya rubuta fasalin lissafin labarin a cikin littafinsa na rubutu.
- Da zarar kowane ɗalibi ya rubuta fasalin, sai a sa su yin aikin tare wajen samar da amsa. Su gwada warware aikin lissafin ta hanyar lissafi a tsaye da kwance.
- A kewaya a ga abin da ɗaliban ke yi da kuma taimaka masu. Idan da lokaci, a sake bada wani aikin warware lissafi.

## Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- Sa ɗaliban su bayyana wa juna abin da suka yi a rukuninsu.

## Aikin Gida

A ce wa ɗalibai su ba da amsar 43 – 18 = ___ cikin littafin rubutunsu aikin gida.

## Na. 110 — Zango na 2, Mako na 10, Darasi na E

**Manufofi:** Ɗalibai su iya bita da gwajin aikin da aka gabatar a makon.

**Kayan Aiki:**

**Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa. (Amsa: 25)

Rera waƙa (minti 3)

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Rera waƙar ɗebewa
Manyan lambobin a sama, ɗebe a ciki!
Manyan lambobin a ƙasa, tsaya mu yi aro.
Lambobin da suke iri ɗaya?
Amsar ta zamo sifil!

### Koyo

Bita da maimaitawa (minti 10)

- Zaɓi wani labari daga ayyukan mako da ake ganin kamar ɗalibai suna fama da shi. A sake maimaita koyar da shi ko kuma a koyar da shi ta wata hanyar daban.

### Gwaji

Aiki ɗaiɗai ko a cikin rukuni : Ɗebewa da tagwayen-lamba da kuma ragowa (minti 15)

- Ba ɗalibai jingar za ta taimaka masu su gwada abin da aka yi masu bita a kai (misali, lissafin ɗebewa ta tsaye ko ta kwance).
- Ɗalibai za su iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma cikin ƙananan ƙungiyoyi.
- A yayin da ɗalibai suka mayar da hankali kan yin aikin jingar, a taimaka wa ɗaliban da suke buƙatar matuƙar taimako.

### Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala yayin gwaji.

### Aikin Gida

A ba ɗalibai aikin gida da za su yi bita da kuma nuna ƙwarewarsu.

| Na. 111 | Zango na 2, Mako na 11, Darasi na A |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai su iya lissafin ɗebewa ta amfani da abubuwan ƙirge da kuma sauya-suna.
**Kayan Aiki:** Damin sanduna **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Rera waƙa (minti 3)

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Rera waƙar ɗebewa
Manyan lambobin a sama, ɗebe a ciki!
Manyan lambobin a ƙasa, tsaya mu yi aro.
Lambobin da suke iri ɗaya?
Amsar ta zamo sifil!

**Koyo**

Gabatar da ɗebe tagwayen-lambobi ta amfani da sanduna da damin goma (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau, za mu gwada ɗebe tagwayen-lambobi da ragowa. Za mu yi amfani da damin goma ya taimaka mana.*
- Kira wani ɗalibi zuwa gaban aji a ba shi damin goma 5 na sanduna. A ce masa ya ƙwance ɗaurin ya ƙirga su a sami jimillar sandunan.
- **Ka/ki ce:** *Muna da sanduna 50, ko damin goma 5. Ina son bayar da sanda 39 daga ciki. Yaya zan rubuta fasalin lissafin?*
- A kira wani ɗalibin ya je kan allo ya rubuta fasalin lissafin 50 – 39 =__.
- Nuna wa ɗalibai yadda za a cire 30 (ɗaurin dami 3) daga 50 (5 ɗaurin dami). Za a sami sanda 20 da za su yi saura (ɗaurin dami 2). Sannan a nuna yadda za a faɗaɗa sauran ɗaurin dami 2 su kama ɗaiɗai, sai a cire 9 daga cikinsu. Za a sami sanda 11 saura. Amsar ita ce11.
- A kuma kira wani ɗalibi ya ƙirga sauran sandunan.
- Rubuta fasalin lissafin 50 – 39 = 11 a kan allo.

**Gwaji**

Aiki cikin ƙaramar rukuni : ɗebewa da ragowa ta amfani da damin goma (minti 15)

- Ɗalibai su zazzauna a ƙananan ƙungiyoyi. Zaɓi shugaba a kowane rukuni ya taimaka wajen raba wa rukuninsa ɗaurin dami 2 na sanduna.
- Rubuta fasalin lissafin 20 – 18 = ___ a kan allo sai ɗalibai su kwafa.
- Ɗalibai su san cewa za su yi aiki tare ta amafani da ɗaurin dami wajen bada amsa.
- **Ka/ki ce:** *Da farko, mutum zai yi tunanin adadin sandunan da ake bukata. Sannan, sai a ɗebe 18 daga cikin su.*
- A kewaya a ga abin da ɗaliban ke yi da kuma taimaka masu.

**Bayyanawa**

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A ce wa ƙungiyoyin su nuna wa juna amsarsu sannan su tattauna kan yadda suka samo amsar.

**Aikin Gida**

A ce wa ɗalibai su ba da amsar 51 – 35 cikin littafin rubutunsu.

Na. 112

# Zango na 2, Mako na 11, Darasi na B

**Manufa:** Ɗalibai za su iya lissafin ɗebewa ta amfani da Faɗaɗa fasalin lamba.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

<u>Duba aikin gida (minti 2)</u>

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa. (Amsa: 16)

<u>Rera waƙa (minti 3)</u>

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

<u>Rera waƙar ɗebewa</u>
Manyan lambobin da ke sama, ɗebe a ciki!
Manyan lambobin da ke ƙasa, tsaya mu yi aro.
Lambobin da suke iri ɗaya?
Amsar ta zamo sifil!

## Koyo

<u>Gabatar da lissafin ɗebewa ta amfani da faɗaɗa fasalin lamba (minti 10)</u>

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi yadda ake ɗebe lambobi ta hanyar faɗaɗa lambobi da ragowa.*
- Rubuta fasalin lissafin 65-29 = ___ a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Idan za a yi lissafin nan 65– 29, da farko, za mu rubuta lambobin a faɗaɗe.*
- Nuna wa ɗalibai yadda za a faɗaɗa 65 zuwagidan goma 6 da gidan ɗaya 5. Sannan, a kira wani ɗalibin ya je kan allo ya rubuta 29 cikin fasalinsa a faɗaɗe.
- **Ka/ki ce:** *Idan za mu ɗebe lambobi cikin fasalinsu a faɗaɗe, za mu fara da ɗebewar da lamba biyu da ke gidan ɗaya. Nawa ne 5- 9? Kash, ba zai yiwu ba!*
- Nuna wa ɗalibai cewa ba za iya ɗebe 9 cikin 5 ba da yatsu.
- **Ka/ki ce:** *Lambar da ke ƙasa ta ɗara ta sama, dole mu je gidan goma mu yi aro! Kamar yadda muke faɗaɗa gidan goma mu samar da ɗaiɗai a gidan ɗaya, haka za mu yi aro goma ɗaya daga gidan goma.*
- Bayyana wa ɗalibai cewa yadda za a sami goma, shi ne za su cire goma daga gidan goma sai su ƙara wa gidan ɗaya.
- **Ka/ki ce:** *60 – 10 shi ne 50, kuma 5+10 shi 15. Yanzu gidan ɗaya na sama ya ɗara na ƙasa, sai mu ci gaba da lissafi! Nawa ne 15-9?*
- Rubuta 6 a layin ƙasa a ƙarkashin gidan ɗaya.
- **Ka/ki ce:** *Nawa ne 50 – 20?*
- Rubuta 30 a layin ƙasa, sai mu yi lissafin fasalin: 30 + 6 = 36

65 – 29 = ___

60 + 5
- 20 + 9

50 15
~~60~~ + ~~5~~
- 20 + 9
30 + 6 = 36

## Gwaji

<u>Aiki ɗaiɗai ko bibbiyu: Ɗebewa ta amfani da faɗaɗa lamba (minti 15)</u>

- A sa su buɗe Shafi na 50 da ke littafinsu. Karanta wa ɗalibai umurnin su ji. Ku amsa tambayar farko tare.
- Sai ɗalibai su amsa tambaya ta gaba. za su iya aiki ɗaiɗai ko kuma su bibbiyu.
- A kewaya a ga abin da ɗaliban ke yi da kuma taimaka masu.

## Bayyanawa

<u>Gaggauta auna fahimci (minti 5)</u>

- A sa ɗalibai su ɗaga takardarsu sama su nuna abin da suka rubuta. A yaba masu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 50 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 113 | Zango na 2, Mako na 11, Darasi na C |
|---|---|

**Manufoa:** Ɗalibai su iya ɗebewa ta tsaye.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Rera waƙa (minti 3)

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Rera waƙar ɗebewa
Manyan lambobin a sama, ɗebe a ciki!
Manyan lambobin a ƙasa, tsaya mu yi aro.
Lambobin da suke iri ɗaya?
Amsar ta zamo sifil!

### Koyo

Gabatar da lissafin ɗebewa ta tsaye (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi yadda ake ɗebe lambobi da ragowa.*
- Rubuta fasalin lissafin 36 – 17 = ___ a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Idan za mu ɗebe lambobi, za mu fara da ɗebewar da lamba biyu da ke gidan ɗaya. Za mu bi hanyar tsaye wajen ɗebewar. Nawa ne 6 - 7? Kash, ba zai yiwu ba! Lambar ƙasa ta ɗara ta sama, dole mu je gidan goma mu yi aro!*
- Nuna wa ɗalibai yadda za ku shafe 3 da ke gidan goma, a rubuta 2. Akwai goma 3 a baya, amma yanzu sun zama goma 2. Gaba, sai a tara gidan goma 1 da gidan ɗaya 6. 10 + 6 = 16.

36 - 17 = ___

 36
\- 17

2 16
~~36~~
\- 17
 19

- **Ka/ki ce:** *Yanzu gidan ɗaya na sama ya ɗara na ƙasa, sai mu ci gaba da lissafi! Nawa ne 16 - 7?*
- Rubuta 9 a layin ƙasa ƙarƙashin gidan ɗaya.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu, sai mu ɗebe lambobin gidan goma. Mun rage goma ɗaya a sama kafin mu fara lissafi,don haka nawa ne 2-1?*
- Rubuta 1 a layin ƙasa, sai mu yi lissafin fasalin: 36 – 17 = 19.

### Gwaji

Aiki ɗaiɗai ko bibbiyu: Ɗebewa ta tsaye da ragowa (minti 15)

- A sa su buɗe Shafi na 51 da ke littafinsu. Karanta wa ɗalibai umarnin su ji. Ku amsa tambayar farko tare.
- Sa ɗalibai su amsa tambaya ta gaba. za su iya aiki ɗaiɗai ko kuma su bibbiyu.
- A kewaya a ga abin da ɗaliban ke yi da kuma taimaka musu.

### Bayyanawa

Gaggauta auna fahimci (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardarsu sama su nuna abin da suka rubuta. A yaba musu.

### Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 51 a cikin littafansu na aiki a matsayin aikin gida.

| Na. 114 | Zango na 2, Mako na 11, Darasi na D |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai su iya warware aikin lissafin ɗebewa na cikin labari.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)
- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Rera waƙa (minti 3)
- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Rera waƙar ɗebewa
Manyan lambobin a sama, ɗebe a ciki!
Manyan lambobin a ƙasa, tsaya mu yi aro.
Lambobin da suke iri ɗaya?
Amsar su ta zamo sifili!

**Koyo**

Warware aikin lissafin ɗebewa da ragowa (minti 10)
- Karanta wannan labari: Akwai awaki 66 a wurin kiyo. Sai manomi ya kai 7 ya sayar. Awaki nawa suka yi saura a wurin kiwon?
- Kira wani ɗalibi ya je gaban aji ya gwada aiwatar da labarin. Sa ɗalibin ya rubuta fasalin lissafin da ake buƙata wajen warware aikin lissafin a kan allo.
- ***Ka/ki ce:*** *Akwai shanu 66 sai aka ɗauke 7 aka sayar. Idan muna son sanin adadin shanun da suka yi saura, sa a ɗebe 7 cikin 66.*
- Tabbata fasalin 66 – 7 = ___ na rubuce a kan allo.
- A kira wani ɗalibin ya je kan allo ya samar da amsar fasalin.
- Bayyana wa ɗalibai cewa idan babu wata lamba a gidan goma ko gidan ɗaya sai a ƙaddara cewa akwai 0 a gurbin. Misali, babu wata lamba a gidan goma da ke kusa da 7, don haka sai mu ƙaddara rubuta "07".
- Taimaka wa dalibai yayin yin aro.

66
\- 7

5 16
66
\- 7
59

**Gwaji**

Aiki cikin ƙaramar rukuni : Warware aikin lissafi ta amfani da ɗebewa (minti 15)
- Ɗalibai su zazzauna a ƙananan ƙungiyoyi.
- **Ka/ki ce:** *Awal yana da alawa 43 da ya kawo don nuna wa 'yan aji. Ya raba wa abokansa alawa 24 a wannan rana. Alawa nawa suka yi wa Auwal saura?* (Amsa: 19)
- Yi ta maimaita lissafin aikin lissafin da ke cikin labarin ta yadda za su fahimci abin da ake faɗa.
- Sa kowane ɗalibi ya rubuta fasalin lissafin labarin a cikin littafinsa na aiki.
- Da zarar kowane ɗalibi ya rubuta fasalin, sai a su yin aikin tare wajen samo amsa. Su gwada warware aikin lissafin ta hanyar lissafi tsaye da kwance.
- A kewaya a ga abin da ɗaliban ke yi da kuma taimaka musu. Idan da lokaci, a sake bada wani aikin warware aikin lissafi.

**Bayyanawa**

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)
- Sa ɗaliban su bayyana wa juna abin da suka yi a rukuninsu.

**Aikin Gida**

A ce wa ɗalibai su ba da amsar 81 - 22 = ___ cikin littafin rubutunsu. .

| Na. 115 | Zango na 2, Mako na 11, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya bita da gwajin aikin da aka gabatar a makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasai**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masugwiwa. (Amsa: 59)

Rera waƙa (minti 3)

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

> Rera waƙar ɗebewa
> Manyan lambobin a sama, ɗebe a ciki!
> Manyan lambobin a ƙasa, tsaya mu yi aro.
> Lambobin da suke iri ɗaya?
> Amsar su ta zamo sifili!

**Koyo**

Bita da maimaitawa (minti 10)

- Zaɓi wani batu daga ayyukan mako da ake ganin kamar ɗalibai suna fama da shi. A sake maimaita koyar da shi ko kuma a koyar da shi ta wata hanyar daban.

**Gwaji**

Aiki ɗaiɗai ko a cikin rukuni : Ɗebewar tagwayen-lamba da kuma sauya-suna (minti 15)

- Baɗalibai jingar da za ta taimaka musu su gwada abin da aka yi musu bita a kai (misali, lissafin ɗebewa ta tsaye ko ta kwance).
- Ɗalibai za su iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma cikin ƙananan ƙungiyoyi.
- A yayin da ɗalibai suka mayar da hankali kan yin aikin jingar, a taimaka wa ɗaliban da suke buƙatar matuƙar taimako.

**Bayyanawa**

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala yayin gwaji.

**Aikin Gida**

A bai wa ɗalibai aikin gida da za su yi bita da kuma nuna ƙwarewarsu.

| No. 116 | Zango 2, Mako 12, Darasi A |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su yi taƙaitacciyar Jarrabawa.
**Kayan Aiki:**

## JARRABAWAR GWAJI

Ka/ki gudanar da jarrabawa ga ɗalibai ɗaya bayan ɗaya, sai a rubutu sakamakon da suka samu a cikin littafin ɗaukar sakamako. Idan akwai buƙata kana iya neman taimakon shugaban makaranta ko membobin kwamitin gudanarwa na makarantu (SBMC) ko wasu daga cikin malami domin su taimaka wajen gudanar da jarrabawa.

A aikin wannan jarrabawa, rubuta aikin lissafin akan allo. Umurci ɗalibai su juyi aikin a cikin takardu, su bayar da amsoshinsu a ciki. Zaga domin lura da ɗalibai a tabbatar su na aiki a ɗaiɗaikunsu. Idan lokaci ya yi a karɓi takardun a samar da sakamako.

| **Jaha:** | | **Karamar hukuma:** | | **Makaranta:** | | **Wata:** | | **Shekara:** | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|

| Lamba | Sunan Ɗalibi | Jinsi | Shekaru | Buƙata ta musamman (Eh/A’a) | Tarawa /6 | Ɗebewa /9 | Jimillar maki / 15 |
|---|---|---|---|---|---|---|---|
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |
| | | | | | | | |

**Darasin Lissafi Aji 2, Zango na 2, Mako na 12 – Jarrabawar ƙarshen Zango**

**Tara waɗannan lambobin**. (A bayar da maki uku ga kowace amsa)

| | |
|---|---|
| 28 | 11 |
| + 64 | + 49 |

**Ɗebe waɗannan lambobin.** (A bayar da maki uku ga kowace amsa)

| | | |
|---|---|---|
| 54 | 61 | 75 |
| - 11 | - 22 | - 36 |

| Na. 117 | Zango na 2, Mako na 12, Darasi na B |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya tara 3 ko fiye na tagwayen-lambobi ta kwance ko tsaye da ragowa.

**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.


Rera waƙa (minti 3)

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

> Rera waƙar tarawa
> Tarawa har zuwa tara ba damuwa.
> 10 ko fiye, ɗau sauran zuwa gidan gaba!

## Koyo

Bita: Tara 3 ko fiye na tagwayen-lambobi ta kwance ko tsaye da ragowa (minti 10)




- **Ka/ki ce:** Yau, *za mu tara tagwayen-lambobi 3 wuri ɗaya.*
- Rubuta fasalin lissafin 18 + 27 + 36 = ___ a kan allo.
- Sa ɗalibai uku su je kan allo su cike gurbin kimar lamba da ke jiin jadawali da lambobin da suka dace na gidan goma da gidan ɗaya na waɗannan: 18, 27, and 36.
- **Ka/ki ce:** *Tun da yanzu an shigar da lambobin 3 duka cikin zanen,za mu iya tara su baki ɗaya. Za mu fara da lambar da ke gidan ɗaya.*
- A sa ɗalibai su ƙirga yawan da'irorin da ke gidan ɗaya.
- **Ka/ki ce:** *Akwai da'ira 21 a gidan ɗaya. Me za mu yi?*
- A kira wani ɗalibin ya je kan allo ya gwada yadda za a sauya ɗaiɗai 20 su koma goma 2.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu 1 ya rage a gidan ɗaya, kuma an sami sabbin goma 2. 18 + 27 + 36 = 81.*
- gaba, rubuta fasalin lissafin na kwance da kuma na tsaye daidai. Fara da gidan ɗaya sai a tambayi ɗalibai abin da 8+7+6 ke nufi.
- A kira wani ɗalibin ya je kan allo ya gwada yadda za a tara lambobin gidan ɗaya, ta sanya 1 a ƙarƙashin gidan ɗaya, da ɗaukar 2 zuwa gidan goma.
- A sa wani ɗalibi ya je kan allo ya tara lambobin da ke gidan goma.

## Gwaji

Aiki ɗaiɗai ko bibbiyu: Tara lamba 3 ko fiye na tagwayen-lambobi ta tsaye ko kwance (minti 15)

- Rubuta wannan fasalin lissafin a kan allo:
  34 + 23 + 13 = ___ ; 24 + 62 + 12 = ___ ; 19 + 12 + 15 = ___
- Umurci ɗalibai da su warware fasalin lissafin a cikin littafasnsu na rubutu. Za su iya aikin a ɗaiɗaiku ko kuma a bibbiyu.
- A zagaya a kula da abin da ɗalibai suke yi. A yayin zagayawar, a tambaye su yadda suka sami amsa, a kuma tabbatar musa da amsar da take daidai.

## Bayyanawa

Gaggauta auna fahimci (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardarsu sama su nuna abin da suka rubuta. A yaba masu.

## Aikin Gida

Umurci ɗalibai da su warware sauran fasalin lissafin da ke gwaji a cikin littafasnsu na rubutu. Za su iya aikin a ɗaiɗaiku ko kuma a bibbiyu.

| Na. 118 | Zango na 2, Mako na 12, Darasi na C |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya ɗebewa ta tsaye ko kuma kwance.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

<u>Waƙa (minti 2)</u>

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

| | |
|---|---|
| Oyoyo oyoyo<br>Oyoyo Baba ya dawo<br>Ya dawo daga kasuwa<br>Ya sawo muna goriba<br>Ni an bani guda huɗu | Na ci daya saura uku<br>In ya ci ɗaya saura biyu<br>In ta ci ɗaya saura ɗaya<br>In ka ci ɗaya ba ko daya |

<u>Duba aikin gida (minti 3)</u>

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafamasu gwiwa.

## Koyo

<u>Ɗebe tagwayen-lambobi ta fasalin lissafi kwance (minti 7)</u>

| |
|---|
| 85 – 43 = <u>42</u> |

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu gwada ɗebe tagwayen-lambobi ta kwance da kuma tsaye.*
- Rubuta fasalin lissafin 85 – 43 = a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Idan za mu yi lissafin ɗebewa ta kwance, za mu yi ne daga hagu zuwa dama, kuma za mu fara daga gidan ɗaya.Gidan ɗaya nawa ne a nan?*
- Kewaye 5 da 3. Tambayi ɗalibai me 5-3 ke nufi. Rubuta 2 a gidan ɗaya bayan alamar daidaito.
- **Ka/ki ce:** *Gaba, sai mu ɗebe lambobin da ke gidan goma. Nawa ne 8 – 4?*
- Kewaye 8 da 4. Tambayi ɗalibai me 8-4 ke nufi. Rubuta 4 a gidan goma bayan alamar daidaito.
- **Ka/ki ce:** *85 a ɗebe 43 daidai da 42.*

| |
|---|
| 85<br>- <u>43</u><br>42 |

<u>Ɗebewa ta tsaye (minti 8)</u>

- **Ka/ki ce:** Da farko za mu ɗebe lambobin da ke gidan ɗaya
- Rubuta fasalin lissafin 85 – 43 = a kan allo sai a tambayi nawa ne 5 – 3. Rubuta 2 a layin ƙasa ƙarƙashin gidan ɗaya.
- **Ka/ki ce:** *Gaba, sai mu ɗebe lambar gidan goman da ke ƙasa daga gidan goma na sama. Nawa ne 8 – 4?*
- Rubuta 4 a layin ƙasa ƙarƙashin gidan goma.
- **Ka/ki ce:** *85 a ɗebe 43 daidai da 42.*

## Gwaji

<u>Aiki ɗaiɗai ko a bibbiyu: Ɗebewa ta tsaye da kuma ta kwance (minti 10)</u>

- Rubuta wannan fasalin lissafin a kan allo:
  34 – 23 = ____ ; 19 – 16 = ___ ; 26 – 15 = ___
- Umurci ɗalibai da su warware sauran fasalin lissafin da ke gwaji a cikin littafasnsu na rubutu. Za su iya aikin a ɗaiɗaiku ko kuma a bibbiyu.

## Bayyanawa

<u>Gaggauta auna fahimci (minti 5)</u>

- A sa ɗalibai su ɗaga takardarsu sama su nuna abin da suka rubuta. A yaba musu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran ayyukan gwaji a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 119 | Zango na 2, Mako na 12, Darasi na D |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya ɗebewa ta tsaye da ragowa.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

<u>Duba aikin gida (minti 2)</u>

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwarsu.

<u>Rera waƙa (minti 3)</u>

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

<u>Rera waƙar ɗebewa</u>
Manyan lambobin da ke sama, ɗebe a ciki!
Manyan lambobin da ke ƙasa, tsaya mu yi aro.
Lambobin da suke iri ɗaya?
Amsar ta zamo  zama sifil!

**Koyo**

<u>Gabatar da lissafin ɗebewa ta tsaye (minti 10)</u>

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi yadda ake debe lambobi da sauya-suna.*
- Rubuta fasalin lissafin 48 – 29 = ___ a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Idan za mu ɗebe lambobi, za mu fara da ɗebewar da lamba biyu da ke gidan ɗaya. Za mu bi hanyar tsaye wajen ɗebewar. Nawa ne 8 - 9? Kash, ba zai yiwu ba! Lambar ƙasa ta ɗara ta sama, dole mu je gidan goma mu yi aro!*
- Nuna wa ɗalibai yadda za a share 4 da ke gidan goma a sama a rubuta 3. Akwai goma 4, amma sun zama  goma 3 yanzu. Gaba, sai a tara goma 1 da 8. 10 + 8 = 18.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu gidan ɗaya na sama ya ɗara na ƙasa, sai mu ci gaba da lissafi! Nawa ne 18 - 9?*
- Rubuta 9 a layin ƙasa gidan ɗaya.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu, sai mu debe a gidan goma. Nawa ne 3 - 2?*
- Rubuta 1 a layin ƙasa, sai mu yi lissafin fasalin:  36 – 17 = 19.

```
  48
- 29
----

 3 18
 4̶8̶
- 29
----
  19
```

**Gwaji**

<u>Aiki a ɗaiɗai ko bibbiyu: Ɗebewa ta tsaye da ragowa (minti 15)</u>

- Rubuta wannan lissafin ta tsaye a kan allo:
  33  – 25 = ___    ;    11 – 9 = ___    ;    21– 16 = ___
- Umurci ɗalibai da su warware sauran fasalin lissafin da ke gwaji a cikin littafasnsu na rubutu. Za su iya aikin a ɗaidaiku ko kuma a bibbiyu.

**Bayyanawa**

<u>Gaggauta auna fahimci (minti 5)</u>

- A sa ɗalibai su ɗaga takardarsu sama su nuna abin da suka rubuta. A yaba musu.

**Aikin Gida**

Umurci ɗalibai da su warware sauran fasalin lissafin da ke gwaji a cikin littafasnsu na rubutu. Za su iya aikin a ɗaiɗaiku ko kuma a bibbiyu.

| Na. 120 | Zango na 2, Mako na 12, Darasi na E |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya warware aikin lissafi ta amfani da ɗebewa.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasai

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Rera waƙa (minti 3)

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

> Rera waƙar ɗebewa
> Manyan lambobin da ke sama, ɗebe a ciki!
> Manyan lambobin da ke ƙasa, tsaya mu yi aro.
> Lambobin da suke iri ɗaya?
> Amsar ta zama sifil!

## Koyo

Warware aiki lissafin ɗebewa da ragowa (minti 10)

- Bada wannan labari: Wata bishiya kusa da ƙauyen na ɗauke da lemu 30. Bayan tashi daga makaranta, wasu yara suka je suka tsinki lemun suka sha. Sun sha lemu 11 a bishiyar. Lemu nawa suka yi saura a jikin bishiyar?
- Kira wani ɗalibi ya rubuta fasalin lissafin a kan allo.
- ***Ka/ki ce:*** *Akwai lemu 30 aka sha 11. Idan muna son mu sami adadin sauran lemun da ba a sha ba, sai mu ɗebe.*
- Tabbata fasalin lissafi 30 – 11 = ___ na rubuce a kan allo.
- A kira wani/wata ɗalibi/daliba ya/ta je kan allo asamar da amsar fasalin.
- Taimaka yayin yin aron.

```
 30
- 11
----

 2 10
 30
- 11
----
 19
```

## Gwaji

Aiki cikin ƙaramin rukuni : Warware aikin lissafi ta amfani da ɗebewa (minti 15)

- Ɗalibai su zazzauna a ƙananan rukuni.
- **Ka/ki ce:** *Isa da ƙanwarsa suka je kasuwa suka sayo ayaba 20. A lokacin cin abincin dare, iyalansu suka ci ayaba 11. Ayaba nawa suka yi saura?*
- Yi ta maimaita aikin lissafin da ke cikin labarin ta yadda za su fahimci abin da ake faɗi.
- Sa kowane ɗalibi ya rubuta fasalin lissafin labarin a cikin littafinsa na rubutu.
- Da zarar kowane ɗalibi ya rubuta fasalin, sai a sa su yin aikin tare wajen samar da amsa. Su gwada warware aikin lissafin ta hanyar lissafin tsaye da kwance.
- A kewaya a ga abin da ɗaliban ke yi da kuma taimaka masu. Idan da lokaci, a sake bada wani aikin warware lissafin.

## Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- Sa ɗaliban su bayyana wa juna abin da suka yi a rukuninsu.

## Aikin Gida

A ce wa ɗalibai su ba da amsar 72 - 38 = ___ cikin littafin rubutusu aikin gida.

| Na. 121 | Zango na 3, Mako na 1, Darasi na A |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su yi lissafin tarawa ta hanyar amfani da Naira.
**Kayan Aiki:** Takardun Naira na wasa **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

> Ina ʻyan yara, ina ʻyan yara, ina ʻyan yara yaran yanzu.
> Mu ne yara mu ne yara mu ne yara yaran yanzu.
> Ina ʻyan yara manyan gobe.Mu ne yara manyan gobe.
> Mu koyi karatu ʻyan yara. Don muzan manyan gobe.

Waƙa (minti 3)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.
- Nemi ɗaya daga cikin ɗaliban ya/ta fito gaban aji domin rerawa ʻyan aji waƙar.

## Koyo

Tarawa da Naira (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu gwada lissafin tarawa da takardun Naira na wasa.*
- Ɗaga takardun kuɗin wasa na Naira daban-daban (tsakanin ₦5 zuwa ₦500).
- Umurci ɗalibi/ ɗaliba ɗaya ya/ta fito gaban aji, sannan a ba shi/ta takardar kuɗi ta ₦100 da ₦50 da kuma ₦200.

```
  ₦100
  ₦ 50
+ ₦200
```

- **Ka/ki ce:** *Kuɗi nawa nake da su gabaɗaya?*
- A sa ɗalibi/ɗalibar ya/ta rubuta fasalin lissafin a kan allo.
- A tabbatar fasalin lissafin 100 + 50 + 200 = aka rubuta.

```
  ₦ 100
  ₦  50
+ ₦ 200
  ₦ 350
```

- **Ka/ki ce:** *Za mu iya gano amsar wannan aikin lissafin ta hanyar amfani da tarawa a tsaye. Idan muka tara su a tsaye, akwai buƙatar mu tabbatar dukkan daiɗaya suna jere cikin layi. Babu wata damuwa ko ya kasance gidajen goma-goma da ɗari-ɗari ba su da wata ƙima, sai dai a kullum ana jera lambobi ne ta hanyar farawa da gidan daiɗaya.*
- **Ka/ki ce:** *Yanzu mu fara da gidan ɗaiɗaya. Nawa ne 0 + 0 + 0?*
- **Ka/ki ce:** *Daga nan sai kuma a tara gidan goma-goma. Nawa ne 0 + 5 + 0?*
- **Ka/ki ce:** *Daga ƙarshe, sai mu tara gidan ɗari-ɗari. Nawa ne 1 + 0 + 2? Kada a manta idan ba a sami wata ƙima a ɗaya daga cikin gidajen nan, sai mu ɗauka cewa 0 ne a gidan.*
- Rubuta amsar ₦350 a ƙasan layi.

## Gwaji

Aiki a ƙananan ƙungiyoyi: Tarawa da takardun Naira (minti 15)

- A sa ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunoni. Zaɓi shugaba 1 daga kowane rukuni da za su taimaka wajen raba takardun kuɗi na wasa guda 3 wa ʻyan rukuninsu.
- A yi wa ɗalibai bayanin cewa su yi aiki tare don su rubuta fasalin lissafi da zai taimaka a gano yawan kuɗin da suke da shi. Ɗalibai su rubuta fasalin lissafin da kuma amsoshinsu a cikin littafan rubutunsu.
- Idan akwai lokaci, a sa ɗalibai su gwada kasuwanci da kuɗinsu da ʻyan wata rukunin sannan su rubuta wani fasalin lissafin.

## Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa wani ɗalibi/ɗaliba daga kowane rukuni da su bayyana aikinsu wa sauran ʻyan aji.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su tara ₦200 + ₦100 + ₦500 = ₦___ a cikin litattafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 122 | Zango na 3, Mako na 1, Darasi na B |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su yi lissafin ɗebewa ta hanyar amfani da Naira.
**Kayan Aiki:** Takardun kuɗi na wasa. **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Ina 'yan yara, ina 'yan yara, ina 'yan yara yaran yanzu.
Mu ne yara mu ne yara mu ne yara yaran yanzu.
Ina 'yan yara manyan gobe.Mu ne yara manyan gobe.
Mu koyi karatu 'yan yara. Don muzan manyan gobe.

Waƙa (minti 2)

- Ku rera waƙar tare da ɗalibai.

**Koyo**

Ɗebewa da takardun Naira (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu gwada lissafin ɗebewa da takardun Naira.*
- Ɗaga takardun kuɗin wasa na Naira daban-daban (tsakanin ₦5 zuwa ₦500).
- Umurci ɗalibi/ɗaliba ɗaya ya/ta fito gaban aji, sannan a ba shi/ta takardar kuɗi ta ₦500.

₦500
- ₦200

- **Ka/ki ce:** *Ka/kina da* ₦500! A ɗauka cewa ka/kina son sayan wani abu na musamman na ₦200. Kuɗinka/ki nawa ne zai rage?
- **Ka/ki ce:** *Kuɗi nawa nake da su gabaɗaya?*
- A sa ɗalibi/ɗalibar ya/ta rubuta fasalin lissafin ɗebewa a kan allo.
- A tabbatar da cewa fasalin lissafin 500 - 200 = aka rubuta.

₦500
- ₦200
₦300

- **Ka/ki ce:** *Za mu iya gano amsar wannan aikin lissafin ta hanyar amfani da ɗebewa a tsaye. Idan muka ɗebe lambobi a tsaye, akwai buƙatar mu tabbatar dukkan ɗaiɗaya suna jere cikin layi. Babu wata damuwa ko ya kasance gidajen goma-goma da ɗari-ɗari ba su da wata ƙima, sai dai a kullum ana jera lambobi ne ta hanyar farawa da gidan ɗaiɗaya.*
- **Ka/ki ce:** *Yanzu mu fara da gidan ɗaiɗaya. Nawa ne 0 - 0?*
- **Ka/ki ce:** *Daga nan sai kuma a tara gidan goma-goma. Nawa ne 0 - 0?*
- **Ka/ki ce:** *Daga ƙarshe, sai mu tara gidan ɗari-ɗari. Nawa ne 5 - 2?*
- Rubuta amsar ₦300 a ƙasan layi.
- Idan akwai lokaci, a maimaita da wani aikin lissafin.

**Gwaji**

Aiki a ƙananan rukunoni : Tara takardun Naira (minti 15)

- A sa ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunoni. Zaɓi shugaba 1 daga kowane rukuni da za su taimaka wajen raba takardun kuɗi na wasa guda 3 wa 'yan rukuninsu.
- A yi wa ɗalibai bayanin cewa su yi aiki tare don su rubuta fasalin lissafi da zai taimaka a gano yawan kuɗin da suke da shi. ɗalibai su rubuta fasalin lissafin da kuma amsoshinsu a cikin littafan rubutunsu.
- Idan akwai lokaci, a sa ɗalibai su gwada kasuwanci da kuɗinsu da 'yan wani rukunin sannan su rubuta wani fasalin lissafin.

**Bayyanawa**

Auna fahimta da Bayyanawa (minti 5)

- A sa wani ɗalibi ko wata ɗaliba daga kowane rukuni da su bayyana aikinsu wa sauran 'yan aji.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su gano amsar wannan ₦50 - ₦20 = ₦___ a cikin litattafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 123 | Zango na 3, Mako na 1, Darasi na C |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su gano kuɗin abubuwa a cikin Naira.
**Kayan Aiki:** Takardun kuɗin Naira na wasa **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Ina 'yan yara, ina 'yan yara, ina 'yan yara yaran yanzu.
Mu ne yara mu ne yara mu ne yara yaran yanzu.
Ina 'yan yara manyan gobe.Mu ne yara manyan gobe.
Mu koyi karatu 'yan yara. Don muzan manyan gobe.

Waƙa (minti 2)

- Ku rera waƙar tare da ɗalibai.

**Koyo**

Gabatarwa a kan kuɗin abubuwa a Naira (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu gano kuɗin abubuwa daban-daban a Naira*.
- Rubuta jerin abubuwa da ake yawan amfani da su tare da farashinsu a kan allo: Fensiri = ₦20, Rula = ₦50, Littafin Rubutu = ₦70, Buredi = ₦250, Sikari = ₦500
- Bayan an jera dukkan farashin a yi wa yara tambayoyi.
- **Ka/ki ce:** *Ina son sayan fensiri. Nawa ne kuɗinsa?*
- **Ka/ki ce:** *Ina son sayan rula. Nawa ne kuɗinta?*
- **Ka/ki ce:** *Ina son sayan littafin rubutu da rula. Nawa ne kuɗinsu?*
- A umurci ɗalibi/ɗaliba ya/ta fito gaban aji sannan a ce ya/ta rubuta fasalin lissafi da za a gano jimillar kuɗin rula da littafin rubutu.
- A gano amsar: ₦70 + ₦50 = ___
- A tabbatar amsar ɗalibai ita ce ₦120.

**Gwaji**

Aiki a ƙananan rukunoni: Gano kuɗin abubuwa a cikin Naira (minti 15)

- A sa ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunoni. Zaɓi shugaba 1 daga kowane rukuni da za su taimaka wajen raba takardun kuɗi na wasa guda biyar wa 'yan rukuninsu.
- Ta hanyar amfani da jerin farashin da ke kan allo, a sa ɗalibai su tattauna a kan abubuwan da za su saya da kuɗinsu na wasa.
- A sa ɗalibai su zana hotunan kayan da za su saya a cikin litattafansu na rubutu. Sannan kuma su rubuta jimillar farashinsu. Haka kuma su zana takardun kuɗin da za su yi amfani da su wajen yin sayayyar.
- Zagaya domin lura da ɗalibai. Yayin da ake zagayawa , a riƙa tambayar yara yadda suka gano amsarsu. A tabbatar masu idan sun yi daidai

**Bayyanawa**

Auna fahimta da Bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibi/ɗaliba ɗaya daga kowane rukuni ya/ta bayyana aikinsu wa sauran 'yan ajin.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su tattauna farashin abubuwa na yau da kullum da za su iya saya tare da mutanen gidansu ko abokansu.

| Na. 124 | Zango na 3, Mako na 1, Darasi na D |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya rarrabewa da bayyana takardun kuɗi, sannan kuma su iya mayar da manyan kuɗi zuwa ƙanana.

**Kayan Aiki:** Takardun Naira na wasa **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Ina 'yan yara, ina 'yan yara, ina 'yan yara yaran yanzu.
Mu ne yara mu ne yara mu ne yara yaran yanzu.
Ina 'yan yara manyan gobe.Mu ne yara manyan gobe.
Mu koyi karatu 'yan yara. Don muzan manyan gobe.

Waƙa (minti 2)

- Ku rera waƙar tare da ɗalibai.

**Learn**

Bayanin takardun kuɗi (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau, za mu koyi yadda za a bayyana takardun Naira da kuma yadda za a fasa zuwa ƙananan kuɗi.*
- Rubuta dukkan kuɗaɗen Naira a kan allo: ₦5 da ₦10 da ₦20 da ₦50 da ₦100 da ₦200 da ₦500 da kuma ₦1000).
- Ɗaga kowace takarda ɗaya bayan ɗaya , sannan a tambayi ɗalibai wacce ce.
- **Ka/ki ce:** *Wani lokaci ana buƙatar manyan takardun kuɗi na Naira, kuma za a iya fasa su zuwa ƙanana ko wasu takardu masu ƙima daban-daban.*
- Kira ɗalibi/ɗaliba ɗaya gaban aji, sannan a ba shi/ta takardar kuɗin wasa ta ₦1000 guda ɗaya da kuma 'yan ₦500 guda biyu.
- **Ka/ki ce:** *Wanne ne ya fi yawa? Takardar ₦1000 ɗaya ko kuma takardar ₦500 guda biyu?*
- A tambayi ɗalibai nawa ne 500 + 500.
- **Ka/ki ce:** *Takardar ₦1000 tana da ƙima iri ɗaya da takardun ₦500 guda biyu.*
- Kira ɗalibi/ɗaliba daban gaban aji, sannan a ba shi/ta takardar kuɗin wasa ta ₦100.
- A sa ɗalibai su gano sauran takardu da za su bayar da ƙima iri ɗaya da ita (Misali, takardun ₦50 guda biyu ko takardar ₦20 guda biyar).
- Idan akwai lokaci, a maimaita da wasu misalan.

**Gwaji**

Aiki a ƙananan rukunoni: Fasa manyan takardun kuɗin Naira (minti 15)

- A ce ɗaliban su buɗe Shafi na 52. A karanta wa ɗalibai umurnin a bayyane, sannan a samo amsar lissafin farko tare da su.
- A sa ɗalibai su yi aiki tare wajen fasa Naira zuwa ƙananan takardun kuɗi, sannan su rubuta fasalin lissafin a cikin littafin ɗalibai.
- A zagaya domin lura da ɗalibai da kuma ba su tallafi.

**Bayyanawa**

Auna fahimta da Bayyanawa (minti 5)

- A umurci wani ɗalibi/ɗaliba ya rubuta ɗaya daga cikin fasalin lissafin da suka rubuta a rukuninsu a kan allo, sannan ya yi bayanin yadda suka gano amsar.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 52 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 125 | Zango na 3, Mako na 1, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za suyi bita da gwajin aikin da aka gabatar a makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

> Ina ‘yan yara, ina ‘yan yara, ina ‘yan yara yaran yanzu.
> Mu ne yara mu ne yara mu ne yara yaran yanzu.
> Ina ‘yan yara manyan gobe.Mu ne yara manyan gobe.
> Mu koyi karatu ‘yan yara. Don muzan manyan gobe.

Waƙa (minti 2)

- Ku rera waƙar tare da ɗalibai.

**Koyo**

Bita da maimaitawa (minti 10)

- Zaɓi wani labari daga ayyukan mako da ake ganin kamar ɗalibai suna fama da shi. A sake maimaita koyar da shi ko kuma a koyar da shi ta wata hanyar daban.

**Gwaji**

Aiki a ɗaiɗaiku ko cikin rukunoni: Tarawa da ɗebewa da Naira (minti 15)

- A ba ɗalibai wani aiki wanda zai taimaka musu gwajin abin da ake bita a kansa (Misali, lissafin ɗebewa a Naira). Ɗalibai za su iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma cikin rukunoni.
- Yayin da ɗalibai suke mayar da hankalinsu a kan aikinsu, a samar da taimako ga waɗanda suke buƙata

**Bayyanawa**

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna ayyukan da suka kammala a lokacin gwaji.

**Aikin Gida**

A ba ɗalibai aikin gida don bita da gwajin abin da suka koya.

| Na. 126 | Zango na 3, Mako na 2, Darasi na A |
|---|---|


**Manufofi:** Ɗalibai za su yi amfani da rukuni-rukuni na ababen ƙirge da kuma ruɓanya tarawa don yin lissafin sau ɗin bibiyu.

**Kayan Aiki:** Ababen ƙirge (wake da tsakuwoyi) **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.




Labarin hoto (minti 5)

- Bayar da labarin hotunan da ke kan allo.
- **Ka/ki ce:** *Wata rana Sani yana kora garken shanunsa don su tsallake wani kogi mai ruwa. A hankali sai Sani ya fara da hayar da shanu guda 2 zuwa ɗaya gaɓar kogin. Sani ya yi irin haka sau 4 ya je ya dawo yana tsallaka kogin.*
- A sa ɗalibai 8 su fito gaban aji domin gwada aiwatar da labarin. A tambayi ɗalibai, shanu nawa yake da su gabaɗaya idan dai sai da ya yi sau 4 zuwa tsallaken kogin, kuma yana hayewa da shanu biyu a kowane lokaci.

## Koyo

Gabatar da lissafin sau da 2 (minti 8)

- **Ka/ki ce:***Yau za mu koyi yadda za mu yi sau da biyu ta hanyar amfani da ruɓanya tarawa. Ruɓanya tarawa shi ne yayin da muka yi ta tara lamba iri ɗaya sau da dama.*





- Rubuta wannan fasalin lissafin 2 + 2 + 2 + 2 = ___ a kan allo. Kidaya da bibiyu a bayyane har sai an sami amsar: 8.
- **Ka/ki ce:** *Bibiyu nawa ne a cikin wannan fasalin lissafin? Akwai bibiyu guda huɗu!*
- Yi amfani da da'irorin da aka zana a kan allo a gwada yadda za a sami rukunonin hurhuɗu guda biyu da ababen ƙirge.
- Idan akwai lokaci, maimaita da wanilissafin daban.

## Gwaji

Aiki a ƙananan rukuni : Tarawa da abubuwan ƙirge (minti 15)

- A sa ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunnai. A zaɓi shugaba ɗaya daga kowane rukuni don su taimaka wajen raba abubuwan ƙirge guda 20 da kuma katunan lambobi tsakanin 1 zuwa 10 wa 'yan rukuninsu.
- A sa ɗalibai su duba katin lambarsu, sannan su tara ababen ƙirge bibiyu har wannan adadin. Misali, idan lambar da take jikin katinsu 5 ce, sai su yi rukuni biyar na ababen ƙirge, kowane rukuni ɗauke da ababen ƙirge 2.




- Daga nan sai a sa ɗalibai su rubuta fasalin lissafi na ruɓanya tarawa da kuma sau a cikin litattafansu na aiki.
- Zagaya domin lura da ɗalibai sannan a tallafa musu. Idan akwai lokaci, a maimaita da wani lissafin daban ta hanyar zana wani katin.

## Bayyanawa

Bayyana kyawawan misalai (minti 5)

- A gano wani rukuni ko wasu rukunnai biyu su nuna fasalin lissafinsu wa sauran 'yan ajinsu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su rubuta wannan lissafin 2 + 2 + 2 = ___ a matsayin lissafin sau a cikin litattafansu na rubutu.


| Na. 127 | Zango na 3, Mako na 2, Darasi na B |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi amfani da rukuni-rukuni na ababen ƙirge da kuma ruɓanya tarawa a matsayin sau ɗin biyar-biyar.
**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge (wake da tsakuwoyi) **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.




Labarin hoto (minti 5)

- Bayar da labarin. Mahaifiya ta bayar da alawa biyar-biyar ga kowane daga cikin yaranta huɗu. Alawa nawa ta bayar gaba ɗaya?
- Gwada aiwatar da labarin ta hanyar sanya ɗaliba ɗaya ta zama ,mahaifiya, sannan a ba su alawa guda 5 (ko ababen ƙirge) ga kowane daga cikin ɗalibai huɗu da suke gaban aji.
- **Ka/ki ce:** *Rukunin alawa biyar-biyar nawa ake da su?*

**Koyo**

Gabatarwa a kan lissafin sau da biyar-biyar (minti 8)




- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi yadda za a yi sau da biyar-biyar.*
- Rubuta wannan fasalin lissafi 5 + 5 + 5 + 5 = ___ a kan allo. A ƙidaya da biyar-biyar da 'yan ajin har sai an zo kan amsar da ta dace: 20.
- **Ka/ki ce:** *Biyar-biyar nawa ne a cikin fasalin lissafin? Akwai biyar-biyar guda huɗu!*
- A yi amfani da ababen ƙirge don aiwatar da yadda za a samar rukunin 5 guda 4.
- **Ka/ki ce:** *Maimaikon a ce 5 a tara da 5 a tara da 5 a tara da 5, sai kawai mu rubuta 5 x 4. Sau shi ne tara rukunin abin da yawansu ɗaya sau wani adadi. A wannan hali, mun tara biyar-biyar sau huɗu.*
- A yi wa ɗalibai bayanin cewa, alamar x tana nuna cewa ana yin sau da lambobin da aka nuna.
- Idan akwai lokaci, a maimaita da wani lissafin.

**Gwaji**

Aiki a ƙananan ƙungiyoyi: Tarawa da abubuwan ƙirge (minti 15)

- A sa ɗalibai su zauna cikin ƙananan ƙungiyoyi. A zaɓi shugaba ɗaya daga kowane rukuni don su taimaka wajen raba abubuwan ƙirge guda 50 da kuma katunan lambobi tsakanin 1 zuwa 10 wa 'yan rukuninsu.
- A sa ɗalibai su duba katin lambarsu, sannan suyi rukunin abubuwan ƙirge biyar-biyar har wannan adadin. Misali, idan lambar da take jikin katinsu 3 ce, sai su yi rukuni uku na abubuwan ƙirge, kowane rukuni ɗauke da abubuwan ƙirge 5.
- Daga nan sai a sa ɗalibai su rubuta fasalin lissafi na ruɓanya tarawa da kuma sau.
- Zagaya domin lura da ɗalibai sannan a tallafa musu. Idan akwai lokaci, a maimaita da wanilissafin daban ta hanyar zana wani katin.

**Bayyanawa**

Bayyana kyawawan misalai (minti 5)

- A gano wani rukuni ko wasu rukunnai biyu su nuna fasalin lissafinsu wa sauran 'yan ajinsu.

**Aikin Gida**


A sa ɗalibai su rubuta wannan matsalar 5 + 5+ 5 + 5 + 5 + 5 = ___ a matsayin lissafin sau a cikin litattafansu na rubutu.

| Na. 128 | Zango na 3, Mako na 2, Darasi na C |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai su iya amfani da haɗa abubuwan ƙirge da lissafin ruɓunya tarawa wajen yin lissafin sau na goma-goma
**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge (wake ko tsakuwa), zanen gidan goma **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)



- A gurguje a duba aikin gida. A faɗa musu sakamakon aikinsu, sannan a ƙarfafa musu guiwa.


Labarin hoto (minti 5)

- Bayar da labarin. A kusa da wani ƙauye akwai bishiyoyin lemu guda goma. A jikin kowace bishiya akwai lemu guda 4. Duka-duka lemu guda nawa ne?
- **Ka/ki ce:** *Rukunin lemu hur huɗu nawa ake da su?*

## Koyo

Gabatarwa a kan lissafin sau da goma-goma (minti 8)

10 + 10 + 10 + 10 = 40
10 x 4 = 40



- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi yadda za a yi sau da goma-goma.*
- Rubuta wannan fasalin lissafin 10 + 10 + 10 + 10 = ___a kan allo. A ƙidaya da goma-goma da 'yan ajin har sai an zo kan amsar da ta dace: 40.
- **Ka/ki ce:** *Goma-goma nawa ne a cikin fasalin lissafin? Akwai goma-goma guda huɗu!*
- A yi amfani da abubuwan ƙirge don gwada aiwatar da yadda za a samar rukunin 10 guda 4.
- **Ka/ki ce:** *Maimaikon a ce 10 a tara da 10 a tara da 10 a tara da 10, sai kawai mu rubuta 10 x 4. Sau shi ne tara rukunin abin da yawansu ɗaya sau wani adadi. A wannan hali, mun tara goma-goma sau huɗu.*
- Idan akwai lokaci, a maimaita da wata matsalar.

## Gwaji

Aiki a ƙananan ƙungiyoyi: Tarawa da ababen ƙirge (minti 15)

- A sa ɗalibai su zauna cikin ƙananan ƙungiyoyi. A zaɓi shugaba ɗaya daga kowane rukuni don su taimaka wajen raba abubuwan ƙirge guda 50 da kuma katunan lambobi tsakanin 1 zuwa 5 wa 'yan rukuninsu.
- A sa ɗalibai su duba katin lambarsu, sannan suyi rukunin ababen ƙirge goma-goma har wannan adadin. Misali, idan lambar da take jikin katinsu 3 ce, sai su yi rukuni uku na ababen ƙirge, kowane rukuni ɗauke da ababen ƙirge 10.
- Daga nan sai a sa ɗalibai su rubuta fasalin lissafi na ruɓanyawa, tarawa da kuma sau.
- Zagaya domin lura da ɗalibai sannan a tallafa musu. Idan akwai lokaci, a maimaita da wani lissafin daban ta hanyar zana wani katin.

## Bayyanawa

Bayyana kyawawan misalai (minti 5)

- A gano wani rukuni ko wasu rukunoni biyu su nuna fasalin lissafinsu wa sauran 'yan ajinsu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su rubuta wannan lissafin 10+ 10 = ___ a matsayin matsalar lissafin sau a cikin litattafansu na rubutu.

| Na. 129 | Zango na 3, Mako na 2, Darasi na D |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai zai su yi amfani da ruɓanya tarawa don su yi sau na 2 da 5 da kuma 10.
**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge (wake da tsakuwoyi), layin lambobi **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Biyu sau ɗaya biyu / Biyu sau biyu huɗu
Biyu sau 3 Shida / Biyu Sau 4 Takwas
Biyu sau 5 Goma / Biyu sau 6 goma sha biyu
Biyu sau bakwai goma sha huɗu /
Biyu sau Takwas goma sha shida
Biyu  sau Tara goma sha takwas /
Biyu sau Goma Ashirin

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.
- Nemi wani ɗalibi ko wata ɗaliba ya/ta fito gaban aji domin rera waƙar ga sauran ʻyan aji.

### Koyo

Bitar sau ta hanyar maimaita tara lambobi (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu ci gaba da yin sau da lambobi ta hanyar ruɓanya tarawa.*
- A umurci ɗalibai biyu su fito gaban aji. A tambayi sauran ʻyan aji ɗalibai nawa ne a gaban aji. Daga nan sai a sake kiran wasu ɗaliban guda biyu zuwa gaban aji, sannan a ce su tsaya tare a gefe.
- **Ka/ki ce:** *Da muna da ɗalibai guda 2, sannan sai muka ƙara wasu ɗaliban guda 2. Yanzu ɗalibai nawa muke da su gaba ɗaya?*
- Kidaya yawan ɗaliban gaba ɗaya a bayyane tare da dukkan ʻyan aji. A sake kiran wasu ɗaliban gaban aji.
- **Ka/ki ce:** *Mun ƙara wasu ɗaliban guda 2. Yanzu kuma ɗalibai nawa muke da su?*
- Rubuta 2+2+2 = 6 a kan allo.
- **Ka/ki ce:** *2 a tara da 2 a tara da 2 sun zama 6. Mun tara 2 guda uku. Za mu iya rubuta fasalin ta hanyar ruɓanya tarawa, ko  kuma mu sanya alamar sau.*
- Rubuta 3 x 2 = 6 a kan allo.
- Idan akwai lokaci a maimaita da wasu ɗalibai na daban da rukunin biyar-biyar da goma-goma.

### Gwaji

Aiki a ɗaiɗaiku da kuma cikin bibiyu: Yin sau da 2 da 5 da kuma 10 (minti 15)

- A ce ɗaliban su buɗe littafin ɗalibai Shafi na 53.
- A karanta wa ɗalibai umurni da tambayar farko a bayyane. A sa ɗalibai su samo amsar lissafin farko a cikin litattafansu na aiki. Za su iya tattauna amsoshinsu da abokan aikinsu.
- A zagaya domin lura da ɗalibai yayin da ake zagayawa a riƙa tambayar su yadda aka yi suka gano amsoshinsu, sannan a tabbatar musu idan sun yi daidai.
- Idan da lokaci, a ƙarasa sauran tambayoyin da suke wannan shafin.

### Bayyanawa

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu domin nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai.

### Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 53 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 130 | Zango na 3, Mako na 2, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za suyi bita da gwajin aikin da aka gabatar a makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu sannan a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)

- Ku rera waƙar tare da ɗalibai.

Biyu sau ɗaya biyu / Biyu sau biyu huɗu
Biyu sau 3 Shida / Biyu Sau 4 Takwas
Biyu sau 5 Goma / Biyu sau 6 goma sha biyu
Biyu sau bakwai goma sha huɗu /
Biyu sau Takwas goma sha shida
Biyu sau Tara goma sha takwas /
Biyu sau Goma Ashirin

**Koyo**

Bita da maimaitawa (minti 10)

- Zaɓi wani batu daga ayyukan mako da ake ganin kamar ɗalibai suna fama da shi. A sake maimaita koyar da shi ko kuma a koyar da shi ta wata hanyar daban.

**Gwaji**

Aiki a ɗaiɗaiku ko cikin ƙungiyoyi: Zanawa da rubutawa (minti 15)

- A ba ɗalibai wani aiki wanda zai taimaka musu gwajin abin da ake bita a kansa (Misali, tara ninkakkun lambobi har zuwa goma ta hanyar amfani da dami-dami ko layin lambobi). Ɗalibai za su iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma cikin ƙungiyoyi.
- Yayin da ɗalibai suke mayar da hankalinsu a kan aikinsu, a samar da wani taimako ga waɗanda suka fi buƙatarsa

**Bayyanawa**

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna ayyukan da suka kammala a lokacin gwaji.

**Aikin Gida**

A ba ɗalibai aikin gida don bita da gwajin abin da suka koya.

| Na. 131 | Zango na 3, Mako na 3, Darasi na A |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya ƙiyasin faɗi da nisa.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masugwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Mage doguwa. Kwalba gajera.
Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
Randa da girma. Moda 'yar karama.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

## Koyo

Kiyasun faɗi da nisa (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi wani abu a kan faɗi da nisa. Faɗi da nisa sukan nuna tazarar da take tsakanin wurare biyu ne. A faɗi akan auna tsakanin ƙarshe da ƙarshen abu. Shi kuma nisa a kan gwada filin da yake tsakanin wurare biyu ne.*
- Nuna wa 'yan aji itatuwa guda biyu: ɗaya gajere da kuma ɗaya dogo.
- Nuna kalmomin guda biyu "Dogo" da "Gajere" da aka rubuta a kan allo.
- A yi bayanin cewa akan danganta abubuwa guda biyu. Yayin dangantawar ana amfani da kalmar "fi" a gaban kalma. Ɗaga ɗaya daga cikin itatuwan, sai a yi bayanin wanda ya fi tsawo da wanda ya fi gajarta.
- Kara "fi" a gaban kalmar "tsawo" da "Gajarta" a kan allo. A sa yaran su maimaita "Fin tsawo" da "Fin gajarta" bayan ka/kin faɗa.
- A sa ɗalibai biyu su fito gaban aji. A sa ɗaya daga cikinsu ɗaga fensir, ɗaya kuma ɗaga itace. A tambayi ɗalibai wanne ne ya fi tsawo.
- **Ka/ki ce:** *Haka kuma muna amfani da kalmomin 'fin tsawo' da 'fin gajarta' wajen yin bayanin nisan da yake tsakanin wurare biyu. Wane ne ya fi tsawo? Tsakanin tafiya daga nan zuwa aji da kuma daga nan zuwa gida?*
- Idan akwai lokaci, a ba ɗalibai dama su yi bayanin fin tsawo da fin gajarta ta hanyar amfani da misalansu.

## Gwaji

Aiki ɗaiɗaya ko bibiyu: Kiyasin faɗin abu (minti 15)

- A sa ɗalibai su buɗe littafinsu Shafi na 54. Karanta umurnin a bayyane wa ɗalibai. Ku gano amsar lissafin farko tare da ɗalibai.
- A sa ɗalibai su gano amsar tambaya ta gaba. Za su iya aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma tare da abokan aikinsu.
- A zagaya domin lura da ɗalibai sannan kuma a ba su tallafi.

## Bayyanawa

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu domin nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 54 a cikin littafansu na rubutu matsayin aikin gida.

| Na. 132 | Zango na 3, Mako na 3, Darasi na B |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su auna faɗin abubuwan cikin aji da ma'aunin da ba tsayayye ba.

**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masugwiwa.

Waƙa (minti 3)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Mage doguwa. Kwalba gajera.
Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
Randa da girma. Moda 'yar karama.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

## Koyo

Gabatarwa wajen auna abubuwa (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi yadda za mu gwada abubuwa daban-daban ta hanyar amfani da kaya aiki iri-iri, har da ma hannaye da ƙafafunmu!*
- Zana wata taswira a kan allo sannan a yi wa ɗalibai bayanin cewa, za a auna faɗin allo ta hanyar ɗamtsen hannaye.



| Awo | Malami | Ɗalibi |
|---|---|---|
| Tsawon allo | Tsawon hannu ____ | Tsawon hannu ____ |

- Ɗamtse dukkan hannayenka/ki (Kamar za a fitar da gaba guda). A ƙidaya gaba nawa daga ƙarshen allo zuwa wani ƙarshen. Misali idan an samu gaba uku sai a rubuta "3" a kan allo.
- A sa wani ɗalibi ko wata ɗaliba ya/ta fito gaban aji domin auna faɗin allo ta hanyar amfani da gaba. A rubuta yawan gaban da aka samu a jikin taswirar amma a saka ɗalibi/ɗaliba.
- A tambayi ɗalibai, bayan wannan hanyar me kuma za su iya amfani da shi wajen auna faɗin abu. (kamar tef ko taku ko ɗani wato amfani da babbar yatsa da manuniya da sauransu)

## Gwaji

Aiki cikin bibiyu: Awon abubuwa (minti 15)

- A faɗa wa ɗalibai za su yi aiki cikin bibiyu. A ce su buɗe litattafansu zuwa Shafi na 55.
- Karanta umurni da tambayar farko a bayyane ga ɗalibai.
- A yi wa ɗalibai bayanin cewa, su auna faɗin littafin karatunsu ta hanyar amfani da babbar yatsa da manuniya. A rubuta ɗani nawa kowane yaro ya samu a cikin litattfansu na aiki.
- A zagaya domin lura da ɗalibai. Yayin da ake zagayawa a riƙa tallafa wa ɗalibai wajen aikin awun da suke yi, sannan kuma a tabbatar musu idan sun yi daidai. Idan akwai lokaci a ƙarasa gano amsar lissafi n gaba da yake shafin.

## Bayyanawa

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu domin nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su ƙarasa sauran aikin da ke Shafi na 55 a cikin littafan rubutunsu a matsayin aikin gida. A ce su sami wani abokinsu ko ɗan gidansu suyi aikin tare.

| Na. 133 | Zango na 3, Mako na 3, Darasi na C |
|---|---|

**Manufar Darasi:** Ɗalibai za su auna tazara a wajen aji da raunannen ma'auni.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masugwiwa.

Waƙa (minti 3)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Mage doguwa. Kwalba gajera.
Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
Randa da girma. Moda 'yar karama.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

## Koyo

Gabatarwa kan awun tazara (minti 10)

| Awo | ɗalibi 1 | ɗalibi 2 |
|---|---|---|
| Tsawon aji | Tsalle _____ | Tsalle _____ |

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi yadda za mu koyi auna tazara daban-daban ta hanyar amfani da kayan aiki iri-iri, har da ma hannaye da ƙafafunmu!*
- Zana wata taswira a kan allo sannan a yi wa ɗalibai bayanin cewa, za a auna faɗin aji da tsalle.
- A saka wani ɗalibi ko wata ɗaliba ya/ta yi tsalle daga ɓangare ɗaya na aji zuwa ɗaya ɓangaren. Daga nan sai a rubuta yawan tsallen a ƙarƙashin sunan ɗalibin ko ɗalibar a kan allo. A maimaita da wani ɗalibin ko wata ɗalibar.
- A tambayi ɗalibai, bayan wannan hanyar, me kuma za su iya amfani da shi wajen auna tazara. (kamar tef ko taku ko amfani da buɗa hannaye da sauransu)

## Gwaji

Aiki cikin bibiyu: Awon tazara (minti 15)

- A faɗa wa ɗalibai za su yi aiki cikin bibiyu. A ce su buɗe litattafansu zuwa Shafi na 56.
- Karanta umurni da tambayar farko a bayyane wa ɗalibai.
- A yi wa ɗalibai bayanin cewa, su auna tazara a cikin filin makaranta ta hanyar amfani da yawan taku. A rubuta takun da kowane yaro ya samu a cikin litattfansu na aiki.
- A zagaya domin lura da ɗalibai. Yayin da ake zagayawa a riƙa tallafa wa ɗalibai wajen aikin awon tazarar da suke yi, sannan kuma a tabbatar masu idan sun yi daidai. Idan akwai lokaci a ƙarasa gano amsar lissafin na gaba da yake shafin.

## Bayyanawa

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu domin nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 56 a cikin littafansu na aiki a matsayin aikin gida. A ce su sami wani abokinsu ko ɗan gidansu su yi aikin tare.

| Na. 134 | Zango na 3, Mako na 3, Darasi na D |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya auna faɗin abu ta hanyar amfani da irin rular nan da ake naɗewa.
**Kayan Aiki**: Rula da ake naɗewa da kuma rula **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masugwiwa.

Waƙa (minti 3)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Mage doguwa. Kwalba gajera.
Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
Randa da girma. Moda 'yar karama.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

**Koyo**

Gabatarwa a kan tsayayyen awu (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Mun auna faɗi da tazara da ababen awo daban-daban: hannayenmu da ƙafafuwanmu da kuma yatsunmu. Amma saboda kasancewar muna da bambancin halitta, sai awon mu ya bambanta a tsakaninmu. Wani lokaci muna son mu sami awon da zai bayar da hakiƙanin gaskiyar abin da muka auna, don haka sai mu yi amfani da rula don mu auna faɗi yadda za mu gano har da sentimita. Duk wanda ya yi amfani da rula (a duk faɗin duniya) zai sami irin wannan sakamako na awo na faɗin abu.*
- Ɗaga rula ga 'yan ajin kowa ya gani. A yi wa yara bayanin layi-layin da yake jikin rular (da aka fi sani sentimita) sannan a bayar da misalan abubuwan da za a iya aunawa da rula cikin sentimita.
- **Ka/ki ce:** *Yanzu bari mu yi gwajin awun faɗin allo cikin mita.*
- Nuna yadda za a yi awo da rula. A yi bayanin cewa idan ba a sami wadda za a auna faɗi da mita-mita ba, sai a ƙirga sentimita, sannan sai a tara su yadda za su kai mita.
- Rubuta faɗin allon cikin mita da sentimita a kan allo.
- A tambayi 'yan aji wani abu daban da suke son auna faɗinsa, sannan sai a nemi ɗaya daga cikinsu ya/ta zo gaban aji ya/ta auna faɗin da rula.

**Gwaji**

Aiki cikin bibiyu: Auna abubuwa (minti 15)

- A faɗa wa ɗalibai za su yi aiki cikin bibiyu. A ce su buɗe litattafansu zuwa Shafi na 57.
- Karanta umurni da tambayar farko a bayyane wa ɗalibai. A sa ɗalibai su rubuta hakiƙanin awun da kowane ɗalibi ya yi a cikin littafin aikinsa.
- A zagaya domin lura da ɗalibai. Yayin da ake zagayawa a riƙa tallafa wa ɗalibai wajen aikin awon da suke yi, sannan kuma a tabbatar musu idan sun yi daidai. Idan akwai lokaci a ƙarasa gano amsar lissafi na gaba da yake shafin.

**Bayyanawa**

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu domin nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 57 a cikin littafansu na aiki a matsayin aikin gida. A ce su sami wani abokinsu ko ɗan gidansu su yi aikin tare.

Na. 135

# Zango na 3, Mako na 3, Darasi na E

**Manufofi:** Ɗalibai za suyi bita da gwajin aikin da aka gabatar a makon.

**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafamasu gwiwa.

Waƙa (minti 2)

- Ku rera waƙar tare da ɗalibai.

Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Mage doguwa. Kwalba gajera.
Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
Randa da girma. Moda 'yar karama.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

## Koyo

Bita da maimaitawa (minti 10)

- Zaɓi wani batu daga ayyukan mako da ake ganin kamar ɗalibai suna fama da shi. A sake maimaita koyar da shi ko kuma a koyar da shi ta wata hanyar daban.

## Gwaji

Aiki a ɗaiɗaiku ko cikin ƙungiyoyi: Zanawa da rubutawa (minti 15)

- A ba ɗalibai wani aiki wanda zai taimaka musu gwajin abin da ake bita a kansa (Misali, auna faɗi da tazara da tsayayyu da kuma ma'aunai marasa fasali). Ɗalibai za su iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma cikin ƙungiyoyi.
- Yayin da ɗalibai suke mayar da hankalinsu a kan aikinsu, a samar da wani taimako ga waɗanda suka fi buƙatarsa

## Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna ayyukan da suka kammala a lokacin gwaji.

## Aikin Gida

A ba ɗalibai aikin gida don bita da gwajin abin da suka koya.

| Na. 136 | Zango na 3, Mako na 4, Darasi na A |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai su iya kimanta tsayi da faɗi.

**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Labari da gwada aiwatarwa (minti 5)

- Bada labarin. Wani tela yana son ya ɗinka wa wata yarinya Binta kyakkyawar riga. Telan yana son sanin adadin yadin zai yi wa Binta.
- A tambayi ɗalibai yadda telan zai yi ya san adadin yadin da zai yi wa Binta.
- Nuna wa ɗalibai yadda za a auna tsayin rigar Binta. A sami wata ɗaliba ta tsaya jikin bango sai a ja layin tsayinta daidai da kafaɗarta da alli. Yi amfani da hannu wajen auna tsayin daga ƙasa zuwa sama.

### Koyo

Kimanta tsayi (minti 5)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi yadda ake auna tsayi da faɗi. Tsayi shi ne sanin tsawo ko gajartar abu. Za mu iya auna tsayi kamar yadda ake auna tazara da tsawo.*
- Kira wasu ɗalibai su je gaban aji su tsaya gefen juna.
- Nuna kalmar "dogo" da "gajere" da ke rubuce a allo.
- Yi bayani cewa yayin kwatanta tsayi sai mu ƙara "fi" kafin kalmar. Sake nuna ɗaliban a bayyana wanda ya fi tsawo da gajere.
- Maimaita da wasu ɗaliban.

Kimanta faɗi (minti 5)

- **Ka/ki ce:** *Yanzu, bari mu auna faɗi.* Faɗi shine tazara ko tsukewar abu.
- ɗaga littafi biyu sama sannan a bayyana bambancin girmansu a ajin su gani.
- Nuna gefen littafi sai a bayyana wa dalibai yadda ake gane faɗin abu.
- **Ka/ki ce:** *Idan za mu auna faɗin abu, za mu yi la'akari da "tsukewa" da "fadi". Idan za mu kwatanta abubuwa dangane da faɗinsu, sai mu ce "tsukakke" da "faffaɗa."*
- A tambayi ɗalibai littafin da yake da faɗi da kuma tsukakke.

### Gwaji

Aiki ɗaiɗai ko bibbiyu: Kimanta tsawo (minti 15)

- A sa ɗalibai su buɗe littafinsu Shafi na 58. Karanta musu umarnin su ji. Ku kammala aikin farko tare.
- A sa ɗalibai amsa tambaya ta gaba. Za su iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko bibbiyu.
- A kewaya a lura da abin da ɗalibai ke yi sannan a taimaka masu.

### Bayyanawa

Gaggauta auna fahimta (minti 3)

- A ce wa ɗalibai su ɗaga takardarsu sama su nuna abin da suka rubuta. A yaba masu.

### Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 58 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 137 | Zango na 3, Mako na 4, Darasi na B |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai su iya auna tsayin abubuwan da ke aji ta gargajiyar hanya.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Mage doguwa. Kwalba gajera.
Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
Randa da girma. Moda 'yar karama.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

### Koyo

Gabatar da awun tsayi (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi yadda ake auna abubuwa mabambanta ta amfani da abubuwan awo daban-daban, da ma hannunmu da ƙafafu!*

| Awo | Malami | Ɗalibi |
|---|---|---|
| Tsayin benci | ɗanin _____ | ɗanin _____ |

- Zana jadawali a kan allo sai a bayyana wa ɗalibai cewa za su auna tsayin bencinansu.
- Ku ƙirga ɗani nawa za a samu na tsayin bencin daga ƙasa zuwa sama sannan, a rubuta adadin a kan allo. Misali, idan ɗani uku aka samu, sai a rubuta "3" a kan allo.
- A sa wani ɗalibi shi ma ya auna tsayin bencinsu da ɗanin hannu. Rubuta ɗanin hannun a cikin jadawalin ƙarƙashin ɗalibi.
- A tambayi ɗalibai wani abun da za su iya auna tsayi da shi. (kamar lurar gwaji, takun ƙafa, ɗanin hannu, da sauransu).

### Gwaji

Aiki mutum biyu: Auna abubuwa (minti 15)

- A ce wa ɗalibai za su yi aiki su bibbiyu. A sa ɗalibai buɗe littafinsu Shafi na 59.
- Karanta wa ɗalibai umarnin da kuma tambayar farko su ji. A ce wa ɗalibai su rubuta awon da ya zama daidai da kowane ɗalibi a littafin rubutunsu.
- A kewaya a duba abin da ɗalibai suke yi. A yayin kewayawar, a taimaka masu wajen awon kuma a tabbatar masu da abin da suke yi daidai. Idan da lokaci ku kammala aikin da ke shafi na gaba.

### Bayyanawa

Gaggauta auna fahimta (minti 5)

- A ce wa ɗalibai su ɗaga takardarsu sama su nuna abin da suka rubuta. A yaba masu.

### Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 59 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.A ce wa ɗalibai su yi aiki tare da abokinsu ko wani ɗan uwa a gida a matsayin abokin aiki.

| Na. 138 | Zango na 3, Mako na 4, Darasi na C |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai su iya auna faɗin abubuwan da ke cikin aji a gargajiyance.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Mage doguwa. Kwalba gajera.
Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
Randa da girma. Moda 'yar karama.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

Waƙa (minti 3)

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

## Koyo

Gabatar da lissafin awon faɗi (minti 10)

| Awo | Malami | Ɗalibi |
|---|---|---|
| Faɗin ƙofa | ɗani _____ | ɗani _____ |

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi yadda ake auna abubuwa mabambanta ta amfani da abubuwan awo daban-daban, da ma hannunmu da ƙafafu!*
- Zana jadawali a kan allo sannan a yi bayani cewa za ku auna faɗin ƙofar aji da ɗanin hannu.
- Ku ƙirga ɗani nawa za a samu na faɗin ƙofar, sai a rubuta adadin a kan allo. Misali, idan ɗani uku aka samu, sai a rubuta "3" a kan allo.
- A sa wani ɗalibi shi ma ya auna adadin ɗanin da ake bukata a sami faɗin ƙofar. Rubuta ɗanin hannun a cikin jadawalin ƙarƙashin ɗalibi.
- A tambayi ɗalibai wani abun da za su iya auna tsayi da shi. (kamar lurar gwaji, kamun gaba, tsalle,  takun ƙafa, da sauransu.)

## Gwaji

Aiki mutum biyu: Auna faɗin abubuwa (minti 15)

- A ce wa ɗalibai za su yi aiki su bibbiyu. A sa ɗalibai su buɗe littafinsu Shafi na 60.
- Karanta wa ɗalibai umarnin da kuma tambayar farko su ji.
- A kewaya a duba abin da ɗalibai suke yi. A yayin kewayawar, a taimaka masu wajen awon kuma a tabbatar masu da abin da suke yi daidai. Idan da lokaci ku kammala aikin da ke shafi na gaba.

## Bayyanawa

Gaggauta auna fahimta (minti 5)

- A ce wa ɗalibai su ɗaga takardarsu sama su nuna abin da suka rubuta. A yaba masu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 60 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida. A ce wa ɗalibai su yi aiki da abokinsu ko wani ɗan uwa a gida a matsayin abokin aiki.

**Na. 139**

# Zango na 3, Mako na 4, Darasi na D

**Manufofi:** Ɗalibai su iya auna tsayi da faɗin abu ta amfani da sandar mitar gwaji.
**Kayan Aiki**: Sandar mitar gwaji da ta lura **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Mage doguwa. Kwalba gajera.
Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
Randa da girma. Moda 'yar karama.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

## Koyo

Gabatar da kayan awu na zamani (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Mun auna tsayi da faɗin abubuwa ta amfani da abubuwan awo mabambanta: hannayenmu, dantsenmu, yatsunmu. Amma kasancewar girmanmu ba ɗaya ba, awonmu sun bambanta. Wani lokaci, muna bukatar samun tsayayyen awo, don haka, sai mu yi amfani da sandar mitar gwaji ta zamani mu auna tsawo da santimita. Duk wanda ya yi amfani da sandar mitar gwaji (duk faɗin duniya) zai sami awon tsayi da faɗin abu daidai.*
- Ɗaga sandar mitar gwajin sama 'yan aji su gani. A tuna masu abin da jerin layukan da ke jikin sandar ke nufi (santimitoti) sai a ba su misali abubuwan da za ku iya aunawa da shi da kuma abin da za a iya aunawa ta santimita.
- **Ka/ki ce:** Bari mu gwada auna mita da santimitocin tsayin ɗaya daga cikin bencin aji.
- Gwada musu yadda za a yi awun dasandar mitar gwajin. Bayyana musu cewa idan akwai mitar gwajin da ba ta cika ba, za a iya gwajin ta ƙirga santimita sannan a mayar da su mita.
- Rubuta awon mita ta tsayin bencin da santimita a kan allo.
- A tambayi ɗalibai wani abun da za su iya auna tsayi da shi sai a sa wani ɗalibi ya je gaban aji ya auna tsayi ko faɗin da sandar mitar gwaji.

## Gwaji

Aiki ɗaiɗai ko bibbiyu: Auna abubuwa (minti 15)

- A ce wa ɗalibai za su yi aiki su bibbiyu. A sa ɗalibai buɗe littafinsu Shafi na 61.
- Karanta wa ɗalibai umarnin da kuma tambayar farko su ji.
- Bayyana wa ɗalibai cewa su auna tsayi da faɗin abubuwa da dama. Sai su rubuta awon a cikin littafin koyo.
- A kewaya a duba abin da ɗalibai suke yi. A yayin kewayawar, a taimaka musu wajen awon kuma a tabbatar masu da abin da suke yi daidai. Idan da lokaci ku kammala aikin da ke shafi na gaba.

## Bayyanawa

Gaggauta auna fahimta (minti 5)

- A ce wa ɗalibai su ɗaga takardarsu sama su nuna abin da suka rubuta. A yaba masu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 61 a cikin littafansu na aiki a matsayin aikin gida.

| Na. 140 | Zango na 3, Mako na 4, Darasi na E |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya bita da gwajin aikin da aka gabatar a makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masugwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

| |
|---|
| Ga girma ga nauyi ga tsayi x2<br>Mage doguwa. Kwalba gajera.<br>Ga girma ga nauyi ga tsayi x2<br>Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.<br>Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)<br>Randa da girma. Moda 'yar karama.<br>Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2) |

## Koyo

Bita da maimaitawa (minti 10)

- Zaɓi wani labari daga ayyukan makon da ake ganin kamar ɗalibai suna fama da shi. A sake maimaita koyar da shi ko kuma a koyar da shi ta wata hanyar daban.

## Gwaji

Aiki ɗaiɗai ko a cikin rukuni: Zane da rubutu (minti 15)

- Ba ɗalibai jingar za ta taimaka musu su gwada abin da aka yi masu bita a kai (misali, auna tsayi da faɗi ta hanyar zamani da gargajiya). Ɗalibai za su iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma cikin ƙananan ƙungiyoyi.
- Yayin da ɗalibai suka mayar da hankali kan yin aikin jingar, a taimaka wa ɗaliban da suke buƙatar matuƙar taimako.

## Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A ce wa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala yayin gwaji.

## Aikin Gida

A b ɗalibai aikin gida da za su yi bita da kuma nuna ƙwarewarsu.

| Na. 141 | Zango na 3, Mako na 5, Darasi na A |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai su iya auna abubuwa daban-daban ta amfani da ƙananan kayan gwaji na gargajiya.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masugwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Mage doguwa. Kwalba gajera.
Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
Randa da girma. Moda 'yar karama.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

**Koyo**

Gabatar da ƙaramin kayan awo na gargajiya (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu ci gaba da auna abubuwa, amma a wannan karo, da ƙanana kayan gwaji na gargajiya. Waɗannan sun haɗa da dabban ɗan yatsa da tsawon yatsa ko magogai.*

| Awu | Malami | Ɗalibi |
|---|---|---|
| Tsawon fensur | ɗani ____ | ɗani ____ |

- Zana jadawali a kan allo sai a bayyana wa ɗalibai cewa za su auna tsawon fensir ɗinsu ta amfani da babban ɗan yatsa.
- Auna fensir da babban ɗan yatsa, sai a rubuta a kan allo. Misali, idan babban ɗan yatsa uku aka samu, sai a rubuta "3" a kan allo.
- A sa wani ɗalibi ya auna fensir ɗin a ga adadin ɗani nawa za a samu. Rubuta awon ɗalibin cikin jadawalin ƙarƙashin ɗalibi.
- A tambayi ɗalibai su ambaci wani kayan gwaji na gargajiya da za su iya auna tsayi da shi.

**Gwaji**

Aiki mutum biyu: Auna abubuwa (minti 15)

- A ce wa ɗalibai za su yi aiki su bibbiyu. A sa ɗalibai buɗe littafinsu Shafi na 62.
- Karanta wa ɗalibai umarnin da kuma tambayar farko su ji. A ce wa ɗalibai su rubuta awon da ya zama daidai da kowane ɗalibi a littafin rubutunsu.
- A kewaya a duba abin da ɗalibai suke yi. A yayin kewayawar, a taimaka musu wajen awon kuma a tabbatar masu da abin da suke yi daidai. Idan da lokaci ku kammala aikin da ke shafi na gaba.

**Bayyanawa**

Gaggauta auna fahimta (minti 5)

- A ce wa ɗalibai su ɗaga takardarsu sama su nuna abin da suka rubuta. A yaba masu.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 62 a cikin littafansu na aiki a matsayin aikin gida. A ce wa ɗalibai su yi amfani da abokinsu ko wani ɗan uwa a gida a matsayin abokin aiki.

| Na. 142 | Zango na 3, Mako na 5, Darasi na B |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai su iya auna abubuwa ta amfani da sandar mitar gwaji da lura.
**Kayan Aiki**: Sandar mitar gwaji da lura/lurori **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)
- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)
- Ku ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Mage doguwa. Kwalba gajera.
Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
Randa da girma. Moda 'yar karama.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

**Koyo**

Awo da sandar mitar gwaji da kuma lura (minti 10)
- **Ka/ki ce:** *Mun auna tsayi da faɗin abubuwa da kayan awo da dama: hannayenmu, dantsenmu da ya yatsu. Amma saboda girmanmu ba ɗaya ba,awon dole su sha bamban. Wani lokaci, muna buƙatar samun awo daidai, don haka sai mu yi amfani da sandar mitar gwajin mita mu auna tsawo da kuma santimitoci. Duk wanda ya yi amfani da sandar mitar gwajin (duk faɗin duniya) zai sami awo daidai na tsayi da faɗin abin da ya auna.*
- Ɗaga sandar mitar gwajin sama a aji su gani. Tuna masu cewa jerin layukan da ke jikin sandar na nufin (santimitoci) sai kuma a ba su misalan abubuwan da za a iya aunawa da sandar mitar gwajin da abubuwan awona santimitoci.
- **Ka/ki ce:** *Bari mu gwada ɗaya daga cikin bencin mu san mita da santimitarsa.*
- Nuna yadda za a yi gwaji da sandar mitar gwajin . Yi bayani cewa yayin awo, idan tsayin ya gaza kai wa mita, sai a yi awon da santimita sai a ƙara kan mitocin da aka samu.
- Rubuta mita da santimitar bencin a kan allo.
- A tambayi ajin abin da suke son aunawa, sai a kira wani ɗalibi ya je gaban aji ya auna tsayi da faɗin abin da sandar mitar gwaji.

**Gwaji**

Aiki ɗaiɗai ko bibbiyu: Auna abubuwa (minti 15)
- A ce wa ɗalibai za su yi aiki su bibbiyu. A sa ɗalibai buɗe littafinsu Shafi na 63.
- Karanta wa ɗalibai umarnin da kuma tambayar farko su ji.
- Bayyana wa ɗalibai cewa su auna tsayi da faɗin abubuwa da dama. Sai su rubuta awon a cikin littafin koyo.
- A kewaya a duba abin da ɗalibai suke yi. A yayin kewayawar, a taimaka masu wajen awun kuma a tabbatar masu da abin da suke yi daidai. Idan da lokaci ku kammala aikin da ke shafi na gaba.

**Bayyanawa**

Gaggauta auna fahimta (minti 5)
- A ce wa ɗalibai su ɗaga takardarsu sama su nuna abin da suka rubuta. A yaba masu.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 63 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 143 | Zango na 3, Mako na 5, Darasi na C |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai su iya gano tsayin ɗaliban aji.

**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Gajere da dogo (minti 3)

- Kira ɗalibai biyu su je gaban aji su tsaya suna ba juna baya.
- **Ka/ki ce:** *Ɗalibin da ya fi tsayi shi ne dogo. Ɗalibin da yake da ƙarancin tsayi shi ne gajere.*

## Koyo

Gabatar da awon tsayi (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi abin da ake nufi da tsayi. Tsayi daidai yake da tsawo. Tsawo shi ne tazarar da ke tsakanin wuri da wuri a shimfiɗe ko a tsaye.*
- Zana jadawali a kan allo sai a faɗawa wa ɗalibai cewa za su gwada auna tsayin abu.

| Tsayi | |
|---|---|
| Ɗalibi na 1 | Ɗalibi na 2 |
| kamu _____ | kamu _____ |

- Kira ɗalibi/ɗaliba ya/ta je gaban aji ya/ta jingina bayansa/ta a jikin allo. Yi amfani da alli, a zana layi a daidai inda kan ɗalibin/ɗalibar ya kai a kan allo.
- A sa ɗalibai yadda za su auna tsayin abokan karatunsu (Misali, za su iya auna tsayin da faɗin hannu, tep na awo, da taƙi ko kamun hannu).
- Kira ɗalibi ɗaya ya je gaban aji ya yi amfani da hannunsu ya auna tsayin ɗaya ɗalibin. Zai fara daga ƙasa zuwa sama har ya kai inda aka ja layin a kan allo. Rubuta awon cikin jadawalin ƙarƙashin ɗalibi na 1.
- Sa wani ɗalibi ya yi awon. Rubuta awon cikin jadawalin ƙarƙashin ɗalibi na 2 a kan allo.
- Umurci ɗalibai su gano wane ɗalibine ya fi tsawo da kuma gajarta.

## Gwaji

Aikin cikin ƙaramin rukuni : Awon tsayi (minti 15)

- A sa ɗaliabai su zazzauna a ƙananan rukunoni 3-5. Zaɓi jagora a kowane rukuni ya taimaka wajen raba littafin ɗalibai. A sa ɗalibai su buɗe littafinsu Shafi na 64.
- Yi wa ɗalibai bayani cewa za su auna juna don sanin tsayinsu. Kira ɗalibin farko ya tsaya jikin allo. Wani ɗalibin ya auna tsayin ɗalibin farkon da hannu, yana farawa daga ƙasa zuwa inda tsayinsa ya kai a jikin allon. Sai su rubuta awon tsayin da hannun, a littafin rubutunsu.
- A yi ta yi har sai an auna kowane ɗalibi.
- A kewaya a lura da abin da ɗalibai ke yi sannan a taimaka masu inda suke da bukata. Tabbata kowane ɗalibi ya auna ɗan'uwansa ɗalibi shi ma kuma an auna shi.

## Bayyanawa

Bayyana kyawawan misalai (minti 5)

- A sa ɗalibai su bayyana wa juna bayanan da suka tattara na rukunin su.

## Aikin gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 64 a cikin littafansu na aiki a matsayin aikin gida.Su ɗauki awan tsayin mutum biyu a gidansu.

| Na. 144 | Zango na 3, Mako na 5, Darasi na D |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai su iya jera abubuwa dangane da tsawo da faɗi da kuma tsayi.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masugwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Ku yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

> Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
> Mage doguwa. Kwalba gajera.
> Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
> Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
> Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
> Randa da girma. Moda 'yar karama.
> Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

## Koyo

Gabatar da shirya abubuwa dangane  da tsawo da kuma faɗi (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau, za mu shirya kanmu dangane da tsayi.*
- Kira wasu ɗalibai uku su je gaban aji su tsaya gefe da gefe da juna.
- A sa sauran ɗalibai su faɗi mafi  tsawon cikinsu da mafi gajarta. A sa ɗaliban nan su jeru daga mafi tsawo zuwa mafi gajarta.
- Kira wani ɗalibi zuwa gaban allo ya ja layin daidai inda tsayin kowane uku daga ɗaliban nan ya kai, ya kuma kiyaye da  jerantuwarsu daga mafi tsawo zuwa mafi gajarta.
- Ci gaba da kiran ɗaliban ɗaya bayan ɗaya suna shiga layi har su kai 20 (ko fiye!) a jere daga dogo zuwa mafi gajarta.
- **Ka/ki ce:** *Wane ɗalibi ne mafi tsawo? Wane ɗalibi ne mafi gajarta?*

## Gwaji

Aiki ɗaidai ko bibbiyu: Gane tsayi da mita (minti 15)

- A sa ɗalibi 1 ko 2 su taimaka wajen rarraba wa ɗalibai littafinsu. A sa ɗaliban su buɗe littafinsu Shafi na 65.
- Karanta wa ɗaliban umarnin su ji.
- **Ka/ki ce:** *Rubuta sunayen ɗaliban dangane da tsayinsu daga mafi tsawo zuwa mafi gajarta.*
- Ɗalibai kan iya duba aikin junansu don ganin ko sun yi daidai.
- A zagaya a duba aikin da ɗalibai ke yi. A yayin zagayawar, a tambaye su yadda suka samo amsarsu, sai a duba ko sun yi daidai.

## Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- **Ka/ki ce:** *Ta* yaya shirya bayanai a jere ke taimaka wa fahimtarku*?*
- Kira wasu ɗaliban su bayyana wa aji amsoshinsu.

## Aikin gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 65 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 145 | Zango na 3, Mako na 5, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai su iya bita da gwajin aikin da aka gabatar a makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Ku ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Mage doguwa. Kwalba gajera.
Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
Randa da girma. Moda 'yar karama.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

### Koyo

Bita da maimai (minti 10)

- Zaɓi wani labari daga ayyukan mako da ake ganin kamar ɗalibai suna fama da shi. A sake maimaita koyar da shi ko kuma a koyar da shi ta wata hanyar daban.

### Gwaji

Aiki ɗaiɗai ko a cikin rukuni: Zane da rubutu (minti 15)

- Ba ɗalibai jingar da za ta taimaka masu su gwada abin da aka yi musu bita a kai (misali, jera abubuwa dangane da tsawo ko faɗi ko kuma tsayinsu). Ɗalibai za su iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma cikin ƙananan rukunai.
- Yayin da ɗalibai suka mayar da hankali kan yin aikin jingar, a taimaka wa ɗaliban da suke buƙatar matuƙar taimako.

### Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A ce wa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala yayin gwaji.

### Aikin Gida

A ba ɗalibai aikin gida da za su yi bita da kuma nuna ƙwarewarsu.

| Na. 146 | Zango na 3, Mako na 6, Darasi na A |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai su iya rubuta gajeren gwajin lissafi.
**Kayan Aiki:**

**JARRABAWAR GWAJI**

A gabatar masu da gwaji ɗaya bayan ɗayasai a rubuta sakamakon nasu a littafin rubuta sakamakon jarrabawa. Idan da buƙata, a nemi taimakon shugaban makarantar ko mambobin kwamitin kula da makarantu (SBMC), ko wasu malamai domin taimakawa gudanar da gwajin.

A samar wa ɗalibai wani aikin  a yayin da suke jiran rubuta gwajin. Misali, ɗalibai na iya gwada yin lissafin tarawa ko ɗebewa na kuɗi ko auna faɗin abubuwa ko tsawonsu a kwance ko tsaye.

| Jaha: | | Karamar hukuma: | | Makaranta: | | Wata: | | Shekara: | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|

| Lamba | Sunan Ɗalibi | Jinsi | Shekaru | Buƙata ta musamman (Eh/A'a) | Rubanya | Tara Naira | Tsawo | Awoj | Jimillar maki |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| | | | | | /5 | /5 | /2 | /3 | / 15 |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |

## Darasin Lissafi Aji 2, Zango na 3, Mako na 6 – Jarrabawar tsakiyar Zango

**Tara waɗannan lambobin.** (A bayar da maki biyar idan an amsa daidai)

**10 + 10 + 10 + 10 + 10 = _____**

**Tara waɗannan takardun kuɗi, a ba da amsa**. (A bayar da maki biyar idan an amsa daidai)





**+**




**=**


**Wane ne ya fi tsawo?** (A bayar da maki biyu idan an amsa daidai)





**Adadin senti mita nawa ne tsawon wannan hula.** (A bayar da maki uku idan an amsa daidai)





| Na. 147 | Zango na 3, Mako na 6, Darasi na B |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai su iya yin lissafin tarawa da ɗebewa ta amfani da Naira.
**Kayan Aiki:** Takardun kuɗi na wasa **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

> Ina ‘yan yara, ina ‘yan yara, ina ‘yan yara yaran yanzu.
> Mu ne yara mu ne yara mu ne yara yaran yanzu.
> Ina ‘yan yara manyan gobe.Mu ne yara manyan gobe.
> Mu koyi karatu ‘yan yara. Don muzan manyan gobe.

Waƙa (minti 3)

- Ku yi ta maimaita rera waƙar tare da ɗalibai na wani lokaci.
- Kira wani ɗalibi waje ya rera wa aji waƙar.

### Koyo

Lissafin tarawa da Naira (minti 8)

- **Ka/ki ce:** *Yau, za mu gwada yin lissafin tarawa da ɗebewa ta amfani da takardun kuɗi na wasa.*
- Kira wani ɗalibi zuwa gaban allo sai a ba shi ₦100 da ₦50 da kuma ₦500.
- **Ka/ki ce:** *Kuɗi nawa nake da su gaba ɗaya?*
- A sa ɗalibi ya rubuta fasalin lissafin tarawar da ke kan allo.
- A tabbata fasalin lissafin 100 + 50 + 200 = ___ na rubuce sai kuma a amsa tare da ɗalibai kowa na ji.

Lissafin ɗebewa da Naira (minti 7)

- **Ka/ki ce:** *Za mu iya kuma gwaji yin ɗebewa da takardun kuɗi.*
- Kira wani ɗalibi/ɗaliba zuwa gaban allo a ba shi ₦50 da ₦20.
- A sa ɗalibi/ɗaliba ya rubuta fasalin lissafin ɗebewar da ke kan allo.
- A tabbata fasalin lissafin 100 – 50 = ___ na rubuce kuma kuma a amsa tare da ɗalibai lokaci guda kowa na ji.

### Gwaji

Gwajin cikin ƙaramar rukuni : lissafin tarawa da ɗebewa ta amfani da takardun kuɗi (minti 10)

- A sa ɗaliabai su zazzauna a ƙananan rukunai. A zaɓi ɗalibi 1 daga kowane rukuni ya raba wa ‘yan rukuninsa kudin wasa. A sa ɗalibai buɗe littafinsu Shafi na 66.
- A faɗa wa ɗalibai su yi aiki tare kuma su yi amfani da kuɗin wasan wajen amsa tambayoyin da ke cikin littafinsu.
- A zagaya a duba aikin da ɗalibai ke yi. A yayin zagayawar, a tambaye su yadda suka samo amsarsu, sai a duba ko sun yi daidai.

### Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- Umurci ɗalibai su kalli abokan zamansu su bayyana abinda sukayi a rukunansu.

### Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 66 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

**Na. 148**

# Zango na 3, Mako na 6, Darasi na C

**Manufofi:** Ɗalibai su iya amfani da hanyar ruɓanya tarawa wajen yin lissafin sau na 2-2 da 5-5 da kuma 10-10.
**Kayan Aiki:** Abubuwan ƙirge (wake ko tsakuwa), Zanen layin lamba **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Ku yi ta maimaita rera waƙar tare da ɗalibai na wani lokaci.
- Kira wani ɗalibi waje ya rera wa aji waƙar.

Biyu sau ɗaya biyu / Biyu sau biyu hudu
Biyu sau 3 Shidda / Biyu Sau 4 Takwas
Biyu sau 5 Goma / Biyu sau 6 goma sha biyu
Biyu sau bakwai goma sha huɗu /
Biyu sau Takwas goma sha shida
Biyu sau Tara goma sha takwas /
Biyu sau Goma Ashirin

## Koyo

Bita kan lissafin sau ta hanyar ruɓanya tarawa (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu ci gaaba dayin lissafin sau ta hanyar ruɓanya tarawa.*
- Kira ɗalibai 5 zuwa gaban allo. A tambayi ɗalibai nawa ne a nan. sannan, a kira wasu biyar su je gaban allo sai a ce masu su tsaya su ma guri guda daban da na farko.
- **Ka/ki ce:** *Muna da ɗalibai 5 sannan muka ƙara wasu gungun 5. Yanzu muna da ɗalibai nawa?*
- Kirga adadin ɗaliban da ƙarfi tare da ɗaliban ajin. Kira wasu ɗalibai guda 5 zuwa gaba.
- **Ka/ki ce:** *Mun ƙara wasu ɗalibai 5. Muna da ɗalibai nawa yanzu?*
- Rubuta 5+5+5 = 15 a kan allo.
- **Ka/ki ce:** 5 *a tara da 5 a kuma tara da 5 daidai yake da 15.* Mun tara gungun 5 uku*. Za mu iya rubuta fasalin lissafin da ruɓanya tarawa, ko kuma mu yi amfani da alamar sau, ko kuma zamu iya rubutashi ta amfani da alamar sau.*
- Rubuta 5 x 3 = 15 a kan allo.
- Idan da lokaci, a maimaita da wasu ɗalibai da kuma rukunai 2 da 10.

## Gwaji

Aiki ɗaiɗai ko bibbiyu: Lissafin sau da 2-2 da 5-5 da kuma 10-10 (minti 15)

- A sa ɗalibai buɗe littafinsu Shafi na 67.
- Karanta wa ɗalibai umarnin, da kuma tambayar farko su ji. A sa ɗalibai su amsa tambaya a littafin rubutunsu. Za su iya nuna wa juna amsarsu su don sanin ko sun yi daidai.
- A zagaya a duba aikin da ɗalibai ke yi. A yayin zagayawar, a tambaye su yadda suka samo amsarsu, sai a duba ko sun yi daidai.
- Idan da lokaci, ku kammala aikin da ke shafi na gaba.

## Bayyanawa

Gaggauta auna fahimta (minti 5)

- A ce wa ɗalibai su ɗaga littafansu sama su nuna abin da suka rubuta. A yaba masu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su kammala sauran aikin dake Shafi na 67 a cikin littafansu na rubutu a matsayin aikin gida.

| Na. 149 | Zango na 3, Mako na 6, Darasi na D |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai su iya auna tsawo da tsayi da faɗin abubuwa da ke cikin aji a gargajiyance.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 3)

- Ku ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Mage doguwa. Kwalba gajera.
Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
Randa da girma. Moda 'yar karama.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

## Koyo

Gabatar da lissafin awun faɗi(minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu auna tsayi da faɗin abubuwa da kayan awo mabambanta.*
- Zana jadawali a kan allo sai a bayyana wa ɗalibai cewa za su auna faɗin littafin aiki da ɗanin yatsu.

| Awo | Malami | Ɗalibi |
|---|---|---|
| Faɗin littafi | yatsa ____ | yatsa ____ |

- Kirga adadin ɗanin yatsan da zai kai a auna faɗin littafin, sai ka rubuta a kan allo. Misali, idan ɗani uku ka samu, sai ka rubuta "3" a kan allo.
- A sa wani ɗalibi/ɗaliba ya/ta ƙirga adadin ɗanin yatsa da ake buƙata wajen awon faɗin littafin rubutu. Rubuta awon a jadawali ƙarƙashin ɗalibi.
- A tambayi ɗalibai abin da za su iya amfani da shi su auna tsawo ko faɗin abu (kamar lurar awo, gaba, tsalle, taku, dasaurансu.)

## Gwaji

Aiki mutum biyu: Auna faɗin abubuwa (minti 15)

- A ce wa ɗalibai za su yi aiki su bibbiyu. A sa ɗalibai su buɗe littafinsu Shafi na 68.
- Karanta wa ɗalibai umarnin da kuma tambayar farko su ji.
- Faɗa wa ɗalibai cewa su auna tsayin litattafinsu na rubutu ta amafani da fensur. Su rubuta awun kowanensu a littafin rubutunsu.
- A zagaya a duba abin da ɗalibai suke yi. A yayin zagayawar, a taimaka masu wajen awon kuma a tabbatar masu da abin da suka yi daidai. Idan da lokaci ku kammala aikin da ke shafi na gaba.

## Bayyanawa

Gaggauta auna fahimta (minti 5)

- A ce wa ɗalibai su ɗaga littafinsu sama su nuna abin da suka rubuta. A yaba musu.

## Aikin Gida

A ce wa ɗalibai su kammala sauran aikin da ke Shafi na 68 cikin littafinsu a matsayin aikin gida. A ce wa ɗalibai su yi aiki da abokinsu ko wani ɗan uwa a gida a matsayin abokin aiki.

| Na. 150 | Zango na 3, Mako na 6, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai su iya auna abubuwa ta amfani da sandar mitar gwaji da lura.
**Kayan Aiki**: Sandar mitar gwaji da lura/lurori **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Mage doguwa. Kwalba gajera.
Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
Randa da girma. Moda 'yar karama.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

Waƙa (minti 3)

- Ku ta rera waƙar tare da ɗalibai.

**Koyo**

Awo da sandar mitar gwaji da kuma lura (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Mun auna tsayi da faɗin abubuwa da kayan awo da dama: hannayenmu, dantsenmu da yatsu. Amma saboda girmanmu ba ɗaya ba,awon dole su sha bamban. Wani lokaci, muna buƙatar samun awo daidai, don haka sai mu yi amfani da sandar mitar gwaji mu auna tsawo da santimitoci. Duk wanda ya yi amfani da sandar mitar gwajin (duk faɗin duniya) zai sami awo daidai na tsayi da faɗin abin da ya auna.*
- Ɗaga sandar mitar gwajin sama a aji su gani. Tuna musu cewa jerin layukan da ke jikin sandar na nufin (santimitoci) sai kuma a ba su misalai abin da za a iya aunawa da mita da kuma wanda za a auna da santimita.
- **Ka/ki ce:** *Bari mu gwada auan tsayin wani ɗalibi da mita da kuma santimita.*
- Nuna yadda za a yi gwaji da sandar mitar gwajin. Yi bayani cewa yayin awo, idan tsayin ya gaza kai wa mita , sai a yi awun da santimita sai a ƙara kan mitocin da aka samu.
- Kira wani ɗalibi ya je gaban allo ya nuna yadda zai auna tsayinsa da mita ko santimita. Rubuta tsayin nasa a kan allo.
- Idan da lokaci, maimaita da wasu ɗaliban.

**Gwaji**

Aikin cikin ƙaramin rukuni : Awun tsayin abubuwa (minti 15)

- A sa ɗaliabai su zauna a ƙananan rukunoni. A sami wani ɗalibi a kowane rukuni ya taimaka wajen raba wa kowane rukuni sandar mitar gwaji (ko wani abu mai tsawonsa).
- Yi wa ɗalibai bayani cewa su nemo abu ɗaya a ajin da ya fi tsawo ko ya fi faɗi ko kuma yake da tsawon da ya ɗara mita ɗaya. Su zana a cikin littafin rubutunsu.
- Sannan, su nemo abun da ya fi gajarta, tsukakke ko kuma mafi ƙanƙanta da ya gaza mita ɗaya. Su zana hoton abun a cikin littafin rubutunsu.
- A kewaya a lura da abin da ɗalibai ke yi sannan a taimaka masu.

**Bayyanawa**

Bayyana kyawawan misalai (minti 5)

- A sa ɗalibai su tattauna da wasu 'yan rukuninsu akan abin da suka iya samowa. Su tattauna kan abubuwan da suka fi girma da waɗanda suka fi ƙanƙanta.

**Aikin Gida**

A ce wa ɗalibai su auna tsawon wani abu a gidansu. Su rubuta awun nasu a littafin rubutunsu.

| Na. 151 | Zango na 3, Mako na 7, Darasi na A |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya rarrabewa sannan su shafa kala a siffofin da suke kama da juna.
**Kayan Aiki:** Siffofi daban-daban da aka yi da takarda. **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)


- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.
- Nemi ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta ya rera wa 'yan ajin waƙar.

> Zan iya rarrabewa, zan iya rarrabewa.
> Lalle zan iya. Lalle zan iya.
> Za ku iya rarrabe wake? Za ku iya rarrabe wake?
> Lalle zan iya. Lalle zan iya.

## Koyo

Gabatarwa a kan siffofi masu kama da juna (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi siffofi masu kama da juna. Siffofi biyu za su iya kama da juna idan suna da kamanni iri ɗaya. Misali za su iya zama ɗaya kala ko ta sifa ko kuma ta girma.*
- Zana siffofin a kan allo sannan a ba kowane lamba daga 1 – 8.




- Nuna kowace sifa sannan a umurci ɗalibai su faɗi sunanta a bayyane tare da kai/ke.
- **Ka/ki ce:** *Tun da yanzu mun ambaci sunayen dukkan siffofin, yanzu sai mu danganasu da waɗanda suka yi kama da juna. Waɗanne siffofi ne suke iri ɗaya?*
- Umurci ɗalibai ɗaya bayan ɗaya zuwa gaban allo su riƙa zagaye siffofi biyu da suke kama da juna.

## Gwaji

Wasan dukkan aji: Siffofi masu kama da juna? (minti 15)

- Zana da'ira da siffar akwati a takardu daban-daban. Rataye kowace takarda wurare daban-daban masu kallon juna a cikin aji.
- Yi bayanin cewa za ka/ki faɗi wani abu wanda ɗalibai suke yawan gani a rayuwarsu ta yau da kullum. Yayin da ka/kika ambaci sunan abin, sai ɗalibai su yi sauri su je wurin sifar da take kama da abin da aka ambata. Misali, idan aka ce "Rana", ɗalibai sai su tafi ɓangaren ajin da yake da da'ira. Saboda siffar rana ta yi kama da da'ira.
- Bayar da waɗannan misalan: *marfin kwalba da tayar keke da ƙofa da littafi da rana, da filin ƙwallon ƙafa da kuma tsabar kuɗi.*
- Idan da sauran lokaci, a maimaita da wasu abubuwan.

## Bayyanawa

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- Zana siffofi daban-daban guda uku a kan allo. A sa ɗalibai su gano waɗanda suka yi kama da juna da kuma waɗanda suka bambanta.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su zana wani abu da suke gani a rayuwarsu ta yau da kullum wanda ya yi kama da siffar akwati.

## Na. 152 Zango na 3, Mako na 7, Darasi na B

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya rarrabe manya da ƙanana da kuma abubuwa masu girma ɗaya
**Kayan Aiki:** Abubuwa masu bambancin girma da siffa (ƙwallo da tsakuwoyi da itatuwa da makamantansu.) **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)


- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masugwiwa.

Wasan motsa jiki (minti 3)

- A sa ɗalibai su kwaikwayi motsin jikin da za ka/ki yi yanzu.
- Da farko, yi ƙaramar da'ira da yatsu sannan kuma sai a yi babbar da'ira da hannu a kan iska. A ce "ƙaramar da'ira", "babbar da'ira" a kowane motsi da aka yi. Daga nan sai a sa ɗalibai ma su aikata bayan ka/kin yi.
- A sa dukkan ajin su tashi domin a yi motsin tare.

### Koyo

Gabatar da abubuwa masu mabambantan girma (minti 10)



- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi wani abu a kan ma fi girma da ma fi ƙanƙanta da kuma masu girma ɗaya. Wata hanyar da za mu iya bi wajen jera abubuwa ita ce ta girma-girma.*
- Zana wani abu mai mabambantan girma a kan allo (Misali: buhunhuna). A yi wa ɗalibai bayanin cewa, ɗaya daga cikin kayan ƙarami ne ɗaya matsakaici ne ɗaya kuma babba ne.
- Ɗaga itatuwa guda uku a gaban aji: ɗaya ƙarami ne, ɗaya matsakaici ne, sannan ɗaya kuma babba ne. A sa ɗalibai su jera waɗannan itatuwan dangane da girmansu.
- A sa ɗalibai su duba wanne ne daga cikin itatuwan ya fi kowane girma a cikinsu sannan da wanda ya fi kowane ƙanƙanta.
- A sa ɗaya daga cikin ɗaliban ya/ta fito gaban aji su duba ko za su sami itatuwa biyu waɗanda girmansu ɗaya ne.
- Maimaita da wasu abubuwa da suke da kamanci da kuma waɗanda suke da bambanci.
- A sa ɗalibai su fito gaban aji su zaɓi abubuwa masu mabambantan girma. Abubuwan za su iya zama iri ɗaya ko masu bambanci. A ce su ɗaga abubuwan da suka zaɓa sama sannan su faɗi manya ne ko ƙanana ko kuma girmansu ɗaya ne da sauran. Daga nan sai a sa ɗaliban su jera su dangane da girmansu.

### Gwaji

Aikin ƙananan rukunoni: Rarrabewa dangane da girma (minti 15)

- A sa ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunoni. A zaɓi shugaba daga kowane rukuni da zai taimaka wajen rabon kaya iri-iri wa 'yan rukuninsu.
- A sa ɗaliban kowane rukuni su riƙa jujjuyawa ɗaya bayan ɗaya, wajen jera abubuwan nan guda uku dangane da girmansu daga ƙarami zuwa babba. Ana so su ware wanne ne "Ma fi ƙanƙanta" sannan kuma wanne ne "Ma fi girma".
- A tambayi ɗalibai ko akwai abubuwa guda biyu ko fiye da haka da girmansu ya zama ɗaya.
- Zagaya domin lura da ɗalibai da kuma bayar da tallafi.

### Bayyanawa

Nuna wa abokin aiki (minti 5)

- Ɗalibai za su tattauna da abokan aikinsu abubuwan da suka yi a rukunoninsu.

### Aikin Gida

A sa ɗalibai su nemo abubuwa uku masu kama da juna amma masu bambancin girma sannan su zana su a cikin litattafansu na rubutu a gida.

| Na. 153 | Zango na 3, Mako na 7, Darasi na C |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su jera abubuwa dangane da siffar su.
**Kayan Aiki:** Fasali daban-daban na takarda **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.


Waƙa (minti 2)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Zan iya rarrabewa, zan iya rarrabewa. Lalle zan iya. Lalle zan iya.
Za ku iya rarrabe wake?
Za ku iya rarrabe wake?
Lalle zan iya. Lalle zan iya.

**Koyo**

Jera abubuwa dangane da siffar su (minti 10)



- **Ka/ki ce:** *Yau za mu rarrabe abubuwa dangane da siffar su.*
- Baje kolin fasali daban-daban masu fuska biyu waɗanda suke da kusurwa-kusurwa, irin su siffar akwati, da siffar gidan dara da kuma kusurwa uku, da kuma siffofi da basu da kusurwa irin su da'ira da siffar ƙwai.
- **Ka/ki ce:** *Za mu ware siffofi masu fuska biyu, da suke da wani abu iri ɗaya misalai masu kusurwa ko kuma marasa kusurwa.*
- A sa ɗalibai biyu ko uku su fito gaban aji su ware waɗannan siffofin, dangane da kamanninsu. A ba su ƙwarin guiwa su riƙa ambaton kamannin ta hanyar tambayar su me ya sa aka saka wannan a nan? Yana da kusurwa ne? Fuskoki nawa yake da su? Gefe nawa yake da su?
- A sa wasu ɗaliban kuma daban su fito gaban aji su sake yin irin haka.

**Gwaji**

Aiki a cikin ƙananan rukunai: Ware abubuwa dangane da siffarsu (minti 15)

- A zagaya ana duba ɗalibai. A yayin zagayawar, a tabbata ko sunyi daidai sannan a taimaka masu idan da bukatar hakan.
- A sa ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunai. A ba kowane rukuni tarin abubuwa masu siffofi daban-daban da aka yi da takarda. A yi musu bayanin cewa za su yi aiki cikin rukunai domin jera abubuwan dangane da siffofinsu.
- A ba su abubuwa daban-daban, sannan a ƙyalesu da tunanin yadda za a jera su dangane da siffarsu. A faɗi masu su yi bayanin ƙa'idar da za su yi amfani da ita wajen warewa. Misali mene ne yake ɗaya a tsakanin abubuwan?
- Zagaya domin lura da ɗalibai. Yayin da ake zagayawa, a tabbatar masu ko abin da suke yi daidai ne, sannan kuma a bayar da tallafi idan buƙatar hakan ta taso.

**Bayyanawa**

Bayyana kyawawan misalai (minti 5)

- Zaɓi shugaba a kowane rukuni wanda zai faɗa wa sauran 'yan ajin yadda suka ware abubuwansu.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai su yi siffofi daban-daban ta hanyar yanka takardu ko katan-katan ɗin da babu komai a ciki.

**Na. 154** 

# Zango na 3, Mako na 7, Darasi na D

**Manufa:** Ɗalibai za su jera abubuwa dangane da girmansu.
**Kayan Aiki:** Abubuwa masu girma daban-daban (itatuwa ko tsakuwoyi ko ganyayyaki da sauransu) **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)

- A yi ta rera waƙar tare da ɗalibai.

Zan iya rarrabewa, zan iya rarrabewa. Lalle zan iya. Lalle zan iya.
Za ku iya rarrabe wake?
Za ku iya rarrabe wake?
Lalle zan iya. Lalle zan iya.

## Koyo

Jera abubuwa dangane da girmansu (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau, za mu jera abubuwa dangane da girmansu.*
- Baje kolin abubuwa daban-daban da aka bayar, (itatuwa ko abubuwa marasa komai a ciki ko tsakuwoyi da murafen kwalba)
- **Ka/ki ce:** Za mu jera abubuwa dangane da girmansu.
- A sa ɗalibai biyu ko uku su fito gaban aji su ware waɗannan abubuwan, dangane da girmansu. A ba su ƙwarin guiwa su riƙa ambaton kamannin ta wajen tambayar su me ya sa aka saka wannan a nan?
- Gayyaci wasu ɗaliban kuma daban su fito gaban aji su sake yin irin haka.

## Gwaji

Aiki a ɗaiɗaiku: Ware abubuwa dangane da girmansu (minti 15)

- A tura dukkan ɗalibai wajen aji a ce su nemo abubuwa daban-daban (murafan kwalba ko itatuwa ko akwatuna ko kuma mazubai da babu komai a ciki).
- A sa ɗalibai su zauna cikin ƙananan rukunai.
- A sa su jera kayan dangane da girmansu. A ce su yi bayanin ƙa'idar da suka bi wajen warewar: misali mene ne bambanci a tsakanin waɗannan abubuwa? (Wasu suna da girma, wasu kuma ƙanana ne)
- Zagaya domin lura da ɗalibai. Yayin da ake zagayawa, a tabbatar masu ko abin da suke yi daidai ne, sannan kuma a bayar da tallafi idan buƙatar hakan ta taso.

## Bayyanawa

Bayyanawa a dukkan aji (minti 5)

- Zaɓi shugaba a kowane rukuni domin gabatar wa 'yan aji yadda suka jera abubuwansu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su rubuta abubuwa guda biyu manya da za a iya samu a gidansu.

| Na. 155 | Zango na 3, Mako na 7, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za suyi bita da gwajin aikin da aka gabatar a makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)

- Ku rera waƙar tare da ɗalibai.

> Zan iya rarrabewa, zan iya rarrabewa. Lalle zan iya. Lalle zan iya.
> Za ku iya rarrabe wake?
> Za ku iya rarrabe wake?
> Lalle zan iya. Lalle zan iya.

## Koyo

Bita da maimaitawa (minti 10)

- Zaɓi wani labari daga ayyukan mako da ake ganin kamar ɗalibai suna fama da shi. A sake maimaita koyar da shi ko kuma a koyar da shi ta wata hanyar daban.

## Gwaji

Aiki a ɗaiɗaiku ko cikin ƙungiyoyi: Tarawa da ɗebewa da Naira (minti 15)

- A ba ɗalibai wani aiki wanda zai taimaka masu gwajin abin da ake bita a kansa (Misali, rarrabe abubuwa dangane da sifarsu ko girmansu ko kuma kalarsu). Ɗalibai za su iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma cikin ƙungiyoyi.
- Yayin da ɗalibai suke mayar da hankalinsu a kan aikinsu, a samar da wani taimako ga waɗanda suka fi buƙatarsa.

## Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna ayyukan da suka kammala a lokacin gwaji.

## Aikin Gida

A ba ɗalibai aikin gida don bita da gwajin abin da suka koya.

| Na. 156 | Zango na 3, Mako na 8, Darasi na A |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su auna girman mazubi sannan a danganta abubuwa ta hanyar amfani da "Ya fi" da "bai kai ba" da "mafi yawa" da "mafi ƙaranci".
**Kayan Aiki:** Mazubi mai girma daban-daban, bokitin ruwa ko yashi da kofi **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)

- Ku rera waƙar tare da ɗalibai.

> Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
> Mage doguwa. Kwalba gajera.
> Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
> Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
> Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
> Randa da girma. Moda 'yar karama.
> Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

## Koyo

Gabatarwa ga girman mazubi (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi wani abu a kan girman mazubi. Girman mazubi ya danganci yawan ruwa ko wasu kaya da mazubi zai iya ɗauka.*
- A sa ɗalibai biyu su fito gaban aji. A ba kowane ɗalibi mazubai guda biyu masu bambancin girma (misali, jarkar zuba fetur da kuma kwalbar ruwa) sannan a ce su nuna wa 'yan aji. A tambayi ɗaliban me ake yi da su, sannan a tattauna a kan abin da za su iya ɗauka.
- A ɗora mazuban a kan teburi sannan a ce ɗalibai su cika kowane da ruwa ko yashi ta hanyar amfani da ƙaramin kofi. A ce ɗaliban su riƙa ƙirga kofi nawa ne zai cika kowane mazubi.
- **Ka/ki ce:** *Jarkar fetur ta fi cin ruwa mai yawa. Kwalbar ruwa kuma ba ta cin ruwa da yawa.*
- A sa ɗaliban da suke gaba su ɗaga mazubansu sannan su jagoranci 'yan ajin wajen "faɗin ma fi yawa" da kuma "Ma fi ƙaranci" da ƙarfi yayin da suke ɗaga mazuban sama.
- Maimaita aikin cika mazuban, misali ƙaramin kwano da ruwa. A yi bayanin cewa yayin da ake da mazubai guda uku ko fiye, sai a bayyana wanda ya fi kowane girma a matsayin "Wanda yake ɗauke da ma fi yawan ruwa". Sannan shi kuma wanda ya fi kowane ƙanƙanta, a bayyana shi a matsayin "Wanda ya fi kowane ƙarancin ruwa".

## Gwaji

Aikin ƙananan rukunai: Danganta girman mazubi (minti 15)

- A sa ɗalibai su fita wajen aji sannan su zauna a cikin ƙananan rukunai. A zaɓi shugaba daga kowane rukuni don taimakawa wajen raba mazubai guda uku, da bokitin ruwa da kuma kofi ga 'yan rukuninsu.
- A sa ɗalibai su tattauna da junansu kan wane mazubi ne a ganinsu zai ɗauki ruwa ma fi yawa.
- A sa ɗalibai su ƙidaya yawan kofin da zai cika kowane mazubi.
- Zagaya domin lura da ɗalibai lokacin da suke cika mazuban. Yayin zagayawa, a riƙa tambayarsu kan wane mazubi ne ya fi yawan ruwa da kuma wanda ya fi ƙarancin ruwa. A tabbatar masu ko abin da suke yi daidai ne.

## Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A faɗa wa dukkan rukunai su sami 'yan wani rukuni da ke kusa da su ba su labarin mazubansu. Su nuna wanda ya fi ɗiban ruwa da kuma wanda ya fi ƙarancin ruwa.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su zana mazubai guda uku masu mabambantan girma a cikin litattafansu na rubutu.

| Na. 157 | Zango na 3, Mako na 8, Darasi na B |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su auna nauyi sannan su danganta nauyin abubuwa daban-daban.
**Kayan Aiki:** Abubuwa masu nauyi daban-daban (duwatsu da ganyayyaki da fensura da kuma litattafan karatu) **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma a ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)

- Ku rera waƙar tare da ɗalibai.
- Nemi ɗaya daga cikin ɗalibai ya/ta fito gaban aji domin rera waƙar ga ɗalibai.

Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Mage doguwa. Kwalba gajera.
Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
Randa da girma. Moda 'yar karama.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

## Koyo

Gabatarwa a kan nauyi (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi wani abu a kan nauyi. Wannan yana magana a kan tsananin nauyi ko rashinsa da abu yake da shi. Wannan yana da bambanci da mazubi, saboda shi mazubi yana awo ne na yawan abin da mazubin zai iya ɗauka.*
- A umurci ɗalibai biyu su zo gaban aji. A ba kowane ɗalibi wani abu masu nauyi daban daban (misali, dutse ko ganye) a umurcesu su nunasu ga 'yan aji.
- A tambayi ɗaliban ko nauyin waɗannan abubuwan ɗaya ne.
- **Ka/ki ce:** *Abin da ya fi nauyi shi ne mai nauyi. Abin da ya fi ƙarancin nauyi kuma shi ne mara nauyi.*
- A sa ɗaliban da suke gaba su ɗaga abubuwansu sama, sannan su jagoranci 'yan ajin wajen "faɗin mai nauyi" da kuma "Marar nauyi" da ƙarfi yayin da suke ɗaga abubuwan sama.
- Maimaita aikin ta hanyar ƙara abu na uku mai mabambancin nauyi (Misali, icce). A yi bayanin cewa idan aka sami abubuwa uku ko fiye, mukan bayyana wanda ya fi kowane a matsayin 'Mai nauyin ciki' sannan wanda yake da ƙarancin nauyi kuma a matsayin 'Wanda ya fi kowane ƙarancin nauyi'.

## Gwaji

Aikin bibiyu: Danganta nauyi (minti 15)

- A fitar da dukkan ɗalibai waje, sannan a ce su zauna cikin bibiyu.
- A sa kowane rukunin biyu su zana manyan da'irori guda biyu da yatsarsu ko da itace a ƙasa.
- A sa kowane rukuni na bibiyu su duba tsakani su samo abubuwa daban-daban da za su iya. Waɗannan abubuwan za su iya zama ganyayyaki ko itatuwa ko duwatsu ko kuma duk wani abu da za su iya samu.
- A ce su yanke hukunci a kan wanne ne daga cikin waɗannan abubuwan yake da nauyi wane ne kuma ba shi da nauyi ta hanyar saka dukkan masu nauyin a cikin da'ira ɗaya, sannan marasa nauyi kuma a cikin ɗaya da'irar.
- Zagaya domin lura da ɗalibai yayin da suke tsara abubuwan. Yayin da ake zagayawa a riƙa tambayar ɗalibai ta yadda suke tsara abubuwansu, sannan a tabbatar masu idan suna yi daidai.

## Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa dukkan ɗalibai su sami wani sabon abokin aiki a kusa da su.
- A sa ɗaliban su faɗa wa juna wanne ne daga cikin da'irorinsu ke ɗauke da abubuwa marasa nauyi, sannan kuma waɗannen ne masu ɗauke da abubuwa masu nauyi.

## Aikin Gida

A sa ɗaliban su zana abubuwa guda biyu masu mabambantan nauyi a cikin litattafan rubutunsu.

| Na. 158 | Zango na 3, Mako na 8, Darasi na C |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su yi ƙiyasin nauyi da kuma girman mazubin abubuwa da aka saba amfani da su yau da kullum.
**Kayan Aiki:** Abubuwa masu nauyi daban-daban (duwatsu da ganyayyaki da fensira da kuma litattafan karatu)
**Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)

- Ku rera waƙar tare da ɗalibai.

Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Mage doguwa. Kwalba gajera.
Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
Randa da girma. Moda 'yar karama.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

## Learn

Kiyasin nauyi (minti 8)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu yi ƙiyasin nauyi da kuma girman mazubi. Idan za mu yi ƙiyasin nauyi, mukan yi hasashe ne a kan wane abu ne ya fi nauyi sannan kuma wane ne mara nauyi.*
- Nuna wa 'yan aji abubuwa guda biyu: guntun alli da kuma littafin karatu. Nuna kalmomin guda biyu "Mai nauyi" da "Mara nauyi" da aka rubuta a kan allo.
- A yi bayanin cewa yayin da muke danganta abubuwa guda biyu, sai mu ƙara da "Wanda ya fi" a gaban kalmar. Ɗaga kowane daga cikin abubuwan ɗaya bayan ɗaya, daga nan sai a yi bayanin wane ne mai nauyi wane ne mara nauyi.
- Kara "Ma fi" a gaban  "Nauyi" ko a gaban "Rashin nauyi" a kan allo. A sa ɗalibai su maimaita kalmomin bayan ka faɗa. "Ma fi nauyi" da "Ma fi rashin nauyi".
- A sa ɗalibai biyu su fito gaban aji. A tambayi ɗaya daga cikinsu ya/ta ɗaga littafin ɗalibai, sannan ɗaya kuma ya ɗaga itace. A tambayi ɗaliban wane ne a cikinsu ya fi nauyi.

Kiyasin girman mazubi (minti 7)

- **Ka/ki ce:***Yayin da muka yi kiyasin girman mazubi, muna yin hasashen wane mazubi ne zai fi ɗaukan abubuwa, wane ne kuma zai fi ƙaranci.*
- Nuna wa 'yan aji abubuwa guda biyu: babban kwano da ƙaramin kwano.
- Nuna kalmomin guda biyu "fi" da "gaza" da aka rubuta a kan allo. A sa ɗalibai su maimaita abin da ka/kika faɗa.
- **Ka/ki ce:** *Wane kwano a ganinku zai fi ɗaukan shinkafa?*

## Gwaji

Aiki a ɗaiɗaiku ko bibiyu: Kiyasin nauyi ko girman mazubi (minti 10)

- A ce ɗaliban su buɗe Shafi na 69. A karanta wa ɗalibai umurnin  tambayar farko a bayyane. A sa ɗalibai su zana hotuna a cikin litattafansu na rubutu, sannan su kewaye amsar da ta dace.
- Idan akwai lokaci, a ƙarasa gano amsar tambayar da ke shafin.

## Bayyanawa

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga littafansu domin nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai ƙarasa samo amsoshin aikin da ke Shafi na 69 cikin littafin ɗalibai.

| Na. 159 | Zango na 3, Mako na 8, Darasi na D |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya jera abubuwa dangane da nauyinsu da kuma yawan abin da za su iya ɗauka.
**Kayan Aiki:** Abubuwa masu mabambancin nauyi (duwatsu da ganyayyaki da fensira da kuma litattafan karatu); mazubai guda uku; wake da ruwa da kuma yashi **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)

- Ku rera waƙar tare da ɗalibai.

Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Mage doguwa. Kwalba gajera.
Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Dutse da nauyi. Takarda 'yar shafal.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
Randa da girma. Moda 'yar karama.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

## Koyo

Jera abubuwa dangane da nauyinsu (minti 5)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu jera abubuwa dangane da nauyinsu da kuma girman mazubi. Yanzu mu fara da jerawa dangane da nauyi.*
- Nuna wa 'yan aji mabambantan abubuwa guda uku: buhun shinkafa da marfin kwalba da ganye.
- Nuna kalmomin nan guda biyu "Nauyi" da "rashin nauyi" da ke kan allo.
- A yi bayanin cewa, yayin da za mu danganta abubuwa fiye da biyu, sai mu ƙara "ma fi" a gaban kalma. Kara "Ma fi a gaban "Nauyi" da "Rashin nauyi" da suke kan allo. A sa ɗalibai su maimaita kalmomin "Ma fi nauyi" da "Ma fi rashin nauyi" bayan ka/kin faɗa.
- A sa ɗalibai uku su fito gaban aji. A sa ɗaya ya/ta ɗauki guntuwar takarda, ɗaya guntun alli ɗaya kuma ya/ta ɗauki dutse. A ce su jera abubuwan daga wanda ya fi nauyi zuwa wanda ya fi rashin nauyi.
- Idan akwai lokaci a maimaita da wasu abubuwan da kuma ɗalibai daban.

Jera abubuwa dangane da girman mazubi (minti 5)

- **Ka/ki ce:** *Yanzu kuma za mu jera abubuwa dangane da yawan abin da za su iya ɗauka.*
- Zaɓi mazubi ɗaya a cika shi da wake ko yashi. A ƙidaya yawan abin awu da ya ci.
- ɗauko mazubi na biyu. A sa ɗalibai su yi ƙiyasi ko mazubi na 2 yafi ko bai fi mazubi na 1 ci ba. A saka yashi a cikin mazubi na 2. A maimaita yanayin da mazubi na 3.
- A sa ɗalibai su jera mazuban a kan teburi daga wanda ya fi ƙanƙanta zuwa wanda ya fi girma.

## Gwaji

Aiki a cikin ƙananan rukunai: Jera abubuwa dangane da nauyinsu (minti 15)

- A sa dukkan ɗalibai su fita waje su nemo abu guda ɗaya. Sannan sai a ce dukkan ɗalibai su shiga cikin ƙananan rukunai bayan sun samo abubuwansu, sannan su saka abubuwan a jere daga ma fi nauyi zuwa ma fi rashin nauyi.
- Zagaya domin lura da ɗalibai da bayar da tallafi.

## Bayyanawa

Bayyana wa abokan aiki (minti 5)

- Ɗalibai su tattauna da abokan aikinsu abin da suka yi a cikin rukunoninsu.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su zana abubuwa uku a cikin litattafansu na aiki a jere daga wanda ya fi nauyi zuwa wanda ya fi rashin nauyi. Daga nan kuma su zana abubuwa uku daga wanda ya fi kowane cin kaya zuwa wanda ya fi rashin cin kaya.

| Na. 160 | Zango na 3, Mako na 8, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za suyi bita da gwajin aikin da aka gabatar a makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 3)
- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)
- Ku rera waƙar tare da ɗalibai.

Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Mage doguwa. Kwalba gajera.
Ga girma ga nauyi ga tsayi x2
Dutse da nauyi. Takarda ʻyar shafal.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)
Randa da girma. Moda ʻyar karama.
Ga girma ga nauyi ga tsayi (x2)

**Koyo**

Bita da maimai (minti 10)
- Zaɓi wani labari daga ayyukan mako da ake ganin kamar ɗalibai suna fama da shi. A sake maimaita koyar da shi ko kuma a koyar da shi ta wata hanyar daban.

**Gwaji**

Aiki a ɗaiɗaiku ko cikin ƙungiyoyi: Zanawa da rubutawa (minti 15)
- A ba ɗalibai wani aiki wanda zai taimaka masu gwajin abin da ake bita a kansa (Misali, dangantawa da ƙiyasin nauyi ko girman mazubi). Ɗalibai za su iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma cikin rukunai.
- Yayin da ɗalibai suke mayar da hankalinsu a kan aikinsu, a samar da taimako ga masu buƙata.

**Bayyanawa**

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)
- A sa ɗalibai su nuna ayyukan da suka kammala a lokacin gwaji.

**Aikin Gida**

A ba ɗalibai aikin gida don bita da gwajin abin da suka koya.

**Na. 161**

# Zango na 3, Mako na 9, Darasi na A

**Manufofi:** Ɗalibai za su tattara bayanai a gida da makaranta.

**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)

- Ku rera waƙar tare da ɗalibai.

| Waƙar Kirge | |
|---|---|
| Ɗaya mafarin ƙirge,<br>Biyu idanun dabba,<br>Uku duwatsun murhu,<br>Huɗu ƙafafun tebur,<br>Biyar na yatsun hannu, | Shida ƙafafun sauro.<br>Bakwai kwanakin mako.<br>Takwas goma ba biyu kenan.<br>Tara daga ke sai goma.<br>Goma biyar biyu kenan. |

## Koyo

Gabatarwa ga tsari (minti 5)

| Mata | Maza |
|---|---|
| | |

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu tattara bayanai sannan mu shirya shi cikin tsari mai kyau. Tsari mai kyau yana nufin mu saka bayanai cikin layuka a tsaye da kwance. Wannan zai fi sauƙin fahimta, kuma zai taimaka mana wajen koyon abubuwa ko rukunin abubuwa cikin sauƙi. Misali, za mu iya ƙirga yawan yara maza da mata da ke cikin ajinmu, sannan mu shirya bayanin da muka samu cikin tsari.*
- Umurci ɗalibai guda goma su fito gaban aji. A ce yara su ɗaga hannayensu sama idan su maza ne, sannan sai a rubuta adadinsu a layi na tsaye a jikin taswira da ke kan allo. A maimaita da yara mata.
- **Ka/ki ce:** *Daga nan, sai mu duba waɗannan lambobi don gano tsakanin rukunin yaran da ya fi yawa, kuma wanne ne ya fi ƙaranci.*
- A sa ɗalibai su faɗa da ƙarfi ko yara maza ko mata ne suka fi yawa a ajin. Sannan kuma a sa ɗaliban su faɗi waɗanda suka fi ƙaranci.

## Gwaji

Aiki a ƙananan rukunai: Kirƙirar tsari mai kyau (minti 10)

- A sa ɗalibai su zauna a cikin rukunoni guda huɗu, a ba kowane rukuni wani harafi: A ko B ko C ko kuma D.
- Ɗalibai su ƙidaya adadin yara maza da matan da ake da su a kowane rukuni, sannan su rubuta lambar a cikin litattafansu na rubutu.
- Zagaya domin lura da ɗalibai. Yayin da ake zagayawa, a riƙa tambayar ɗalibai yadda aka yi suka sami amsoshinsu. A tabbatar masu idan sun yi daidai.

## Bayyanawa

Tattaunawa ta dukkan ajin (minti 15)

| | Mata | Maza |
|---|---|---|
| **Rukunin A** | | |
| **Rukunin B** | | |
| **Rukunin C** | | |
| **Rukunin D** | | |
| **Jimilla** | | |

- A sa ɗalibi ɗaya daga kowane rukuni ya karanta bayanan da suka tattara a rukuninsu a bayyane. A rubuta bayanan a taswirar da ke kan allo na rukunonin A – D.
- A tara adadin yara maza da na mata da ke kowane layi sannan a rubuta jimilla.
- A tambayi ɗalibai waɗanne ne suka fi yawa, sannan kuma waɗanne ne suka fi ƙaranta. A kewaye lambobin.
- A tambayi ɗalibai wane rukuni ne yake da mata da yawa. A tambaya wane rukuni ya fi ƙarancin mata. A tambaya wane rukuni ne ya fi yawan yara maza sannan kuma wane ne ya fi ƙarancin yara maza.

## Aikin Gida



A sa ɗalibai su faɗa wa mutanen gidansu ko abokansu fa'idar shirya bayanai cikin tsari mai kyau.

| Na. 162 | Zango na 3, Mako na 9, Darasi na B |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su shirya bayanai cikin tsari mai kyau.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)

- Ku rera waƙar tare da ɗalibai.

| Waƙar Kirge | |
|---|---|
| Ɗaya mafarin ƙirge,<br>Biyu idanun dabba,<br>Uku duwatsun murhu,<br>Huɗu ƙafafun tebur,<br>Biyar na yatsun hannu, | Shida kafafun sauro.<br>Bakwai kwanakin mako.<br>Takwas goma ba biyu kenan.<br>Tara daga ke sai goma.<br>Goma biyar biyu kenan. |

**Koyo**

Wasan dukkan aji: Saka yara maza da mata cikin rukuni-rukuni (minti 10)

- Rataya guntayen takardu guda 2, ɗaya an rubuta "Maza" ɗaya kuma an rubuta "Mata" a wurare daban-daban na cikin ajin.
- A sa ɗalibai su nemi takarda mai ɗauke da jinsin da suke su tsaya a gabanta.
- **Ka/ki ce:** *Idan dukkan ɗalibai suka sami jinsin da suke mun sami rukuni biyu kenan a dukkan ajin.*
- **Ka/ki ce:** *Me kuka lura da shi game da yawan kowane rukuni?*
- **Ka/ki ce:** *Wane rukuni ne ya fi girma? Wane ne ya fi ƙaranta?*
- **Ka/ki ce:** *Mene ne dangantakarku da sauran mutanen da suke rukuninku?*

**Gwaji**

Aiki a ɗiɗaiku ko cikin bibiyu: Saka yara maza da mata cikin rukuni-rukuni (minti 15)

- A sa ɗalibai su buɗe littafinsu zuwa Shafi na 70.
- A yi wa ɗalibai bayanin cewa su ƙirga adadin yara maza da mata da ke cikin hoton sannan su cike taswirar. Daga nan, sai su amsa tambayoyin da ke ƙasan shafin a cikin litattafansu na rubutu.
- Zagaya domin lura da ɗalibai sannan a bayar da tallafi.

**Bayyanawa**

Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu domin nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai.

**Aikin Gida**

A sa ɗalibai ƙarasa samo amsoshin ayyukan da ke Shafi na 70 cikin littafin ɗalibai.

| Na. 163 | Zango na 3, Mako na 9, Darasi na C |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su tattara bayani dangane da shekaru a gida da makaranta.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)

- Ku rera waƙar tare da ɗalibai.

| Waƙar Kirge | |
|---|---|
| Ɗaya mafarin ƙirge,<br>Biyu idanun dabba,<br>Uku duwatsun murhu,<br>Huɗu ƙafafun tebur,<br>Biyar na yatsun hannu, | Shida ƙafafun sauro.<br>Bakwai kwanakin mako.<br>Takwas goma ba biyu kenan.<br>Tara daga ke sai goma.<br>Goma biyar biyu kenan. |

## Koyo

Bita a kan tsari mai kyau (minti 5)

- **Ka/ki ce:** *A wannan makon mun shirya bayanai zuwa tsari mai kyau. Wa zai ba mu misalin tsari mai kyau?*

| Shekara 6 | Shekara 7 | Shekara 8 | Shekara 9 | Shekara 10 |
|---|---|---|---|---|
| | | | | |

- **Ka/ki ce:** *A yau kuma za mu tattara bayani a kan shekarun ɗaliban ajin mu sannan kuma mu shirya bayanan a tsari mai kyau.*
- Umurci ɗalibai guda 10 su fito gaban aji. A ce duk ɗaliban da suka kai shekara 6 su ɗaga hannunsu. Kirga adadin ɗaliban da suka ɗaga hannunsu, sannan a rubuta a layin da ya dace a jikin taswirar da ke kan allo. Maimaita wannan da shekaru 7 da 8 da 9 da kuma 10.
- **Ka/ki ce:** *Daga nan kuma sai mu duba waɗannan lambobi mu gano rukunin da ya fi yawa, sannan kuma wane rukuni ne ya fi ƙaranci.*
- A sa ɗalibai su faɗa a bayyane wace 'yan wace shekara ne suka fi yawa. Sannan kuma a faɗa a bayyane 'yan shekarun da suka fi ƙaranta.

## Gwaji

Aiki a ƙananan ƙungiyoyi: Kirƙirar tsari mai kyau (minti 10)

- A sa ɗalibai su zauna a cikin rukunoni guda huɗu, a ba kowane rukuni wani harafi: A ko B ko C ko kuma D.
- Ɗalibai su ƙidaya adadin ɗaliban da suke kowace shekara a rukuninsu, sannan su rubuta a lambar a cikin litattafansu na rubutu.
- Zagaya domin lura da ɗalibai. Yayin da ake zagayawa, a riƙa tambayar ɗalibai yadda suka samo amsoshinsu. A tabbatar masu idan sun yi daidai.

## Bayyanawa

Tattaunawa ta dukkan aji (minti 15)

- A sa ɗalibi ɗaya daga kowane rukuni ya karanta bayanan da suka tattara a rukuninsu a bayyane. A rubuta bayanan a taswirar da ke kan allo na rukunonin A – D.
- A tara adadin ɗaliban da ke kowane layi sannan a rubuta jimillarsu.

| | Shekaru 6 | Shekaru 7 | Shekaru 8 | Shekaru 9 | Shekaru 10 |
|---|---|---|---|---|---|
| Rukuni A | | | | | |
| Rukuni B | | | | | |
| Rukuni C | | | | | |
| Rukuni D | | | | | |
| Jimilla | | | | | |

- A tambayi ɗalibai wace shekara ce ta fi yawa, sannan kuma wace ce ta fi ƙaranta. A kewaye waɗannan lambobin.
- A tambayi ɗalibai wane rukuni ne yake da 'yan shekara 7 da yawa. A tambaya wane rukuni ya fi ƙarancin 'yan shekara 8.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su tattauna da mutanen gidansu ko abokansu wasu bayanai da za a iya shiryawa cikin tsari mai kyau.

**Na. 164**

# Zango na 3, Mako na 9, Darasi na D

**Manufa:** Ɗalibai za su shirya bayanai a kan shekaru a tsari mai kyau.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

<u>Duba aikin gida (minti 3)</u>

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

<u>Waƙa (minti 2)</u>

- Ku rera waƙar tare da ɗalibai.

| Waƙar Kirge | |
|---|---|
| Ɗaya mafarin ƙirge,<br>Biyu idanun dabba,<br>Uku duwatsun murhu,<br>Huɗu ƙafafun tebur,<br>Biyar na yatsun hannu, | Shida kafafun sauro.<br>Bakwai kwanakin mako.<br>Takwas goma ba biyu kenan.<br>Tara daga ke sai goma.<br>Goma biyar biyu kenan. |

## Koyo

<u>Wasan dukkan aji: Rukunoni dangane da shekaru (minti 10)</u>

- Rataya ƙananan takardu 5 kowace an rubuta shekaru daban-daban a jikinta (6 da 7 da 8 da 9 da kuma 10) a kewayen aji.
- A sa ɗalibai su duba takarda mai ɗauke da shekarunsu sannan su tsaya a gabanta.
- **Ka/ki ce:** *Dukkan ɗalibai sun samu shekarunsu. Mun samu rukunoni guda biyar dangane da shekarunku. Me kuka lura da shi dangane da girman rukunonin? Wane rukuni ne ya fi girma? Wane ne kuma ya fi ƙaranta? Mene ne alaƙarka/ki da sauran mutanen da suke rukuninku?*
- A tambayi ɗalibai waɗanne ne suka fi ƙarancinshekaru ko kuma tsufa.
- Idan akwai lokaci, a sa ɗalibai su shiga wani dogon layi ya fara daga ma fi yarinta zuwa wanda ya fi kowa tsufa.

| | Shekara 6 | Shekara 7 | Shekara 8 | Shekara 9 | Shekara 10 |
|---|---|---|---|---|---|
| Rukunin A | | | | | |
| Rukunin B | | | | | |
| Rukunin C | | | | | |
| Rukunin D | | | | | |
| Jimilla | | | | | |

## Gwaji

<u>Aiki a ɗaiɗaiku ko cikin bibiyu: Kafa rukunoni dangane da shekaru (minti 15)</u>

- A sa ɗalibai su buɗe littafinsu zuwa Shafi na 71.
- A yi wa ɗalibai bayanin cewa su ƙirga adadin mutanen da suke kowace shekara cikin hoton sannan su cike taswirar. Daga nan, sai su amsa tambayoyin da ke ƙasan shafin a cikin litattafansu na rubutu.
- Zagaya domin lura da ɗalibai sannan a bayar da tallafi.

## Bayyanawa

<u>Auna fahimta cikin gaggawa (minti 5)</u>

- A sa ɗalibai su ɗaga takardunsu domin nuna abin da suka rubuta. A yaba wa ɗalibai.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai ƙarasa samo amsoshin aikin da ke Shafi na 71 cikin littafin ɗalibai.

| Na. 165 | Zango na 3, Mako na 9, Darasi na E |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za suyi bita da gwajin aikin da aka gabatar a makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)

- Ku rera waƙar tare da ɗalibai.

| Waƙar Kirge | |
|---|---|
| Ɗaya mafarin ƙirge,<br>Biyu idanun dabba,<br>Uku duwatsun murhu,<br>Huɗu ƙafafun tebur,<br>Biyar na yatsun hannu, | Shida kafafun sauro.<br>Bakwai kwanakin mako.<br>Takwas goma ba biyu kenan.<br>Tara daga ke sai goma.<br>Goma biyar biyu kenan. |

**Koyo**

Bita da maimai (minti 10)

- Zaɓi wani labari daga ayyukan mako da ake ganin kamar ɗalibai suna fama da shi. A sake maimaita koyar da shi ko kuma a koyar da shi ta wata hanyar daban.

**Gwaji**

Aiki a ɗaiɗaiku ko cikin rukunoni: Zanawa da rubutawa (minti 15)

- A ba ɗalibai wani aiki wanda zai taimaka musu gwajin abin da ake bita a kansa (Misali, tattara bayanai a kan shekaru da kuma yin tsari mai kyau). Ɗalibai za su iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma cikin ƙungiyoyi.
- Yayin da ɗalibai suke mayar da hankalinsu a kan aikinsu, a samar da taimako ga masu buƙata.

**Bayyanawa**

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna ayyukan da suka kammala a lokacin gwaji.

**Aikin Gida**

A ba ɗalibai aikin gida don bita da gwajin abin da suka koya.

**Na. 166**

# Zango na 3, Mako na 10, Darasi na A

**Manufofi:** Ɗalibai su iya samo abubuwa masu surori fuska biyu su kuma bayyana wa ajin.
**Kayan Aiki:** fallen takarda ɗauke da zanen surori masu fuska biyu da sunayensu **Lokaci:** Minti 35

**Fara darasi**

Duba aikin gida (minti 2)


- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Ni wace sura ce? (minti 3)

- Wasan Ni wace sura ce? Karanta wa ɗalibai waɗannan bayanai. A sa ɗalibai amsa tambayoyin ta ambaton sunan surar a bayyane. Idan ɗaliban sun amsa tambaya daidai, sai a nuna masu surar a kan allon.
- **Ka/ki ce:** *Ba ni da ɓangarori. A kewaye nake. Wace sura ce ni?*
- **Ka/ki ce:** *Ina da ɓangare uku. Wace sura ce ni?*

**Koyo**

Gabatar da surori masu fuska 2 (minti 10)



- **Ka/ki ce:** *Yau za mu san abu game da surori masu fuska biyu. Sura mai kusurwa 4 da mai murabba'i da mai kusurwa uku da kuma mai siffar da'ira duka surori ne masu fuska biyu wannan na nufin a shimfiɗe suke.*
- **Ka/ki ce:** *Akwai cikinku wanda yake da wata sura da ya fi so? Me ya sa?*
- Nuna surorin da ke kan allon a kuma ambaci sunayensu ɗaya bayan ɗaya. A ce wa ɗaliban su faɗi sunayen surorin bayan ka ambace su.
- A sa ɗaliban su miƙe tsaye su ɗaga yatsa sama, sannan su zana surorin nan guda huɗu cikin iska (Sura mai siffar murabba'i, mai kusurwa huɗu, mai kusurwa uku, da mai siffar da'ira) da yatsun nasu.
- A sa ɗaliban su zana surori mabambanta da sassan jikinsu. Misali, su riƙe dantsensu a da'ira su samar da siffar da'ira ko su yi amfani da babban ɗan yatsa da manuniya su samar da sura mai kusurwa huɗu.
- A tambayi ɗalibai inda suke iya ganin waɗannan surori kullum (misali, idanunsu a kewaye suke kuma littafinsu yana da sura mai kusurwa huɗu)

**Gwaji**

Aiki a ƙaramin rukuni : surori masu fuska biyu (minti 15)

- Ɗalibai su zauna a ƙananan rukunoni. A ba kowane rukuni fallen takarda ɗauke da surori masu fuska 2 (sura mai kusura, mai siffar murabba'i dasauransu.). Sunan kowace sura ya kasance a jikin takardar.
- A ce wa ɗaliban su fita wajen aji su nemo misalan surori da ke harabar makarantar. Da zarar sun samo abun da ya dace da surar da ke rukuninsu, sai su zana hoton abun a cikin littafin rubutunsu.
- A zagaya a duba aikin da ɗalibai ke yi. A yayin zagayawar, a tambaye su abubuwan da suke zanawa da sunan surorinsu, sai a duba ko sun yi daidai.
- Bayan minti 15, kira ɗalibai su koma aji.

**Bayyanawa**

Bayyana kyawawan misalai (minti 5)

- A sa rukunoni ɗalibai su bayyana wa juna misalan da suka samo.

**Aikin gida**


A sa ɗalibai su zana sura mai siffar da'ira da ta murabba'i da mai kusurwa huɗu da kuma mai kusurwa uku a cikin littafin rubutunsu.

| Na. 167 | Zango na 3, Mako na 10, Darasi na B |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai su iya sanya abubuwa masu fuska biyu rukuni -rukuni dangane da surarsu.
**Kayan Aiki:** fallen takarda ɗauke da siffofi mabambanta; ƙananan siffofi da aka yi su da takarda
**Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)



- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Labari cikin hotoi (minti 5)

- Karanta wa ɗalibai labarin cikin hoto na kan allon. Ali ya koyi wani abu game da siffofi a makaranta . A kan hanyarsa ta zuwa gida, ya ga siffofi a ko'ina. Rana tana da siffarda'ira, akwati yana da siffar murabba'i da kuma littafinsa yana da siffar kusurwa huɗu.
- A kira ɗalibi ɗaya zuwa gaban allo. A yayin sake karanta labarin, ɗalibi ya riƙa taɓa sifa da aka ambata a labarin . Misali, rana tana da siffarda'ira, sai ɗalibi ya nuna sifar da'ira da ke kan allon.

## Koyo

Ware Siffofi (minti 8)

- A jikin kowane bango na ajin, liƙa fallen takarda ɗauke da wata siffa. Misali, siffa mai kusurwa uku da mai kusurwa huɗu da mai murabba'i da kuma da'ira.
- Ba kowane ɗalibi da ke ajin zanen 'yar ƙaramar siffa.
- Ace wa ɗaliban su kewaya cikin aji su je su tsaya a kusa da siffa da ta dace da wadda aka ba kowannen su.
- A ce su tattauna da juna kan sunan siffar da ke hannunsu. A kuma ce su tattauna kan wasu abubuwa da suka sani da suka yi kama da siffofin nasu.
- A kewaya a duba abin da suke yi. A tambayi kowane rukuni sunan siffan nasu.

## Gwaji

Wasan aji bai-ɗaya: Neman wasu siffofin (minti 15)

- Faɗa wa ɗalibai cewa za su je neman siffa kuma su tabbata sun samo siffofi uku mabambanta don cikar rukuninsu. Misali, idan ɗalibi ɗaya ya sami siffa mai kusurwa uku, sai a sami wani mai siffar da'ira, wani da siffarr murabba'i, da kuma wani siffara kusurwa huɗu sai su haɗu su samar da rukuni.
- Da zarar ɗaliban sun kafa rukunonin, sai a kira kowa ya faɗa wa juna sunan siffofin da ke rukuninsa.
- A faɗa masu cewa su tabbata kowane ɗan rukuni zai iya faɗar sunan siffofin da ke rukuninsa.
- Idan da lokaci, a sa ɗalibai su sake ƙirƙirar wasu rukunoni.

## Bayyanawa

Gaggauta auna fahimta (minti 5)

- A ce su ambacin sunan siffa a bayyane. A sa dukan ɗaliban da ke riƙe da siffar ɗagawa sama.
- Ku maimaita da duka siffofin.

## Aikin Gida

A ce wa ɗalibai su zo da wani abu daga gida da ya yi kama da ɗaya daga cikin siffofin nan guda huɗu: siffa mai kusurwa uku ko mai siffar da'ira ko mai siffar murabba'i ko kuma mai kusurwa huɗu.

**Na. 168** | # Zango na 3, Mako na 10, Darasi na C

**Manufa:** Ɗalibai su iya haɗa abubuwa masu fuska biyu dangane da siffarsu.
**Kayan Aiki:** Siffofi da aka ƙirƙira (siffa mai kusurwa uku da mai murabba'i da kuma mai kusurwa huɗu) **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)


- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Ni wace sura ce? (minti 3)

- Karanta wa ɗalibai waɗannan bayanai. A sa ɗalibai amsa tambayoyin ta ambaton sunan siffar a bayyane. Idan ɗaliban sun amsa tambaya daidai, sai a nuna masu siffar a kan allon.
- **Ka/ki ce:** *Ina da ɓangarori biyu da suke dogaye da wasu biyu gajeru. Ɓangarorin da suke kallon juna tsawonsu ɗaya. Wace sura ce ni?*
- **Ka/ki ce:** *Ina da ɓangare huɗu tsawonsu ɗaya. Wace sura ce ni?*

## Koyo

Gabatar da ware siffofi (minti 10)



- **Ka/ki ce:** *Yau za mu duba abubuwa da suke kama da juna mu bayyana siffofin da suka haɗa su.*
- Zana hoton a kan allon sai a tambayi ɗaliban abin da suka gani.
- Sannan, a tambayi ɗalibai waɗanne siffofi suka samar da abubuwan da ke hoton. Misali, rana tana da siffa da'ira, sai kuma mota tana da kewayayyun tayu.
- Idan lokaci ya saura, a tambai ɗalibai abin da za su iya ƙara wa hoton.
- A kira wasu ɗalibai su je kan allo su zana wa aji hoton da suke so.  A tambayi sauran ɗalibai siffofin da aka samar da hoton da aka zana.

## Gwaji

Aiki a ƙaramar rukuni : Ware siffofi (minti 15)

- A ce wa ɗalibai su yi aiki a cikin rukuninsu wajen zana hoton abubuwan da ke ajin da aka samar da siffofi mabambanta. A sa ɗalibai su ƙoƙarta wajen shigar da sura mai kusurwa da da'ira da mai murabba'i da kuma mai kusurwa huɗu cikin zanensu.
- A kewaya a duba abin da suke yi, sannan a taimaka masu.

## Bayyanawa

Bayyana kyawawan misalai (minti 5)

- A sa kowane rukuni ya nuna abin da ya zana. A tattauna da aji siffofin da kowane rukuni ya samu a cikin ajin da suke kama da na wani rukuni  da kuma waɗanda suka bambanta.

## Aikin Gida


A ce wa ɗalibai su zana hoton abubuwa a gida da ake samar da su da siffofi daban-daban.

| Na. 169 | Zango na 3, Mako na 10, Darasi na D |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai su iya gano adadin ɓangarori na kowace siffa.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

<u>Duba aikin gida (minti 2)</u>




- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

<u>Labari cikin hoto (minti 3)</u>

- Karanta wa ɗalibai labarin hoton dake kan allon. Ishak yana kan hanya zuwa gida. Lokacin da ya isa gidan, sai ya fahimci cewa gidansa na ɗauke da siffofi mabambanta masu yawa.
- **Ka/ki ce:** *Waɗanne siffofi kuka iya gani a hoton gidan Ishak?*

**Koyo**

<u>Gabatar da ɓangarorin siffofi (minti 10)</u>



- **Ka/ki ce:** *Yau za mu san mabambanta ɓangarorin siffa mai kusurwa uku da mai kusurwa huɗu da mai siffar murabba'i. Ɓangarorin siffa su ne layukan da suka haɗe siffr daga kusurwa ɗaya zuwa waninsa.*
- Zana siffar murabba'i a kan allon. A yayin da ake nuna kowane ɓangare na siffar, sai ku ƙirga adadin ɓangarorin a bayyane tare da ɗalibai.
- **Ka/ki ce:** *Siffar murabba'i na da ɓangarori huɗu kuma dukansu tsawonsu ɗaya.*
- A kira ɗalibai uku zuwa gaban aji a sa su zana siffa mai kusurwahuɗu da siffa mai kusurwa uku da da'ira a kan allon. A umurci ɗalibai su ƙirga a bayyane yawan ɓangarorin.
- **Ka/ki ce:** *Siffa mai kusurwa huɗu na da ɓangarori huɗu.bangarorin da suke fuskantar juna tsawon su ɗaya. Mafi yawon lokaci, ɓangare biyu na da tsawo, sauran ɓangare biyu kuma gajeru ne.*
- **Ka/ki ce:** *Siffa mai kusurwa uku na da ɓangarori uku, sai kuma d'irori ba su da wani ɓangare saboda a kewaye suke!*

**Gwaji**

<u>Aiki a ƙaramin rukuni: Kirkirar siffofi (minti 15)</u>

- A sa ɗalibai su samo sanduna da yawa, tsakuwoyi da ganyayyaki a wajen aji da sauri.
- Bayan minti 5, kira ɗalibai su koma aji da abubuwan da suka samo su kuma zauna a ƙananan rukunoni.
- A kira kowane rukuni ya yi amfani da abubuwan da ya samo ya yi siffa mai kusurwa huɗu da mai kusurwa uku da siffar murabba'i da kuma da'ira. Su kuma rubuta adadin ɓangarorin kowace sura da suka yi a takarda sai su ajiye a tsakiyarta.
- A kewaya a duba abin da suke yi, sannan a taimaka masu.

**Bayyanawa**

<u>Bayyana kyawawan misalai (minti 5)</u>

- A zaƙulo rukuni ɗaya ko biyu da suka yi zane masu kyau. A sa sauran aji su miƙe su ga abin da suka yi.

**Aikin Gida**

A ce wa ɗalibai su tattauna da wani a gida ko abokinsu kan abin da suka sani game da siffa mai kusurwa huɗu da da'iara da kuma siffa mai kusurwa uku. Ɗaliban su faɗa masu adadin ɓangarorin kowace sura da suka bayyana masu.

**Na. 170** | 

# Zango na 3, Mako na 10, Darasi na E

**Manufofi:** Ɗalibai su iya yin bita da gwajin aikin da aka gabatar a makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Ni wace siffa ce? (minti 5)

- Wasan Ni wace siffa ce? Karanta wa ɗalibai waɗannan bayanai. A sa ɗalibai amsa tambayoyin ta ambaton sunan siffar a bayyane. Idan ɗaliban sun amsa tambaya daidai, sai a nuna musu siffar a kan allon.
- **Ka/ki ce:** *Ina da ɓangare huɗu. biyu gajeru biyu kuma dogaye. wace siffa ce ni?*
- **Ka/ki ce:** *Ba ni da ɓangarori. a kewaye nake. Wace sura ce ni?*

## Koyo

Bita da maimai (minti 8)

- Zaɓi wani labari daga ayyukan mako da ake ganin kamar ɗalibai suna fama da shi. A sake maimaita koyar da shi ko kuma a koyar da shi ta wata hanyar daban.

## Gwaji

Aiki ɗaiɗai ko a cikin rukuni: Zane da rubutu (minti 15)

- Ba ɗalibai jingar da za ta taimaka masu su gwada abin da aka yi masu bita a kai (misali, gano siffofri masu murabba'i da masu kusurwa huɗu da masu kusurwa uku). Ɗalibai za su iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma cikin ƙananan rukunoni.
- Yayin da ɗalibai suka mayar da hankali kan yin aikin jingar, a taimaka wa ɗaliban da suke buƙatar matuƙar taimako.

## Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A ce wa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala yayin gwajii.

## Aikin Gida

A ba ɗalibai aikin gida da za su yi bita da kuma nuna ƙwarewarsu.

| Na. 171 | Zango na 3, Mako na 11, Darasi na A |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai su iya samo abubuwa masu fuska uku da tattaunawa a aji.
**Kayan Aiki:** Fallen takarda ɗauke da hoton siffofi masu fuska3 da sunayensu; ire-iren siffofi masu fuska 3, kamar ƙwallon ƙafa guda 3, alƙalamin rubutu ko taɓare, alli, littafi da akwati
**Lokaci:** Minti 35

**Fara darasi**

Duba aikin gida (minti 2)


- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Ni wace sura ce? (minti 3)

- Karanta wa ɗalibai waɗannan bayanai. A sa ɗalibai su amsa tambayoyin ta ambaton sunan siffar a bayyane. Idan ɗaliban sun amsa tambaya daidai, sai a nuna masu siffar a kan allon.
- **Ka/ki ce:** *Ina da ɓangare huɗu. Biyu daga ciki gajeru da kuma biyu dogaye. ɓangarori masu kallon juna tsawonsu ɗaya. Wace sura ce ni?*
- **Ka/ki ce:** *Ina da ɓangare huɗu, kuma duka ɓangarorin daidai suke. Wace sura ce ni?*

**Koyo**

Gabatar da abubuwa masu fuska 3 (minti 10)



- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi siffa mai fuska 3. Siffa mai kusurwa huɗu da mai kusurwa uku da kuma da'ira duk siffofi ne masu fuska biyu da ke nuna cewa shimfiɗaɗɗu ne. Abubuwa masu fuska uku ba shimfiɗaɗɗu ba ne. Yau za mu san sunayen abubuwa huɗu masu fuska uku: sura mai siffar dunƙulen magi da mai siffar kwalin ashana da silinda da kuma mai alamar ƙwallo.*
- Nuna wa ajin abubuwan da aka tattaro, a faɗa musu sunan kowace sura da aka ɗaga su gani (misali, a ƙwallon ƙafa a kewaye yake, akwati ko dai ya kasance mai alamar dunƙulen magi ko kuma kwalin ashana, alli yana da siffar silinda, littafi yana da surar kwalin ashana). Ɗaliban su maimaita faɗin sunan siffofin bayan an furta sunansu.
- Kira wani ɗalibi zuwa gaban aji ya bayyana kamanci da kuma bambancin da ke tsakanin siffofin (misali, siffar dunƙulen magi dasiffar kwalin ashana dukansu na da siffa murabba'i). A maimaita da wasu ɗaliban.
- Ku sake ambatar sunayen siffoin tare da ɗaliban karo na ƙarshe.

**Gwaji**

Aiki a ƙaramin rukuni: Siffofi masu fuska 3 (minti 15)

- Ɗalibai su zauna a ƙananan rukunai. Bakowane rukuni fallen takarda ɗauke da hoton abubuwa masu fuska 3 (siffar ƙwai da mai siffar kwalin ashana da silinda da kuma mai siffar dunƙulen magi). Ko wace siffa da sunanta a rubuce.
- A ce wa ɗaliban su fita wajen aji su nemo misalan siffofi da ke harabar makarantar. Da zarar sun samo abun da ya dace da siffar da ke rukuninsu, sai su zana hoton abin a cikin littafin rubutunsu.
- A zagaya a duba aikin da ɗalibai suke yi. A yayin zagayawar, a tambaye su abubuwan da suke zanawa da sunan surorinsu, sai a duba ko sun yi daidai.
- Bayan minti goma, kira ɗalibai su koma aji.

**Bayyanawa**

Bayyana kyawawan misalai (minti 5)

- A sa rukunonin ɗalibai su bayyana wa juna misalan da suka samo.

**Aikin Gida**


A ce wa ɗalibai su nemi wani misalin, a gida, na wani abu da za su zana a matsayin gwaji. A ce masu su zana hoton sabon abun nan a cikin littafin rubutunsu a gaban hoton da suka zana a aji.

| Na. 172 | Zango na 3, Mako na 11, Darasi na B |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya haɗa abubuwa masu fuska 3 dangane da siffaru.
**Kayan Aiki:** Ire-iren abubuwa masu fuska 3, kamar kwallo 3, alƙalami ko teburi, alli, littafi, da akwati
**Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)



- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Labari cikin hoto (minti 5)

- Karanta wa ɗalibai labarin cikin hoto a kan allon. Ali ya koyi wani abu game da siffofi a makaranta. A kan hanyarsa ta zuwa gida, ya ga siffofi a ko'ina. Rana tana da siffar da'ira, gangar jikin bishiya silinda ce, littafinsa kuma sura ce mai kusurwa huɗu.
- A kira ɗalibi ɗaya zuwa gaban allo. A yayin sake karanta labarin, ɗalibi ya riƙa taɓa surar da aka ambata a labarin. Misali, rana tana da siffar da'ira, sai ɗalibi ya nuna siffar da'ira da ke kan allon.

### Koyo

Ware abubuwa masu fuska 3 (minti 8)

- A sa duka ɗalibai su zana siffa mai fuska 3 a cikin littafin rubutunsu. Za su iya zana kowace siffar mai fuska 3.
- Yayin da ɗalibai ke yin zanen, manna hoton abubuwa masu fuska 3 cikin ajinnesa da juna.
- Sa ɗalibai su dudduba su zaƙulo hoton da ya yi kama da wanda suka zana.
- Sa ɗalibai su tattauna da juna kan sunan hoton da suka zana. A kuma ce su tattauna kan wasu abubuwa da suka sani da suka yi kama da siffofin nasu.
- A kewaya a duba abin da suke yi. A tambayi ɗaliban kowane rukuni su ambaci sunan siffarsu.

### Gwaji

Wasan aji bai-ɗaya: Neman wasu abubuwan (minti 15)

- A faɗa wa ɗalibai cewa za su je neman abu kuma su tabbata sun samo guda uku mabambanta. Don cikar rukuninsu. Misali, idan wani ɗalibi ya samo siffar dunƙulen magi, sai ya duba wanda yake da siffar silinda, da mai siffar kwalin ashana da kuma mai siffar ƙwallo sai su kafa rukuni .
- Da zarar sun kafa rukunai, sai a sa su faɗa wa juna sunayen abubuwan nasu.
- A ce masu su tabbata kowa a rukunin zai iya ambaton sunan siffarsu.
- Idan da lokaci, a sa ɗalibai su sake ƙirƙirar wasu rukunonin.

### Bayyanawa

Gaggauta auna fahimta (minti 5)

- Ambaci sunan wani abu a bayyane. A sa duka ɗaliban da ke da hoton wannan abu su ɗaga sama.
- Yi haka da sauran abubuwan.

### Aikin Gida

A ce wa ɗalibai su nemi wani abu a gida da ya yi kama da ɗaya daga cikin siffa mai fuska 3. Su kuma gwada zana hoton abun a littafin rubutunsu.

| Na. 173 | Zango na 3, Mako na 11, Darasi na C |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane bambancin da ke tsakanin shimfiɗaɗɗun surori da dunƙulallu.
**Kayan Aiki:** siffofi masu fuska 3 da masu fuska 2 (murabba'i, da'ira, alli, littafi, akwati, kwallo, dasauransu.) **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)


- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Ni wace sura ce? (minti 3)

- Wasan Ni wace sura ce? Karanta wa ɗalibai waɗannan bayanai. A sa ɗalibai su amsa tambayoyin ta ambaton sunan siffar a bayyane. Idan ɗaliban sun amsa tambaya daidai, sai a nuna masu siffar a kan allon.
- **Ka/ki ce:** *Ina da ɓangare huɗu kuma a shimfiɗe nake. Waɗanne sura guda biyu zan kasance?*
- **Ka/ki ce:** Ni a miƙe nake kamar alli. *Wace sura ce ni?*

**Koyo**

Gabatar da shimfiɗaɗɗun siffoi da dunƙulallu (minti 10)



- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi* shimfiɗaɗɗun siffofi da dunƙulallu*.*
- Nuna kowace shimfiɗaɗɗiyar siffa da ke kan allon sai a sa ɗaliban su faɗi sunanta a bayyane.
- Nuna wa ɗalibai siffa mai kama da dunƙulen magi (misali, akwati) sai a sanya ta kusa da siffa murabba'i da ke kan allon.
- A tambayi ɗalibai su faɗi bambancin da suka iya gani tsakanin siffar murabba'i da siffar dunƙulen magi.
- **Ka/ki ce:** *Abubuwa, kamar wannan siffa ta dunƙulen magi, dunƙulallu ne. Siffofi, kamar wannan murabba'i da ke kan allo,shimfiɗaɗɗu ne.*
- A sa ɗalibai su maimaita faɗin "dunƙulalle" da "shimfiɗaɗɗe" bayan an faɗa.
- Nuna wa ajin cewa siffar dunƙulen magi na da siffar murabba'a a kowane ɓangarenta. Yi bayani cewa dunƙulalliyar siffa tana da ɓngarori da suka ƙunshi na shimfiɗaɗɗun surori.

**Gwaji**

Aiki daidai: Zanen siffr dunƙulen magi da ta ashana (minti 15)

- Sa ɗalibai buɗe littafinsu Shafi na 72.
- **Ka/ki ce:** *Yau za mu gwada yin zanen siffr dunƙulen magi da ta kwalin ashana.*
- Ce wa ɗalibai su bi matakan da ke shafi na gaba su zana siffar dunƙulen magi da ta kwalin ashana a cikin littafin rubutunsu. Za su iya yin aikin tare da abokinsu idan suna buƙatar taimako.
- A zagaya a duba abin da suke yi. A yayin kewayawar, a duba a ga idan suna yin abin da ya kamata, a kuma taimaka wa mai buƙata.

**Bayyanawa**

Gaggauta auna fahimta (minti 5)

- A sa ɗalibai su ɗaga takardarsu su nuna abin da suka yi. A kuma yaba masu.

**Aikin Gida**

A ce wa ɗalibai su zana ƙarin hotuna masu siffr dunƙulen magi da na kwalin ashana bibbiyu a cikin littafin rubutunsu.

| Na. 174 | Zango na 3, Mako na 11, Darasi na D |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya gane siffar ƙwallo da kuma silinda.
**Kayan Aiki:** Abubuwa masu fuska 3 (alli, littafi ko akwati, kwallo, dasauransu) **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)
- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Ni wace sura ce? (minti 3)
- Wasan Ni wace sura ce? Karanta wa ɗalibai waɗannan bayanai. A sa ɗalibai su amsa tambayoyin ta ambaton sunan siffr a bayyane. Idan ɗaliban sun amsa tambaya daidai, sai a nuna masu siffr a kan allon.
- **Ka/ki ce:** *Ni sura ce kamar bal. Wane abu ne ni?*
- **Ka/ki ce:** *Ina da ɓangare uku kuma a shimfiɗe nake. Wane abu ne ni?*

**Koyo**

Fasalin siffofi da abubuwa: Ɓangarori da kusurwa (minti 10)
- **Ka/ki ce:** *Yau za mu koyi ɓangarori da kusurwan siffofi. Ɓangarorin siffa ko abu na da tsawo, da shimfiɗaɗɗun gyaffa. Kusurwa shi ne inda ɓangare biyu suka haɗu da juna na siffa ko abu.*
- Ɗaga littafi sama aji su gani. A tambayi ɗalibai ko za su iya faɗin sunan siffaar. A kuma tambaye su siffa ce shimfiɗaɗɗiya ko kuwa dunƙulalliya.
- Ku ƙirga ɓangarorin littafin tare da ɗalibai. Gaba, Ku ƙirga kusurwan.
- Kira ɗalibi ɗaya zuwa gaban aji. Ba shi alli ɗaya.
- A sa ɗalibin ya faɗa wa sauran aji sunan abin kuma dunƙulalle ne ko kuwa shimfiɗaɗɗe.
- A sa ɗalibin ya faɗi adadin ɓangarori da kusurwan allin.
- **Ka/ki ce:** *Da'ira ba ta da ɓangarori! A kewaye take, ko'ina da ina. Idan ko ba ɓangarori, to babu mahaɗa kenan. Don haka silinda, siffar ƙwallo,da da'ira ba su da ɓangarori da kuma kusurwa.*
- Idan da lokaci, a sake maimaita da wani abin da kuma wani ɗalibin na daban.

**Gwaji**

Aiki ɗaiɗai: Zanen siffar ƙwallo da silinda (minti 15)
- A sa ɗalibai su buɗe littafinsu Shafi na 73.
- **Ka/ki ce:** *Yau za mu gwada zanen siffr ƙwallo da silinda.*
- A ce wa ɗalibai su bi matakan da ke shafi na gaba su zana siffar ƙwallo da ta silinda a cikin littafin rubutunsu. Za su iya yin aikin tare da abokinsu idan suna buƙatar taimako.
- A zagaya a duba abin da suke yi. A yayin kewayawar, a duba a ga idan suna yin abin da ya kamata, a kuma taimaka wa mai buƙata.

**Bayyanawa**

Gaggauta auna fahimta (minti 5)
- A sa ɗalibai su ɗaga takardarsu su nuna abin da suka yi . A kuma yaba musu.

**Aikin Gida**

A ce ɗalibai su zana ƙarin siffar anƙwati da ta silinda guda bibbiyu a cikin littafin rubutunsu.

| Na. 175 | Zango na 3, Mako na 11, Darasi na E |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya yin bita da gwajin aikin da aka gabatar a makon.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Wasan Ni wace sura ce? (minti 5)

- Wasan Ni wace siffa ce? Karanta wa ɗalibai waɗannan bayanai. A sa ɗalibai amsa tambayoyin ta ambaton sunan siffar a bayyane. Idan ɗaliban sun amsa tambaya daidai, sai a nuna musu siffar a kan allon.
- **Ka/ki ce:** *Ina da ɓangare huɗu. Biyu gajeru biyu kuma dogi. Wace siffa ce ni?*
- **Ka/ki ce:** *Ba ni da ɓangarori. A kewaye nake. Wace siffa ce ni?*

### Koyo

Bita da maimaitawa (minti 8)

- Zaɓi wani labari daga ayyukan mako da ake ganin kamar ɗalibai suna fama da shi. A sake maimaita koyar da shi ko kuma a koyar da shi ta wata hanyar daban.

### Gwaji

Aiki ɗaiɗai ko a cikin rukuni : Zane da rubutu (minti 15)

- Ba ɗalibai jingar da za ta taimaka masu su gwada abin da aka yi masu bita a kai (misali, gano surori masu siffar silinda da na dunƙulen magi da na kwalin ashana da na ƙallo). Ɗalibai za su iya yin aiki a ɗaiɗaikunsu ko kuma cikin ƙananan ƙungiyoyi.
- Yayin da ɗalibai suka mayar da hankali kan yin aikin jingar, a taimaka wa ɗaliban da suke buƙatar matuƙar taimako.

### Bayyanawa

Auna fahimta da bayyanawa (minti 5)

- A ce wa ɗalibai su nuna aikin da suka kammala yayin gwajii.

### Aikin Gida

A ba ɗalibai aikin gida da za su yi bita da kuma nuna ƙwarewarsu.

**Na. 176**

# Zango na 3, Mako na 12, Darasi na A

**Manufa:** Ɗalibai za su iya rubuta gajeren gwaji na lissafi.
**Kayan Aiki:**

## JARRABAWA GWAJI

A gabatar masu da gwaji ɗaya bayan ɗaya sai a rubuta sakamakon nasu a littafin rubuta sakamakon jarrabawa. Idan da buƙata, a nemi taimakon shugaban makarantar ko membobin kwamitin kula da makarantu (SBMC), ko wasu malamai domin taimakawa gudanar da gwajin.

A samar wa ɗalibai wani aikin jinga a yayin da suke jiran rubuta gwajin. Misali, ɗalibai na iya gwada gano siffofi masu fuska 2 da masu fuska 3.

| Jaha: | | Karamar hukuma: | | Makaranta: | | Wata: | | Shekara: | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|


| Lamba | Sunan Ɗalibi | Jinsi | Shekaru | Buƙata ta musamman (Eh/A'a) | Kima | Nauyi | Siffa dangin 3 | Siffofi | Jimillar maki |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| | | | | | /3 | /3 | /4 | /5 | / 15 |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |
| | | | | | | | | | |

# Darasin Lissafi Aji 2, Zango na 3, Mako na 12 – Jarrabawar ƙarshen Zango

**Wane kwano ne zai fi ɗaukar adadi wani abu mai yawa?** (A bayar da maki uku idan an amsa daidai)




**Wanne ne ya fi nauyi daga cikin waɗannan?** (A bayar da maki uku idan an amsa daidai)



**Wace siffa ce mai dangi 3 daga cikin waɗannan?** (A bayar da maki biyu ga kowace amsa)



**A lissafa adadin fasulla da suke da ɓangare 4 a cikin waɗannan.** (A bayar da maki ɗaya ga kowace amsa)



| Na. 177 | Zango na 3, Mako na 12, Darasi na B |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya ware da kuma jera abubuwa gida gida dangane da girma da kuma launinsu.
**Kayan Aiki:** Abubuwa (tsakuwoyi, sanduna, murafan kwalba, ganyayyaki) **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 3)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Waƙa (minti 2)

- Sa ɗalibai ku rera waƙar tare.

Zan iya rarrabewa, zan iya rarrabewa.
Lalle zan iya. Lalle zan iya.
Za ku iya rarrabe wake?
Za ku iya rarrabe wake?
Lalle zan iya. Lalle zan iya.

**Koyo**

Jere dangane da girma (minti 5)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu ware abubuwa gida-gida dangane da girma da kuma launin su.*
- Ɗaga tsakuwa guda uku mabambanta sama aji su gani: ƙarami, matsakaici, da babba. Sa ɗalibai su ware su dangane da girmansu a jere.
- Ku sake da wasu abubuwa masu kamanni da waɗanda suka bambanta.

Jere dangane da launi (minti 5)

- Kira ɗalibi 1 zuwa gaban aji ya zaɓi wani abu ɗaya. A sa shi ya bayyana launin abin da ya zaɓa.
- A kira wani ɗalibin ya yi da wani abin kamar na farko.

**Gwaji**

Aiki a ƙaramin rukuni : Jere dangane da girma da launi (minti 15)

- Ɗalibai su zauna a ƙananan rukunoni.
- A zaɓi shugaba da zai taimaka wajen rarraba wa rukunoni abubuwa mabambanta.
- A sa ɗaliban su sanya abubuwan gida uku dangane da girmansu.
- Sannan, a sa  su sanya su dangane da launin gida-gida.
- A zagaya a duba abin da suke yi. A yayin zagayawar, a tambaye su dangane da kamanci da bambancin abubuwan da ke gun su, sannan a duba ko sun yi daidai.

**Bayyanawa**

Nuna wa abokin aiki (minti 5)

- Ɗalibai su tattauna da abokin aiki abin da suka yi a rukuninsu.

**Aikin Gida**

A ce wa ɗalibai su nemo abubuwa uku masu launi iri ɗaya, amma mabambanta girma, a gida. Su zana hotonsu a jere dangane da girma a cikin littafin rubutunsu.

| Na. 178 | Zango na 3, Mako na 12, Darasi na C |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya tattaro bayanai kan tsayi.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

### Fara Darasi

Duba aikin gida (minti 2)

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Gajere da dogo (minti 3)

- Umurci ɗalibai 5 su fito gaban aji su jeru daga mafi gajerta zuwa mafi tsawo.
- **Ka/ki ce:** *Wane ɗalibine mafi tsawo? Wanene kuma mafi gajerta?*

### Koyo

Bita: awon tsayi (minti 10)

- **Ka/ki ce:** *Yau za mu gwada yin awon tsayin ɗaliban ajinmu ta amfani da jadawali. A makon baya, mun auna tsayin ɗalibai da hannunmu. Yau, za mu yi amfani da fensir.*

| Tsayi | |
|---|---|
| Ɗalibi na 1 | Fensuri ____ |
| Ɗalibi na 2 | Fensuri ____ |

- Kira ɗalibi 1 ya je ya tsaya a jikin allo yana fuskantar aji. Yi amfani da alli, a zana layi a kan allon daidai inda kansa ya kai.
- Kira wani ɗalibin ya yi amfani da fensirinsa ya auna tsayin ɗalibin farko daga ƙafarsa zuwa daidai layin da aka ja aka allo. Rubuta awon cikin jadawalin ƙarƙashin ɗalibi na 1.
- A auna wani ɗalibin. Rubuta awon cikin jadawalin ƙarƙashin ɗalibi na 2.
- A tambayi ɗalibai su faɗi wanda ya fi tsayi da gajerta a tsakanin ɗaliban nan biyu.

### Gwaji

Aiki a ƙaramin rukuni: Awon tsayi (minti 15)

- Ɗalibai su zauna a ƙananan rukunoni daga 3 zuwa 5. Sa ɗalibai su buɗe littafinsu Shafi na 74.
- Yi bayani cewa za su auna juna dangane da tsayi. Ɗalibi ɗaya ya jingina bayansa a kan allo. Sai wani ya auna tsayinsa da fensir, ya fara daga ƙasa zuwa inda kansa ya kai. Ɗalibai su rubuta awon tsayin, da fensir, a cikin littafin rubutunsu.
- A yi ta yi har sai an auna kowane ɗalibi.
- A kewaya a duba abin da suke yi, sannan a taimaka musu gwargwadon buƙata. A tabbata kowane ɗalibi ya auna wani ɗalibin kuma shi ma an auna shi.

### Bayyanawa

Bayyana kyawawan misalai (minti 5)

- A sa ɗalibai su nuna wa juna bayanan da suka tattara na rukuninsu.

### Aikin Gida


A sa ɗalibai ƙarasa samo amsoshin aikin da ke Shafi na 74 cikin littafin ɗalibai. Su auna tsayin mutum 2 a gidansu.

| Na. 179 | Zango na 3, Mako na 12, Darasi na D |
|---|---|

**Manufofi:** Ɗalibai za su iya zana da sanya wa siffofi mabambanta sunansu.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

**Fara Darasi**

Duba aikin gida (minti 2)



- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.

Labari cikin hoto (minti 3)

- Karanta wa ɗalibai labarin cikin hoto a kan allon. Ishak yana kan hanya zuwa gida daga makaranta. Da ya isa gida, sai ya fahimci cewa gidansu yana ɗauke da siffofi mabambanta.
- **Ka/ki ce:** *Waɗanne siffofi kuke iya gani a hoton gidan Ishak?*

**Koyo**

Samar da siffofi (minti 10)

- A sa duka ɗalibai su haɗu a wajen aji. Da zarar sun fita, a raba su zuwa gida uku.
- Umurci rukunin nan uku cewa da zarar an ambaci siffa, duka ɗaliban a kowane rukuni za su haɗu su yi wannan siffa. Misali, idan an ce "siffa mai kusurwa uku" kowane rukuni sai su shirya kansu ta yadda za su samar da siffa mai kusurwa uku.
- A yi ta yin haka har sai an ambaci duka surorin.

**Gwaji**

Aiki a ƙaramin rukuni: Kirkirar siffofi (minti 15)

- A sa duka ɗalibai nemo sanduna iri-iri da tsakuwoyi da kuma ganyayyaki.
- A ce wa ɗalibai su koma aji da abubuwan da suka samo su kuma zauna a cikinrukuni.
- A kira kowane rukuni ya yi amfani da abubuwan da ya samo su yi siffa mai kusurwa huɗu da mai kusurwa uku da siffar murabba'i da kuma da'ira.
- A zagaya a duba aikin da ɗalibai ke yi. A yayin zagayawar, a tambaye su abubuwan da suke zanawa da sunan siffofinsu, sai a duba ko sun yi daidai.
- A tambayi ɗalibai ko za su iya faɗin wani abu da suka sani game da siffa mai kusurwa uku da da'ir da kuma mai kusurwa huɗu.

**Bayyanawa**

Bayyana kyawawan misalai (minti 5)

- A nemo rukuni ɗaya ko biyu da suka yi zane masu kyau da waken ko wani abu. A sa sauran aji su miƙe su ga abin da suka yi.

**Aikin Gida**

A ce wa ɗalibai su tattauna da wani a gida ko abokinsu kan abin da suka sani game da siffa mai kusurwa huɗu da da'iara da kuma siffa mai kusurwa uku. Ɗaliban su faɗa masu adadin ɓangarorin kowace siffa da suka bayyana masu.


| Na. 180 | Zango na 3, Mako na 12, Darasi na E |
|---|---|

**Manufa:** Ɗalibai za su iya gane bambanci tsakanin surori masu fuska 2 da masu fuska 3.
**Kayan Aiki:** **Lokaci:** Minti 35

## Fara Darasi

<u>Duba aikin gida (minti 2)</u>

- Gaggauta duba aikin gida. A faɗa wa ɗalibai sakamakonsu a kuma ƙarfafa masu gwiwa.



<u>Labari cikin hotoi (minti 5)</u>

- Karanta wa ɗalibai labarin cikin hoto a kan allon. Ali ya koyi wani abu game da siffofi a makaranta. A kan hanyarsa ta zuwa gida, ya ga siffofi a ko'ina. Rana tana da siffa mai surar da'ira, gangar jikin bishiya siffar ce ta silinda, littafinsa kuma siffa ce mai kusurwa huɗu.
- A kira ɗalibi ɗaya zuwa gaban allo. A yayin sake karanta labarin, ɗalibi ya riƙa taɓa siffar da aka ambata a labarin. Misali, rana tana da siffar da'ira, sai ɗalibi ya nuna siffar da'ira da ke kan allon.

## Koyo

<u>Ware siffofi (minti 8)</u>

- A jikin kowane bango na ajin, liƙa fallen takarda ɗauke da wata siffa. Misali, siffa mai kusurwa uku da mai kusurwa huɗu da mai murabba'i da kuma da'ira.
- Ba kowane ɗalibi da ke ajin zanen 'yar ƙaramar siffar.
- Ce wa ɗaliban su kewaya cikin aji su je su tsaya a kusa da siffar da ta dace da wadda aka bai wa kowannen su.
- A ce su tattauna da juna kan sunan siffr da ke hannunsu. A kuma ce su tattauna kan wasu abubuwa da suka sani da suka yi kama da siffofin nasu.
- A kewaya a duba abin da suke yi. A tambayi kowane rukuni sunan siffar tasu.

## Gwaji

<u>Wasan aji bai-ɗaya: Neman wasu siffofin (minti 15)</u>

- Faɗa wa ɗalibai cewa za su je neman siffa kuma su tabbata sun samo siffofi uku mabambanta don cikar rukunin su. Misali, idan ɗalibi ɗaya ya sami siffa mai kusurwa uku, sai a sami wani mai siffar da'ira, wani da siffar murabba'i, da kuma wani siffar huɗu sai su haɗu su samar da rukuni.
- Da zarar ɗaliban sun kafa rukunonin, sai a kira kowa ya faɗa wa juna sunan siffar da ke rukunin sa.
- A faɗa musu cewa su tabbata kowane ɗan rukuni zai iya faɗar sunan siffofin da ke rukunin sa.
- Idan da lokaci, a sa ɗalibai su sake ƙirƙirar wasu rukunonin.

## Bayyanawa

<u>Gaggauta auna fahimta (minti 5)</u>

- A ce su ambaci sunan siffar a bayyane. a sa dukan ɗaliban da ke riƙe da siffar su daga sama.
- Ku maimaita da duka siffofin.

## Aikin Gida

A sa ɗalibai su zana siffar da'ira da ta murabba'i da ma kusurwa huɗu da kuma mai kusurwa uku a cikin littafin rubutunsu.

# Littafin Ɗalibai – Amsoshi

**Zango na 1 Mako na 1 Darasi na D**

1. 16
2. 62
3. 56
4. 37
5. 7
6. 22
7. 92
8. 78
9. 42
10. 11

**Zango na 1 Mako na 2 Darasi na B**

Aikin Aji
8 + 2

Aikin Gida
1. 10 + 3
2. 2 + 12

**Zango na 1 Mako na 2 Darasi na C**

Aikin Aji
3 + 10 = 13

Aikin Gida
6 + 6 = 12


**Zango na 1 Mako na 2 Darasi na D**

Aikin Aji
8 + 2 = 10


Aikin Gida
7 + 6 = 13

**Zango na 1 Mako na 2 Darasi na E**


1. 17




2. 13



3. 20



4. 12



5. 14
6. 12
7. 16
8. 18

**Zango na 1 Mako na 3 Darasi na B**

Aikin Aji
8 – 2 = 6

Aikin Gida
1. 10 – 3 = 7
2. 12 – 2 = 10

**Zango na 1 Mako na 3 Darasi na C**

Aikin Aji
10 - 3 = 7


Aikin Gida
12 - 6 = 6


**Zango na 1 Mako na 3 Darasi na D**


Aikin Aji
12 - 2 = 10


Aikin Gida
14 - 3 = 11

## Zango na 1 Mako na 3 Darasi na E

1. 


2. 


3. 


4. 


5. 14
6. 10
7. 10
8. 10


## Zango na 1 Mako na 4 Darasi na D

Aikin Aji
Cika: 24, 44, 22, 4, 16, 90, 60
Mara: 17, 11, 3, 15, 77

Aikin Gida
Cika: 28, 12, 84, 12, 6, 10
Mara: 33, 13, 13, 91, 45, 99.

## Zango na 1 Mako na 5 Darasi na C

1. 


2. 


3. 


## Zango na 1 Mako na 6 Darasi na E

Aikin Aji
Cika: 42, 16, 100, 4, 80, 60, 74
Mara: 81, 15, 23, 93, 1

Aikin Gida
Cika: 64, 62, 78, 54, 96
Mara: 65, 39, 47, 9, 25, 5, 85

## Zango na 1 Mako na 7 Darasi na C

1. 40, 50, 60; ƙirge ta tsallaken 10.
2. 50, 55, 60; ƙirge ta tsallaken 5.
3. 101,102,103; ƙirge ta tsallaken 1.
4. 198, 199, 200; ƙirge ta tsallaken 1.
5. 180, 190, 200; ƙirge ta tsallaken 10.
6. 100, 110, 120; ƙirge ta tsallaken 10.
7. 140, 145, 150; ƙirge ta tsallaken 5.
8. 126, 128, 130; ƙirge ta tsallaken 2.
9. 106, 108, 110; ƙirge ta tsallaken 2.
10. 184, 185,186; ƙirge ta tsallaken 1.

## Zango na 1 Mako na 7 Darasi na D

1. 165; ƙirge ta tsallaken 5.
2. 100; ƙirge ta tsallaken 2.
3. 100; ƙirga ta tsallaken 10.
4. 117; ƙirge ta tsallaken 1.
5. 20; ƙirge ta tsallaken 10.
6. 80; ƙirge ta tsallaken 5.
7. 76; ƙirge ta tsallaken 2.
8. 46; ƙirge ta tsallaken 1.
9. 34; ƙirge ta tsallaken 1.
10. 40; ƙirge ta tsallaken 10.

## Zango na 1 Mako na 8 Darasi na C

1. Lambar ita ce 24. Goma 2 da ɗaiɗaya 4.
2. Lambar ita ce 35. Goma 3 da ɗaiɗaya 5.
3. Lambar ita ce 60. Goma 6 da ɗaiɗaya 0.
4. Lambar ita ce 28. Goma 2 da ɗaiɗaya 8.

**Zango na 1 Mako na 8 Darasi na D**


1. Lambar ita ce 33.
   Ɗari 0
   Goma 3
   Ɗaiɗaya 3
2. Lambar ita ce 146.
   Ɗari 1
   Goma 4
   Ɗaiɗaya 6
3. Lambar ita ce 111.
   Ɗari 1
   Goma 1
   Ɗaiɗaya 1

**Zango na 1 Mako na 9 Darasi na A**

545

**Zango na 1 Mako na 9 Darasi na C**

1. 


2. 


3. 


4. 


**Zango na 1 Mako na 9 Darasi na D**

1. 6; ƙirge ta tsallaken 2
2. 106; ƙirge ta tsallaken 2
3. 80; ƙirge ta tsallaken 5
4. 915; ƙirge ta tsallaken 5
5. 824; ƙirge ta tsallaken 1
6. 600; ƙirge ta tsallaken 100
7. 990; ƙirge ta tsallaken 10
8. 130; ƙirge ta tsallaken 1
9. 440; ƙirge ta tsallaken 5
10. 618; ƙirge ta tsallaken 2


**Zango na 1 Mako na 10 Darasi na B**


1. 


2. 


3. 


**Zango na 1 Mako na 10 Darasi na D**

1. 


2. 


3. 


4. 


**Zango na 1 Mako na 11 Darasi na A**

1. 6 = 6
2. 198 < 298
3. 999 > 997
4. 221 > 88
5. 67 > 32
6. 100 > 90
7. 54 < 540

**Zango na 1 Mako na 11 Darasi na C**


1. 321, 456, 954
2. 0, 236, 936
3. 1, 10, 100
4. 85, 105, 285
5. 97, 799, 977
6. 92, 123, 872
7. 196, 309, 742


**Zango na 1 Mako na 11 Darasi na D**


1. 954, 456, 321
2. 86, 45, 34
3. 333, 222, 111
4. 875, 675, 275
5. 900, 90, 9
6. 889, 888, 564
7. 657, 35, 11

**Zango na 1 Mako na 12 Darasi na C**

1. 


2. 


3. 


4. 


**Zango na 1 Mako na 12 Darasi na D**

1. Lambar ita ce 23.
   Ɗari 0
   Goma 2
   Ɗaiɗaya 3
2. Lambar ita ce 141.
   Ɗari 1
   Goma 4
   Ɗaiɗaya 1
3. Lambar ita ce 136.
   Ɗari 1
   Goma 3
   Ɗaiɗaya 6

**Zango na 1 Mako na 12 Darasi na E**

1. 12 < 15
2. 478 > 278
3. 28 < 36
4. 185 > 85
5. 982 = 982
6. 999 > 200
7. 593 > 6

**Zango na 2 Mako na 1 Darasi na D**

1. $\frac{1}{2}$
2. $\frac{1}{4}$
3. $\frac{3}{4}$
4. $\frac{1}{4}$
5. $\frac{3}{4}$
6. $\frac{1}{2}$

**Zango na 2 Mako na 2 Darasi na D**

1. $\frac{1}{3}$
2. $\frac{2}{3}$
3. $\frac{1}{2}$
4. $\frac{1}{4}$
5. $\frac{3}{4}$

**Zango na 2 Mako na 3 Darasi na D**

1. $\frac{1}{5}$
2. $\frac{1}{2}$
3. $\frac{1}{3}$
4. $\frac{1}{6}$
5. $\frac{3}{4}$
6. $\frac{1}{4}$
7. $\frac{2}{3}$

**Zango na 2 Mako na 4 Darasi na B**

1. 66
2. 28
3. 52
4. 69
5. 58
6. 24
7. 78

**Zango na 2 Mako na 4 Darasi na C**

1. 59
2. 59
3. 98
4. 38
5. 48
6. 66

**Zango na 2 Mako na 5 Darasi na B**

1. 663
2. 875
3. 394
4. 783
5. 629
6. 596
7. 581

**Zango na 2 Mako na 5 Darasi na C**

1. 999
2. 986
3. 517
4. 688
5. 472
6. 846

**Zango na 2 Mako na 6 Darasi na D**

1. 30 + 6
2. 400 + 0 + 2
3. 900 + 90 + 9
4. 30 + 4
5. 300 + 50 + 4
6. 70 + 8
7. 800 + 70 + 4
8. 20 + 1
9. 600 + 70 + 8
10. 600 + 0 + 2

**Zango na 2 Mako na 6 Darasi na E**

1. 54
2. 745
3. 26
4. 369
5. 814
6. 96

**Zango na 2 Mako na 7 Darasi na A**

1. 300 + 60 + 0
2. 40 + 2
3. 500 + 80 + 9
4. 300 + 40 + 6
5. 500 + 60 + 7
6. 800 + 70 + 2
7. 80 + 7
8. 30 + 4
9. 200 + 30 + 1
10. 100 + 10 + 1

**Zango na 2 Mako na 7 Darasi na C**

1. 61
2. 81
3. 86
4. 63
5. 92
6. 40
7. 70

**Zango na 2 Mako na 8 Darasi na B**

1. 81
2. 96
3. 72
4. 83
5. 90
6. 50
7. 93

**Zango na 2 Mako na 8 Darasi na C**

1. 99
2. 97
3. 71
4. 71
5. 44

**Zango na 2 Mako na 9 Darasi na B**

1. 55
2. 5
3. 50
4. 5
5. 50
6. 5
7. 35
8. 40
9. 20
10. 35

**Zango na 2 Mako na 9 Darasi na C**

1. 11
2. 1
3. 54
4. 40
5. 55
6. 14

**Zango na 2 Mako na 10 Darasi na B**

1. 19
2. 49
3. 59
4. 19
5. 17
6. 28
7. 59

**Zango na 2 Mako na 10 Darasi na C**

1. 9
2. 29
3. 47
4. 52
5. 37
6. 3
7. 7

**Zango na 2 Mako na 11 Darasi na B**

1. 16
2. 59
3. 9
4. 19
5. 8
6. 27
7. 29

**Zango na 2 Mako na 11 Darasi na C**

1. 37
2. 9
3. 39
4. 69
5. 38
6. 9
7. 34



**Zango na 3 Mako na 1 Darasi na D**

1. ₦5
2. ₦20 + ₦5
3. ₦50

**Zango na 3 Mako na 2 Darasi na D**

1. 5 x 6 = 30
2. 10 x 3 = 30
3. 2 x 8 = 16
4. 10 x 5 = 50
5. 10 x 2 = 20
6. 5 x 5 = 25
7. 2 x 2 = 4
8. 2 x 12 = 24

**Zango na 3 Mako na 3 Darasi na A**

1. 
2. 
3. 

**Zango na 3 Mako na 3 Darasi na D**

1. Sentimita: 35
2. Sentimita: 17
3. Sentimita: 65

**Zango na 3 Mako na 4 Darasi na D**

1. Sentimitoci: 75
2. Mitoci: 2

**Zango na 3 Mako na 5 Darasi na B**

1. Sentimitoci: 45
2. Sentimitoci: 55
3. Sentimitoci: 30

**Zango na 3 Mako na 5 Darasi na D**

Amina, Nasir, Zahra, Isaac, Abubakar



**Zango na 3 Mako na 6 Darasi na B**

1. ₦50
2. ₦100
3. ₦170
4. ₦480
5. ₦125
6. ₦610

**Zango na 3 Mako na 6 Darasi na C**

1. 5 x 3 = 15
2. 10 x 2 = 20
3. 2 x 3 = 6
4. 10 x 7 = 70
5. 10 x 9 = 90
6. 5 x 12 = 60
7. 2 x 2 = 4
8. 2 x 12 = 24

**Zango na 3 Mako na 8 Darasi na C**

1. 
2. 
3. 

**Zango na 3 Mako na 9 Darasi na B**

Yara maza = 10
Yara mata = 8

1. Maza
2. Mata

**Zango na 3 Mako na 9 Darasi na D**

1. Shekara 7
2. Shekara 9; Shekara 10